# MUN KUSA DA KARSHE

BA TARE DA NEMAN GAFARA DAGA KOWA BA, MANUFAR WANNAN LITTAFI SHINE YA GARGAƊI JAMA'A GAME DA SHAIDUN DA SUKE BAJE CIKIN LITTAFI MAI-TSARKI WAƊANDA KE NUNA CEWA MUNA DAB DA KARSHEN DUNIYA. KARSHEN DUNIYA SHINE WANNAN LOKACIN NAN MAI BAN RAZANA NA BAYYANUWAR YESU KRISTI, BABBAN MAI MULKIN DUKAN MUTANE, DOMIN YA KAMMALA YANKE SHARI'AR DA AKA FARA TUN A LAMBUN ADDINI, LOKACIN DA ADAMU DA HAUWA'U SUKA YI WA ALLAH RASHIN BIYAYYA.

HAROLD CAMPING/FAMILY RADIO

MUN KUSA DA KARSHE
(Hausa: We Are Almost There!)
Harold Camping

Family Stations, Inc.
Oakland, California, 94621 U.S.A.

Internet: www.familyradio.com

06-05-09

## MUN KUSA DA KARSHE

# Abinda ke ciki


Gabatarwa ........................................................................ v

**Sura ta Fari: Maɗaukakiyar Maganar Allah** ........................................ 1
Rubutacciyar dokar Allah ........................................................... 2
Kashi na uku na zamanin da Wahayin Yahaya
ke magana akai ..................................................................... 3
Fassarar Littafi Mai-Tsarki ......................................................... 3
A ƙarshe, cika bayyani game da shirin Allah na ceto ........................ 4

**Sura ta biyu: Littafi Mai-Tsarki ya bada jerin lokaci na tarihi** ............. 7
Yadda Allah ya shinfiɗa shirinsa na ceto a cikin jerin kwanaki na
tarihi ................................................................................ 8
Isra'ila da shekarun da suka kama daga 1447 B.C
zuwa A.D. 33 ........................................................................ 8
Farkon zamanin Ikklisiya.......................................................... 11
Littafi Mai-Tsarki ya san Ikklisiya za ta bijire................................ 12
Matsalar Shaiɗan a cikin Ikklisiya ................................................ 14
Shin ko dukan Littafi Mai-Tsarki cikakkar
Maganar Allah ce?.................................................................. 16
Zamanin Ikklisiya zai kai ga ƙarshe ............................................. 17

**Sura ta uku: Shirin Allah na jinkirta fahimtar yadda zamani ƙarshe zai kasance** ........................................................................ 19
Yanzu muna zamanin fahimta...................................................... 21
An danganta muhimman datsin lokatai da bukukuwa
da suka zama alamu ............................................................... 26
Shinfiɗaɗɗun al'amura da suka shafi shiri na ceto.......................... 29
Allah yayi amfani da haikali a matsayin alamar
gaskiya ta ruhaniya................................................................ 30
Abubuwan da suka shafi haikali sun bada sanarwa
a kan muhimman lokatai .......................................................... 31

Rana ta takwas, 21 Oktoba 2011 .......... 33
Mu sake duba Idin bukkoki .......... 33

**Sura ta huɗu: Mun fara binciken mu game da tsarin lokaci .......... 36**
Ranar da zamanin Ikklisiya ke ƙarewa .......... 43

**Sura ta biyar: Shin ko abin da muka sani game da tsarin kwanakin ƙarshe daidai yake?** .......... 47
Cikar shekara 13,000 ta duniya .......... 50
Kwana ɗaya shekara dubu ne .......... 54
Watanni biyar na ƙarshe .......... 56
Karin bayanai ƙwarara .......... 57
Daga Ranar Fansa zuwa fyaucewa: kwanaki 722,500 .......... 58
Karin Tabbaci .......... 59
Allah Ya ci gaba da ɗaukar Matakan Hukunci yayinda ake ci gaba da ceton ɗinbin mutane .......... 60

**Sura ta shida: Ko akwai bege domina? .......... 62**
Waɗanda basu taɓa ji ba .......... 63
Waɗanda suka ji amma suka yi ba'a .......... 63
Waɗanda a cikin tawali'u suka amince da cewa suna bukatar yin biyayya da Littafi Mai-Tsarki .......... 66
Waɗanda suke da kunne bari su ji. .......... 67

# Gabatarwa

**BA TARE DA NEMAN GAFARA DAGA KOWA BA, MANUFAR WANNAN LITTAFI ITA CE YA GARGAƊI JAMA'A GAME DA SHAIDUN DA SUKE BAJE CIKIN LITTAFI MAI-TSARKI WAƊANDA KE NUNA CEWA MUNA DAB DA KARSHEN DUNIYA. KARSHEN DUNIYA SHINE WANNAN LOKACIN NAN MAI BAN RAZANA NA BAYYANUWAR YESU KRISTI, BABBAN MAI MULKIN DUKAN MUTANE, DOMIN YA KAMMALA YANKE SHARI'AR DA AKA FARA TUN A LAMBUN ADDINI, LOKACIN DA ADAMU DA HAUWA'U SUKA YI WA ALLAH RASHIN BIYAYYA.**

Duk mutumin da bashi da ceto zai fuskanci cikakken fushin Allah. Idan har Kristi bai biya bashin zunubin ka ba, za ka fuskanci zafin fushin Allah.

Ba wanda yake jin daɗin yin magana akan irin wannan sanarwar. Babu abinda yafi wannan karya gwiwa. Ya fi sauƙi mutum ya yi rayuwa cikin musu, yana fata a asirce cewa da so samu ne, wannan maganar hukumcin ya zama magana ce kawai ba abinda za'a ɗauka da muhimmanci ba.

Sai dai kuma, yayinda muke sane da cewar Littafi Mai-Tsarki gaskiya ne kuma mai iko, an umurce mu da mu shaidawa duniya dukan abinda Littafi Mai-Tsarki ya koyar game da wannan abin mai firgitaswa. Mai-bin Kristi na gaskiya bashi da zaɓi. Dole ne su gargaɗi duniya game da hukumcin nan mai zuwa. Alal misali, Allah ya umurci Annabi Yunana da ya tafi Nineva ya yi masu kashedi cewa a cikin kwanaki 40, Allah zai hallaka su. Yunana bai ji daɗin ɗaukar wannan mugun labari zuwa ga mutanen Nineva ba, amma daga ƙarshe, yayi biyayya. Abin ban sha'awa, mutanen Nineva sun tuba, suka kuma roƙi Allah cikin ƙasƙanci, suna fatan Allah zai ji ƙansu. Allah kuma ya ji ƙansu, Allah kuma bai hallaka birnin su ba.

Haka yanayin yake a yau, sai dai a yau, abin ya shafi dukan duniya ne. Lokacin kuma bai kai shekara huɗu ba a maimakon kwana arba'in. Yayinda dukan birnin Nineva ya tuba, dukan duniyar mu ta yau ba zata tuba ba. Sai dai kuma, labari mai daɗin shine, Littafi Mai-Tsarki ya shaida cewa ɗinbin mutane, waɗanda ba mai iya ƙirgawa, za su roƙi Allah cikin ƙasƙanci, kuma girbi mai girma na waɗanda Allah ya zaɓa ya kuma ceta, za a basu rai na har abada, kuma zasu tserewa wannan hukumcin Allah, da suka cancanta sabili da zunubansu.

Waɗansu mutane, musamman ma waɗanda har yanzu suna cikin Ikklisiya sun ɗauka cewa Kristi zai zo kamar ɓarawo da dare. Sabili da haka suna cewa kada ma mutum ya dami kansa da wani ƙoƙarin sanin abinda Littafi Mai-Tsarki ke faɗa game da lokacin da duniya zata zo ga ƙarshe.

Waɗannan mutanen sun yi daidai. Littafi Mai-Tsarki na koyasda cewa, ga mutane da yawa, Kristi zai zo kamar ɓarawo da dare. Mun karanta a cikin 1 Tassalunikawa 5:2-3 cewa:

> **Domin ku da kanku kun sani sarai, ranar Ubangiji zata zo ne kamar ɓarawo da dare. Lokacin da mutane suke cewa, "muna zaman**

**salama da zaman lafiya.'' wuf; sai hallaka ta auko masu, kamar yadda naƙuda take kama mace mai ciki, ba kuwa hanyar tsira.**

Sai dai kuma a aya ta 4-6, Littafi Mai-Tsarki yace

:

**Amma ai ba a cikin duhu ku ke ba, yan'uwa har da ranar nan zata mamaye ku kamar ɓarawo. Domin duk mutanen haske kuke, na rana kuma. Mu ba na dare ko na duhu ba ne. Ashe, saboda haka kada mu yi barci kamar yadda waɗansu suke yi, sai dai mu zauna a faɗake da natsuwa.**

Waɗannan ayoyin suna nuna cewa akwai mutane iri biyu waɗanda suka gane cewa wannan duniya zata kai ga ƙarshe, a wannan lokacin kuma, Allah zai ware cetattu da waɗanda ba cetattu ba. Dukan waɗannan mutanen kuma sun sani cewa waɗanda basu da ceto zasu fuskanci fushin Allah, waɗanda ke da ceto kuwa, za su kasance da Kristi cikin murna da ɗaukaka har abada.

Kungiya ɗaya ta ƙunshi mutane da yawa waɗanda suke ganin kamar suna da ceto, sai dai kuma, ba su da ceto. Ba su da sanin cewa Allah ya bayyana abubuwa da dama a cikin Littafi Mai-Tsarki waɗanda suka shafi jerin lokaci na tarihi wanda ya kai har ga ƙarshen duniya, kuma basu damu da su koyi abinda Littafi Mai-Tsarki ke koyaswa ba. Suna gaba-gaɗi cewa suna da ceto, sabili da haka, koma yaushe Kristi zai dawo, ba laifi. A garesu, zai zo kamar ɓarawo da dare. Abin baƙin cikin shine, waɗannan ayoyin na nunin cewa lokacin da Kristi zai komo, "hallaka zata abko masu" Ta wurin rashin marmarin koyon abin da Littafi Mai-Tsarki ke faɗa, suna nuna cewa basu da ceto, kuma har yanzu suna ƙarƙashin fushin Allah.

Sai dai kuma, akwai mutane da yawa waɗanda sakamakon ƙauna da bangirma da suke yi wa Littafi Mai-Tsarki, sun gane cewa Littafi Mai-Tsarki ya faɗi abubuwa da dama game da jerin lokaci na tarihi. Ta wurin yin haka, sun iya koyon abubuwa da suka shafi jerin al'amuran da suka shafi ƙarshen zamani da kuma lokutan da waɗannan abubuwan zasu faru. Littafi Mai-Tsarki ya kira su "Masu tsaro" (Ezekiel 33:2-9), ta wurin yin haka, sun iya gargaɗin marasa ceto na duniya game da ƙarshen duniya, wadda ke gabatowa.

An rubuta wannan littafin da fatan cewa kai ma, zaka iya gane muhimmancin bala'in da duniya ke ciki. Ba yadda za'a yi a canza shirin Allah game da ƙarshen duniya. Sai dai kuma, kai ma, kana iya zama ɗaya daga cikin waɗanda zasu tserewa fushin Allah ta wurin jinƙan shahararren shirinsa na ceto.

A cikin wannan littafin, zamu duba abubuwan da Allah ya aikata cikin tarihin duniya yayinda yake buɗe shirinsa na ceto ga duniya. Za mu fi maida hankali ne ga lokaci na ƙarshe a tarihin duniya, inda manyan abubuwa biyu za su riƙa faruwa tare. Waɗannan abubuwan sune cikar shari'ar Allah, da kuma ceton ɗinbin mutane, waɗanda ba mai iya ƙirgawa.

A cikin wannan littafin, an bada kwanakin waɗansu manyan abubuwa da suka faru a tarihi ya haɗe kuma da waɗansu abubuwa masu zuwa. Ga waɗanda ke so su ƙara bincika Littafi Mai-Tsarki domin ƙarin bayyani game da waɗannan kwanakin, da kuma tantance waɗannan kwanakin, zasu iya kiran mu ko kuma su ruboto mana a Family Radio domin samun littattafai kyauta waɗanda ke nuna cewa dukan abin nan da muke faɗa sun fito ne daga Littafi Mai-Tsarki, kuma ba daga ƙage ko bara-da-ka aka fito da su ba. Waɗannan littattafan sun haɗa da:

*Lokaci na da ƙarshensa*
*Ƙarshen zamanin Ikklisiya da abin da ya biyo baya*
*Alkama da zawan*
*Maƙasudin farko na binciken Littafi Mai-Tsarki*
*Ina fata Allah zai cece ni*
*Adamu, yaushe?*
*Babbar mawafukar lambobin Sarakunan Ibraniyawa.*

# Sura ta Fari: Maɗaukakiyar Maganar Allah

Fahimtar wannan babban ra'ayin na cewa duniya ta kusa zuwa ga ƙarshe na bukatar kyakkyawar fahimtar yanayi da kuma ikon da maganar Allah watau Littafi Mai-Tsarki yake da shi. Littafi Mai-Tsarki ya shinfiɗa manyan ginshiƙai waɗanda idan har muna so mu karɓi gaskiya daga Allah, dole ne muyi biyayya da su. Dole ne waɗannan maƙasudan abubuwan su shinfiɗu a cikin zuciyar kowane mutumin da yake marmarin fahimtar wannan babban ra'ayin.

Littafi Mai-Tsarki maganar Allah ce. A cikin asalin harshen Littafi Mai-Tsarki wanda yawancin sa Helinanci ne da Ibraniyanci, kowacce kalma, da kowace harufa, daga bakin Allah ta fito. Sabili da haka, ba za'a amince da cewa wai mahaluƙi ko wata ƙungiya da ke da iko akan wata kalma ko wani kalami da harshen Littafi Mai-Tsarki na asali ya ƙunsa ba. Allah ya keɓe ya kuma lura da littattafan na farko waɗanda ke cikin harshen Helinanci da Ibraniyanci domin mu iya tabbatar da cewa muna da ainihin maganar da ta fito daga bakin Allah. Littattafan da aka juya zuwa harshen turanci juyi na King James da kuma sauran juyin da aka yi a wancan zamanin, sune takardun da Allah ya keɓe. Gaskiya ne cewa dukan malamin Littafi Mai-Tsarki wanda ya ɗauki aikinsa da muhimmanci, dole ne ya riƙa duba aikin da masu juyawa suka yi ya kuma riƙa yin gyara inda ake bukatar yin haka, yayinda yake binciken Littafi Mai-Tsarki.

Littafi Mai-Tsarki gaba ɗayansa, shine babban littafin dokokin Allah, kuma ya kamata kowane mutum yayi cikakkar biyayya da shi. A matsayinsa na babban littafin shari'ar Allah, Littafi Mai-Tsarki ya furta cewa hukumci na hallaka yana jiran kowane mutumin da ya ƙetare maganar Allah ko ta wanne fanni (Romawa 6:23; Yakubu 2:10).

Littafi Mai-Tsarki shine saƙon Allah na ceto. Watau, shari'ar Allah ta ƙunshi labarin yadda Allah da kansa ya zama musanyar, ko kuma ya tsaya a madadin, domin ya ɗauki hukumcin fushin Allah cikin Yesu Kristi a madadin dukan waɗanda Allah yayi niyar ya ceta daga hukumcin zunubi, wanda shine hallaka ta har abada.

Littafi Mai-Tsarki shine ƙamus da kuma littafin fasarar kansa. Dole ne a fahimci dukan harufofi, kalamai da sauransu, ta wurin binciken wannan kalmar ko kuma kalamin daga wasu sassa na Littafi Mai-Tsarki. Bai kamata a riƙe wata koyaswa ta Littafi Mai-Tsarki ba ba tare da an bincike ta a hankali a cikin Littafi Mai-Tsarki gaba ɗayansa domin a tabbatas tana tafiya daidai da sauran koyaswa ta Littafi Mai-Tsarki ba. A cikin 1 Korantiyawa 2:13, Allah ya bada wannan umurnin:

> **Su ne kuwa muke sanarwa ta maganar da ba hikimar ɗan adam ce ta koyar ba, sai dai wadda Ruhu ya koyar, muna bayyana al'amura masu ruhu ga waɗanda suke na ruhu.**

Rubutacciyar dokar Allah

Ta wurin jinƙansa, Allah ya tanada rubutacciyar dokar Allah. Wannan rubutacciyar dokar ita ce Littafi Mai-Tsarki, maganar Allah. Wannan dokar kuma, ita ce alkawalin Allah da mutane, kuma akan kira ta Bishara da kuma Tsoho da Sabon Alkawali. Sabili da haka, ko da Littafi Mai-Tsarki yayi amfani da kalmar nan 'Shari'a,' ko 'doka.' ko 'alkawali,' ko 'Bishara,' ko 'kalma,' duka yana magana ne akan Littafi Mai-Tsarki shi kaɗai. Dukan waɗannan kalmomin suna nufin abu ɗaya ne.

An ba mutum Littafi Mai-Tsarki ta fannoni guda biyu, amma Allah ya rubuta Littafi Mai-Tsarki ta hanyar da aka bayyana gaskiyar Littafi Mai-Tsarki ta sassa guda uku.

Sashi na farko na rubutattun kalmomin da Allah ya bayas shine Tsohon Alkawali. An fara rubutun Tsohon Alkawali shekaru dubu ɗaya da ɗari huɗu da arba'in da bakwai kafin haihuwar Yesu (1447 B.C.) a lokacin da Allah ya ba 'ya'yan Isra'ila dokoki goma haɗe da waɗansu sharuɗɗai masu yawa. Haka kuma, a cikin wannan alkawalin, Allah ya rubuta abubuwa da yawa da suka shafi halittar duniya, shigowar zunubi cikin duniya, da kuma ruwan tsufana na zamanin Nuhu, haɗe kuma da sharuɗai da dama da suke nanata bukatar da mutum yake da ita na mai-ceto. Allah ya ci gaba da rubutun Tsohon Alkawali har zuwa shekara ta ɗari uku da casa'in da ɗaya kafin haihuwar Yesu (301 B.C.).

Sai dai kuma, Allah ya rubuta Tsohon Alkawali a wani salo inda ba a bayyana abubuwa da yawa sosai ga mutum ba, waɗanda rubutaccen Tsohon Alkawalin ya ƙunsa. Haka kuma, sabili da babu injinan buga littattafai, an yi ƙarancin rubutattun littatttafan Tsohon Alkawali. A wancan lokacin, littattafan Tsohon Alkawali kaɗan ne kawai ake da su.

Allah ya fara rubuta sashi na biyu na alkawalin wanda ake kira Sabon Alkawali a wajen shekara ta talatin da uku bayan tashin Yesu daga matattu (A.D. 33). An kammala shi kuma a wajen shekara ta casa'in da biyar bayan tashin Yesu (A.D. 95). Ya ƙunshi abubuwa da yawa waɗanda suka taimaka wajen fahimtar Tsohon Alkawali. Wannan ya faru ne domin Sabon Alkawali ya bada labarin Yesu Kristi Mai-Ceto sosai, yadda ya ɗanɗana fushin Allah a madadin waɗanda yayi shirin ceto. Duk da haka, kamar Tsohon Alkawali, Allah ya rubuta Sabon Alkawali ta hanyar da akwai gaskiya jibge wadda take a ɓoye ga masu bi na gaskiya a zamanin Ikklisiya.[1]

Sabili da haka, ko da yake an gama rubuta Littafi Mai-Tsarki ko rubutattun dokokin har kimanin shekaru dubu biyu, ba a bayyana waɗansu gaskiya masu yawa da ke cikin Littafin ga mutane ba kome ƙoƙarinsu, kome sanin ko tsoron Allan su. Waɗannan ɓoyayyun koyaswar sun shafi cikakken sanin tsarin lokaci da yanayin shirin ceton Allah, haɗe da manya manyan abubuwan da zasu faru a cikin shekaru 23 na tarihin ƙarshen duniya.

---

1. Mun yi amfani da Kalmar nan "zamanin Ikkilisiya" domin nuna lokacin da Allah ya yi amfani da Ikkilisiyai wajen kawo Bishara

## Kashi na uku na zamanin da Wahayin Yahaya ke magana akai

Sai dai kuma, a zamanin nan namu, mu da muke kusa da ƙarshen duniya, Allah, a kashi na uku, yana buɗe mana wata gaskiya wadda tun dama can tana cikin Littafi Mai-Tsarki, amma da ana ganinta a duhunce. Sabili da haka, sai yayi kamar Allah yayi mana ƙari ne a bisa Tsoho da Sabon Alkawali, amma gaskiyar ita ce, ba wani ƙari da aka yi akan Littafi Mai-Tsarki. Ba a ƙara masa waɗansu kalmomi ba. Littafi Mai-Tsarkin da muke amafani da shi, idan ka ɗauke shi a harshen da aka rubuta shi tun da can, daidai yake da wanda aka rubuta wajen shekaru 1,900 da suka wuce. Abin da ya faru kawai shine, a yau, ana iya ganin cikar ɗaukakar Bisharar domin Allah yana buɗe idanunmu mu fahimci waɗannan koyaswa da a da suke ɓoye. A cikin Ibraniyawa 8:8, Littafi Mai-Tsarki ya ce:

> **Gama ya ga laifinsu da ya ce, "Lokaci yana zuwa, in ji Ubangiji, da zan tsara sabon alkawari da jama'ar Isra'ila da kuma zuriyar Yahuza.**

A wannan aya, ya kamata da an rubuta kalmomin nan 'Zan yi sabon Alkawali" su zama "Zan ƙarasa sabon Alkawali." Sabon Alkawalin shine Sabon Alkawali wanda muke da shi a cikin Littafi Mai-Tsarki, sai dai kuma, a ƙarshen zamani ne, cikin kwanakin nan namu, Allah yake ƙara sanar da mu wannan alkawalin ta wurin buɗe idanunmu domin mu iya ganin gaskiyar. Tun dama wannan gaskiyar tana cikin Littafi Mai-Tsarki, amma a zamanin nan na mu, ana bayyana mana su domin mu iya fahimtar su. Yayi kamar Allah yana ƙarasa rubuta alkawalin da ke cikin Littafi Mai-Tsarki ne. Wannan yayi daidai da abin da ayoyi kamar su Daniyel 12:9 inda Allah ke cewa:

Sai ya ce, "Yi tafiyarka, Daniyel, gama an rufe wannan magana, an kuma kulle ta har ƙarshen lokaci.

## Fasarar Littafi Mai-Tsarki

Abin baƙin ciki ne ganin yadda Ikklisiyoyi ko ina a cikin duniya basu iya gane mafiya yawan gaskiyar da ke cikin Littafi Mai-Tsarki ba. Wannan ya faru ne domin basu yi biyayya da umurnin Littafi Mai-Tsarki game da fasarar Littafi Mai-Tsarki ba. Haka kuma, yana yiwuwa mafiya yawan malaman Littafi Mai-Tsarki basu gane da cewa kowace kalma dake cikin harshen Littafi Mai-Tsarki na asali daga bakin Allah ta fito ba, sabili da haka, tana da babban muhimmanci, kuma babu kuskure ko kaɗan a cikin ta.

Ya kamata a yi watsi da fassara, tarihi da hanyoyin fassara Littafi Mai-Tsarkin da muke gani a cikin majami'u, makarantun tauhidi da dai sauransu. Fasarar Littafi Mai-Tsarki ta gaskiya na kafe ne akan furucin Littafi Mai-Tsarki dake cewa, Littafi Mai-Tsarki littafi ne na ruhaniya wanda aka rubuta ta hanyar duniya.

Domin Allah ne da kansa ya rubuta shi, kowane abin da ya faru a tarihi, kowace magana, da dukan abin da aka rubuta a ciki gaskiya ne kuma

abin dogara ne. Sai dai kuma, domin dole ne a fahimci waɗannan kalaman ta fuskar ruhaniya, ba za'a iya fahimtar saƙon da Allah yake da shi zuwa ga 'yan adam a cikin Littafi Mai-Tsarki ba sai idan an iya gane koyaswar ruhaniyar da littafin ya ƙunsa.

Yesu yayi magana a cikin Markus 4:33-34 inda yace:

> **Da misalai da yawa irin waɗannan Yesu ya yi musu maganar Allah, daidai gwargwadon ganewa tasu. Ba ya faɗa musu kome sai da misali, amma a keɓe yakan bayyana wa almajransa kome.**

Yesu shine asalin kalmar Allah. A cikin Yahaya 1:14, muka karanta cewa, kalmar ta zamo jiki, ta zauna a cikin mu. Shi ya sa, tushen samun ma'anar kowace kalma a cikin Littafi Mai-Tsarki ya shafi dukan Littafi Mai-Tsarkin kamar yadda ake danganta Kristi da dukan Littafi Mai-Tsarki. Littafi Mai-Tsarki maganar Allah ce. Kristi Kalmar Allah ne. Kuma domin Littafi Mai-Tsarki littafin Allah ne, dole ne dukan ɗaliban Littafi Mai-Tsarki su nemi taimako daga Ruhu Mai-Tsarki, Allah da kansa. Allah ne kaɗai zai iya shinfiɗa gaisuwa a cikin zukatanmu (Yahaya 16:13). Dole ne ɗalibin Littafi Mai-Tsarki ya gwada kowace gaskiya ya kuma tabbatar cewa tana mawafuka da sauran gaskiyar da Littafi Mai-Tsarki yake koyaswa.

Wannan tushen maganar da ke cewa Kristi yayi magana da su da misalai, da kuma bai faɗa masu komai ba sai da misalai, tana kama da ginshiƙin da Allah yake amfani da shi wajen taimakawa masu bi na gaskiya su ƙara ganewa da Littafi Mai-Tsarki. Sai dai kuma, da alama shine kuma abin da Allah yake amfani da shi domin ya makantar da waɗanda ke fasara Littafi Mai-Tsarki da iyawar kansu. An kafa wannan ginshiƙin ne a cikin Markus 4:11-12, inda Allah ke cewa:

> **Sai ya ce musu, 'Ku kam, an yardar muku ku san asirin Mulkin Allah, amma ga waɗanda ba sa cikinku, kome sai a cikin misali, don gani da ido kam, su gani, amma ba da zuciya ba. Ji kuma, su ji, amma ba za su fahimta ba, wai don kada su juyo a yafe musu.'**

Alal misali, dukan wanda ke bin koyaswa da fasarori irin na mutane, wanda shine abin da Ikklisiya ke aiki da shi ko ina cikin duniya, ba zai iya fahimtar gaskiyar Littafi Mai-Tsarki yadda ya kamata ba. Wannan kuwa ya ƙunshi koyaswa da ta shafi ƙarshen zamanin Ikklisya, da kuma gaskiyar da ke nuna cewa masu bi na gaskiya zasu iya sanin lokacin da Allah yayi shirin kawo wannan duniya ga ƙarshe.

**A ƙarshe, cikar bayyani game da shirin Allah na ceto.**

Yayinda Allah yake buɗe idanunmu a wannan zamani namu musamman domin mu fahimci muhimman gaskiya da ke shinfiɗe waɗanda ba'a iya fahimta a zamanin Ikllsisiya ba, akwai abubuwa uku da Allah yake

nuna mana. Waɗannan abubuwan sune, (1) Lokaci da kuma yadda shirin Allah na ceto yake. (2) Yadda ƙarshen zai kasance, wanda ya ƙunshi tsarin lokatai. (3) Yadda shirin Allah na hukumci yake.

A cikin wannan binciken, zamu fi maida hankali ne a kan shirin Allah na ceto. Abu na biyu kuma shine, zamu maida hankali akan abubuwa da suka shafi ƙarshen zamani. Yadda shirin hukumcin Allah yake kuma, za mu fitar da shi a cikin wani ɗan littafi nan gaba.

A cikin Ibraniyawa 8:10-11, Allah ya umurce mu da cewa:

> **Wannan shi ne alkawarin da zan yi da jama'ar Israila, bayan kwanakin nan, in ji Ubangiji, wato, zan sa shari'una a birnin zuciyarsu. Zan kasance Allahnsu, su kuma su kasance jama'ata. Ba kuma sai sun koyawa ɗan garinsu ba, balle wani ya ce ɗan'uwansa, 'ka san Ubangiji! Domin kowa zai san ni, Daga ƙaraminsu, har zuwa babbansu.**

Waɗannan ayoyi suna maida hankali ne akan shirin Allah na ceto. Dukan shekarun nan na zamanin Ikklsiya, abin da ya riƙa faruwa shine, sai wani yazo ya sami wani ɗan'uwa ko wata 'yar'uwa ya fara faɗa masu yadda tabbas cewa suna da ceto, ko kuma, yadda zasu iya samun ceto. Idan ka binciki wannan koyaswar sosai, sai ka gane cewa cikin dukan su, akwai abin da ya kamata mutumin yayi kafin ya sami ceto. Waɗannan abubuwan sun haɗa da abubuwa kamar su baftisma ta ruwa, shaidar bangaskiya, karɓar Yesu ya zama Mai-Ceto, cin jibi ko kuma yin wata irin addu'a. Cikin dukan waɗannan, akwai inda aka saɓawa dokar Allah, wadda ta shaida cewa Kristi ya gama dukan aikin ceton mutum, tun ma kafin a haifi mutumin.[2]

A cikin Ibaraniyawa 8:10-11 inda muka yi karatu, Allah yana nanata cewa da zaran cikakken bayyani na Littafi Mai-Tsarki ya fito, dukan koyaswar da ta shafi ceto a cikin duniyar nan zata zama daga cikin Littafi Mai-Tsarki. Ba za'a ƙara koyawa mutum yadda zai sami ceto ba, sai dai a koyas da cewa ceto gaba ɗayansa, aiki ne na Allah. (Afisawa 2:8-9). Allah zai ci gaba da ceton ɗinbin mutane waɗanda ba su da wani sanin Littafi Mai-Tsarki mai zurfi.

Za mu yi ƙoƙari mu shinfiɗa wata 'yar koyaswa mai sauƙi daga cikin Littafi Mai-Tsarki wadda ta shafi ceton ɗinbin mutane, wanda ba mai iya ƙirgawa, waɗanda ake ceta a kwanakin nan na mu.

1. Littafi Mai-Tsarki ya umurci dukan masu bi na gaskiya da su aika da Bishara ko ina cikin duniya. Allah ya jagoranci ƙirƙiro hanyoyin sadarwa kamar su radiyo da na'ura mai ƙwaƙwalwa, domin kowane mutum a duniya ya iya jin Bishara.

---

2. Ana gayyatar ka ka rubuto domin a aika maka ƙaramin littafi mai suna *Ina Begen Allah zai Cece Ni* domin samun ƙarin bayani a kan wannan batun.

2. A cikin shirin Allah wanda ya fi gaban ganewa, mutanen da basu san wani abu game da Littafi Mai-Tarki ba, zasu fara gane abubuwa kamar su:

a. Su masu zunubi ne kuma suna kan hanyarsu zuwa mummunan ƙarshe inda zasu karɓi hukumci sabili da zunubansu.

b. Littafi Mai-Tsarkin nan da suke jin labari akai kuma wanda a yanzu suka fara sauraro, lallai maganar Allah ne, sabili da haka, sai su fara ƙoƙarin yin biyayya da umurnan shi.

c. Zasu gane cewa ranar shari'a ta kusa, sai dai kuma, Allah yana ceton mutane.

d. Za su gane cewa suna iyawa, kuma dole suyi kuka ga Allah domin jinƙai, suna begen Allah zai cece su.

Abin da duniya take ciki a yau kenan, yayinda mutane da yawa daga ko'ina cikin duniya ke samun ceto ta wurin aikin Allah. Idan Allah ya ceci mutum, Ya kan ba mutumin sabon, rayayyen ruhu na har abada. Sabili da haka, sukan sami babban marmarin yin biyayya da Littafi Mai-Tsarki. Karin yawan mutanen da ke samun ceto a yau, kamar yadda Littafi Mai-Tsarki yake ta nanatawa (Wahayin Yahaya 7:9-14), yana da nasaba ne da gaskiyar cewa a wannan lokacin, Allah yana bayyana gaskiyar Littafi Mai-Tsarki, wadda mutane ba su sani ba a da.

# Sura TA 2:
# Littafi Mai-Tsarki ya bada jeren lokaci na tarihi

Ta wurin binciken Littafi Mai-Tsarki a hankali, yanzu mun iya gane cewa Littafi Mai-Tsarki ba wai kawai littafin dokoki wanda ke nuna yadda Allah yake gudanar da duniya ba ne, amma littafi ne da aka ba mutane domin su iya sanin jerin lokuta na Allah tun daga tarihi. Mun karanta a cikin littafin Maihadisi 8:5-7 cewa:

> **Muddin ka kiyaye umarnin sarki, gidanka lafiya, mai hikima yakan yi abu, ya kuma san lokacin yi da hanyar da ta dace da yinsa. Akwai lokacin da ya dace, da hanyar da ta dace na yin kowane abu, ko da yake wahalar mutum ta yi masa yawa. Ko ɗaya daga cikinmu ba wanda ya san abin da zai faru, wanene zai faɗa mana?**

A waɗannan ayoyin, kalmar nan umurni daidai take da doka. Sabili da haka, wannan na nuna cewa ba sanin dokar Allah kaɗai mai bi na gaskiya wanda ya san shari'ar Allah musamman ma yadda suka shafi yadda hukumci zai kasance zai yi ba, amma zai iya sanin lokutan da Allah ya tsara domin gudanar da abubuwa a wannan duniya.

Wannan shi ya sa mai bi na gaskiya zai iya sanin tsarin lokatai da abubuwa suke faruwa, wannan kuma ya haɗa da gaskiyar lokacin da duniya zata kai ga ƙarshe. Ga waɗanda basu bi yadda Littafi Mai-Tsarki ke fasarra kansa daki-daki ba, Kristi zai zo kamar ɓarawo da dare. Da zaran sun gane cewa ƙarshen duniya ya abko masu ba shiri, nan take sai baƙinciki ya rufe su. Daga nan ba za'a ƙara samun jinƙai ko alheri ko ceto ga waɗanda basu rigaya sun sami ceto ba. Shi ya sa 1 Tassalunikawa 5:2-6 ke cewa:

> **Lokacin da mutane ke cewa, 'Muna zaman salama da zaman lafiya,' wuf, sai halaka ta auko musu, kamar yadda naƙuɗa ke kama mace mai ciki, ba kuwa hanyar tsira. Amma, ai, ba a cikin duhu kuke ba, 'yan'uwa, har da ranan nan za ta mamaye ku kamar ɓarawo. Domin duk mutanen haske kuke, na rana kuma. Mu ba na dare ko na duhu bane. Ashe, saboda haka, kada mu yi barci yadda waɗansu ke yi, sai dai mu zauna a faɗake, da natsuwa.**

Haka kuma mun karanta a cikin Wahayin Yahaya 3:3 cewa:

> **Don haka sai ka tuna da abin da ka karɓa ka kuma ji, ka kiyaye shi, sa'an nan ka tuba. In ba ka yi tsaro ba, zan zo kamar ɓarawo, ba kuwa za ka san lokacin da zan auko maka ba.**

A waɗannan ayoyin, Allah yana koya mana cewa waɗanda ke karanta Littafi Mai-Tsarki sun kasu kashi biyu. Akwai waɗanda suke dangana ga dangantakar da suke da ita da Allah a yanzu. Sun sani cewa wata rana

duniya zata ƙare, amma abin da suka sani shine lokacin da wannan zai faru, Allah ne kaɗai ya sani. Sabili da haka, a ganin waɗannan mutanen, bai ma kamata mutum ya dami kansa da wannan ba. A garesu, hakika Kristi zai zo kamar ɓarawo da dare. Sai dai kuma, zai dawo ne domin ya hallaka irin waɗannan mutanen. Abin baƙinciki.

Sai dai kuma, akwai waɗanda suka gane cewa Allah ya shinfiɗa sadarwa mai yawa game da tsarin lokacin a cikin Littafi Mai-Tsarki. Sabili da haka sun koyi abubuwa da dama game da lokacin da aka halicci duniya da kuma manya manyan abubuwan da suka yi ta faruwa waɗanda ke rubuce a cikin Littafi Mai-Tsarki. Sun kuma koyi abubuwa da dama game da lokacin da duniya zata zo ga ƙarshe. A garesu, ƙarshen duniya ba zai zo musu ba shiri ba.

## Yadda Allah ya shinfiɗa shirinsa na ceto a cikin jeren kwanaki na tarihi.

Littafi Mai-Tsarki ya koyas da yadda Allah ya bada saƙon Bishara ga mutum a cikin tsarin lokaci na tarihi. Bishara ta ƙunshi dukan Littafi Mai-Tsarki. Sabili da haka, mun iya ganewa da shirin Allah na ceto ta wurin binciken Littafi Mai-Tsarki a hankali.

A cikin shekaru 9,500 na farko, Allah bai yi amfani da wata ƙungiya a wannan duniya a matsayin wakiliyar mulkin Allah a nan duniya ba. A wannan lokacin, Allah ya riƙa amfani da mutane ɗaya ɗaya ne domin su zama jakadun mulkinsa. Kayinu, Enoch, wanda aka ɗauka zuwa sama, Nuhu da iyalinsa, Ibrahim, Ishaku, da Yusuf duka sunaye ne da Allah ya lisafta a cikin Littafi Mai-Tsarki a matsayin wakilan mulkin Allah.

Yayinda muke ci gaba da binciken Littafi Mai-Tsarki, mun gane cewa an halicci duniya wajen shekaru 13,000 da suka wuce.[3]

Littafi Mai-Tsarki ya hakikance wannan, sabili da haka idan muka kwatanta kalandar Littafi Mai-Tsarki da kalandar da muke da ita a yau, mun sani cewa an halicci duniya ne a shekara ta 11,013 kafin haihuwar Yesu.

Da alama, a cikin shekaru 9,500 na farkon tarihin duniya, mutane kaɗan ne suka sami ceto. A misali, a zamanin Nuhu, a cikin dukan mutanen da ke duniya a cikin shekara ta 4,990 kafin haihuwar Yesu, lokacin da Allah ya hallaka duniya da ruwa, mutum takwas ne kaɗai suka sami tsira.

## Isra'ila a cikin shekarun da suka kama daga 1447 B.C zuwa A.D. 33

Sai dai kuma, a cikin shekara ta 1,447 kafin a haifi Yesu, Allah ya sake wani sabon shiri na yadda za'a wakilci mulkinsa a nan duniya. A cikin

3.Ana gayyatarka ka rubutowa Family Radio domin a aika maka kyautar littafi mai suna *Adamu Yaushe* , wanda ya nuna yadda Littafi Mai-Tsarki ya yi waɗannan bayanan.

wannan shekara, Allah ya fara amfani da 'ya'yan Isra'ila a matsayin wakilan mulkin Allah. A cikin wannan shekara ne Isra'ilawa suka baro Masar ƙarƙashin jagorancin Musa. Isra'ilawa sun ƙunshi zuriyar Ibrahim, wanda aka haifa fiye da shekaru 700 da suka wuce. An haifi Ibrahim a shekara ta 2,167 kafin haihuwar Yesu a wata ƙasa da ake kira Ur ta Caldiyawa ko kuma Babila. A cikin shekara ta 2,092 kafin haihuwar Yesu, shi da matar sa Saratu suka yi biyayya da Allah, suka fita zuwa ƙasar Kan'ana. Sune suka zama tushen 'ya'yan Isra'ila, kuma Allah ya yi amfani da ƙasar Kan'ana a matsayin wakilan mulkin Allah a nan duniya.

'Ya'yan Isra'ila haɗe da ƙasar Kan'ana, sune suka zama ginshiƙin bayyanuwar shirin Allah har na shekaru 2,100 kafin haihuwar Yesu Kristi. A gaskiya ma, Yesu Ɗan Allah ya sami yanayinsa na mutumtaka a matsayin tsatson Ibrahim.

A cikin shekara ta 1,447 kafin haihuwar Yesu, zuriyar Ibrahim waɗanda ake kira Isra'ila sun ƙasaita har sun zama al'umma mai-wajen mutane miliyan biyu. A cikin wannan shekara ne suka fita daga cikin bauta a Masar. Daga wannan lokacin har wajen shekaru 1,480 masu zuwa, an yi ta kiran Isra'ila mutanen Allah. An yi ta ba su dokokin Allah. Sun zama wakilan Allah a nan duniya.

Allah ya ba 'ya'yan Isra'ila ƙasa, watau ƙasar Kan'ana, wadda kuma ake kira ƙasar Isra'ila a matsayin wurin zama, da kuma haikali domin yin sujada. Ya basu dokoki, waɗanda muke kira dokoki da alamu, waɗanda ya kamata a kiyaye domin waɗannan dokokin suna jagorantar 'ya'yan Isra'ila ga zuwan Mai-Ceto, watau Yesu Kristi. Waɗannan dokokin na alamu sun haɗa da kiyaye ranakun bukukuwa, sabon wata, ranar asabaci, hadayu na ƙonawa, hadayu na jini da dai sauransu.

Allah yayi amfani da abubuwa na duniya kamar su Kan'ana, Isra'ila, Yahuda, Urushalima, Zaitun, haikali, Yahudiya da dai sauransu domin su zama kwatancin mulkin Allah. Shi yasa, aka yi ta ambaton waɗannan kalmomin a cikin Littafi Mai-Tsarki suna wakiltar mulkin Allah na ruhaniya. A misali, a zamanin Ikklisiya, Ikklisiyoyi sune wakilan mulkin Allah. Sabili da haka, Littafi Mai-Tsarki yayi ta amfani da kalmomi kamar su Isra'ila, Yahuda, haikali da dai sauransu yayinda yake magana akan Ikklisiyoyin zamanin Ikklisiya.

Wani abu da ya zamo jiki ga 'ya'yan Isra'ila shine dokokin da Allah ya bayar game da yadda za'a zaɓi Firistoci, Lawiyawa, annabawa da sarakuna waɗanda zasu yi mulki a bisan dukan jama'a. Wannan wani shiri ne da Allah da kansa yayi domin ya zama alama ta mulkin Allah a wannan duniya. Kowane Bayahude zuriyar Ibrahim yana cikin wannan ƙungiyar. Domin a tabbatar da kasancewa a cikin wannan ƙungiyar, dole ne a yi wa kowane ɗa namiji kaciya, wadda ita ma ta zama ɗaya daga cikin dokoki na misali waɗanda Allah ya kafa ta wurin dokar sa.

Littafi Mai-Tsarki ya bamu sadarwa mai yawa game da shekarun da suka gabaci kafuwar al'ummar Isra'ila da kuma shekarun tarihinta dubu na farko. Littafi Mai-Tsarki ya bada cikakken labari game da Isra'ila, a matsayin

al'umma, lokacin da Allah ya ƙwato su daga bauta ya kuma fitar da su daga Masar, lokacin da suka ƙetare jan teku a bisa sandararriyar ƙasa, wani abu mai ban al'ajibi. Daga nan sai Littafi Mai-Tsarki ya bada labarin shekaru 360 da suka biyo baya a cikin tarihin Isra'ila, yayinda Allah yake mulkin su, yana kuma amfani da waɗansu mutane da ya kira alƙalai a cikin ƙasar Kan'ana.

Daga nan sai aka bamu labarin shekaru 116 da suka biyo baya, lokacin da Isra'ila ta yi suna sosai a duniya, lokacin da sarki Saul yake mulki a bisa kansu, bayan shi kuma sai Dauda, daga nan sai sarki Sulemanu.

Har wa yau, Littafi Mai-Tsarki ya bada labarin rabuwar wannan ƙasar da a da take ƙasa ɗaya, wadda ta ƙunshi kabilu 12 na Isra'ila. Bayan mutuwar Sulemanu, kabilu goma sun ware kansu suka kira kansu Isra'ila, wadda babban birninta shine Samariya, sauran kabilun biyu kuma suka zama Yahuda, babban birnin su kuma shine Urushalima. Littafi Mai-Tsarki ya bada labarai masu dama game da waɗannan masarautun da kuma sarakunan da suka yi mulkin a bisan su.

Littafi Mai-Tsarki ya kuma bada labarin yadda suka ƙarasa. Asiriyawa sun ci kabilun nan goma na Isra'ila da yaƙi a cikin shekara ta 709 kafin zuwan Yesu. Kana a shekara ta 587 Kafin zuwan Yesu, sarkin Babila ya ci Yahuda da yaƙi inda aka lalata babban haikalin nan da Sulemanu ya gina a Urushalima.

Sai dai kuma, bayan lalatawar Urushalima a cikin shekara ta 587 kafin haihuwar Yesu, sai labarin abin da yake faruwa da waɗannan kabilun 12 na Isra'ila ya zama da ƙaranci. Mun ji cewa a cikin shekara ta 539 kafin haihuwar Kristi, mutane wajen 40,000 waɗanda suka rayu lokacin da mutanen Babila suka lalata Urshalima, sun dawo Urushalima. Mun sami 'yan labarai kaɗan game da ƙudurin sake gina haikalin, wani yunƙuri da aka iya kammalawa a shekara ta 515 kafin zuwan Yesu. Mun ji kaɗan daga cikin abubuwan da waɗannan da suka dawo suka shiga ciki daga cikin littattafan Littafi Mai-Tsarki da aka ba sunaye, Ezra, Nehemiah da Esta.

Sai dai kuma daga shekara ta 391 kafin zuwan Yesu har shekara ta 8 kafin zuwan Yesu, shekaru wajen 400 na tarihin Isra'ila, Littafi Mai-Tsarki bai ce komai game da ƙasar Isra'ila, mutanenta, ko wata ƙasa ta duniya ba.

Abin baƙin cikin shine, cikin dukan zamanin da Isra'ila ta kasance, mutane ƙalilan ne suka sami ceto. Littafi Mai-Tsarki na cike da kalamai game da zunubi, kaucewa Allah, da kuma tawayen 'ya'yan Isra'ila gaba da dokokin Allah. Har ma lokacin da Yesu ya zo a matsayin Mai-Ceto, wanda a kasancewar sa ta mutumtaka, shima zuriyar Ibrahim ne, sun yi tawaye, suka kuma ƙi su ɗauke shi a matsayin Mai-Ceto. A gaskiya ma, sun ƙarasa da kashe shi (Ayyukan Manzanni 2:22-23).

Littafi Mai-Tsarki ya tabbatar mana cewa Kristi shine babban abin alherin da ya fito daga cikin Isra'ila. Daga cikin Bani Isra'ila ne Allah ya ɗauki jikin mutum, budurwa Maryamu ta haifeshi, wanda kuma daga kabilar Yahuda ne.

Daga shekara ta 8 kafin haihuwar Yesu, Littafi Mai-Tsarki ya fara bamu cikakken labari game da Yahudawa. A cikin wannan shekara, an sanar

da haihuwar Yahaya mai-baftisma, kuma Yahaya ne zai sanarwa duniya cewa Mai-Ceto, Ubangiji Yesu Kristi, Ɗan Rago na Allah, ya zo domin ya ɗauki zunubin duniya duka. Yesu Kristi kaɗai ne hanyar da mutum zai iya samun biyan bashin zunubansa, ta wurinsa kuma, mutumin zai iya samun sulhu da Allah.

Daga lokacin da aka haifi Yesu a shekara ta 7 B.C. har zuwa A.D. 65, Littafi Mai-Tsarki yayi ta bada labarin Bani Isra'ila. A cikin wannan lokacin ne abinda yafi kowanne ban mamaki a duniya ya faru. Allah, Ubangiji Yesu Kristi, ya ɗauki sifar ɗan adam ta wurin haihuwarsa da budurwa Maryamu tayi. Cikin wannan lokacin ne, Yesu yayi wa'azi na wajen shekaru uku. An giciye Yesu a shekara ta A.D 33. Ya tashi daga matattu ya kuma hau zuwa sama. Wannan shekara ta A.D. 33 ta zama ƙarshen shekaru 1,480 na wakilcin mulkin Allah da 'ya'yan Isra'ila suka yi.[4]

## Farkon Zamanin Ikklisiya

Bayan hawan Kristi zuwa sama da 'yan kwanaki kaɗan, ƙungiyar da Allah ya shirya ta yi wakilcin mulkin Allah a nan duniya har na tsawon shekaru 1,955 ta samo asali.

A ranar Pentakos cikin shekara ta A.D. 33, kimanin mutane 3,000 suka sami ceto (Ayyukan Manzanni 2). Waɗanda suka sami ceto a wannan ranar sun fito ne daga ƙasashe dabam dabam. Wannan babban al'amarin ya zamo farkon zamanin Ikklisiya. A wannan sashen a zamanin Ikklisiya ne aka bada cikakken labarin masu wa'azin da aka yi ta aikawa ƙasashe dabam dabam waɗanda ayau muka sani da Turkiya, Greece da Italiya.

Allah ya kafa zamanin Ikklisiya a matsayin wani shiri nasa na aikawa da Bishara zuwa ko'ina a cikin duniya. A yanzu, ba za a ƙara yin amfani da haikalin Yahudawa, ko birnin Urushalima, ko Bani Isra'ila, ko kuma haikalin da ke cikin Urushalima a matsayin wakilan Allah a nan duniya ba. Yanzu, ƙungiyoyin masu bin da za a kafa a ko'ina cikin duniya sune zasu zama wakilan Allah. Wannan shi ya sa a cikin ruhaniya, Littafi Mai-Tsarki ya kira waɗannan ƙungiyoyin 'haikalin,' 'Isra'ila' 'Yahuda' 'Yahudiya,' da dai sauransu.

Wannan ƙungiyar da Allah ya shirya, wadda daga ƙarshe ta ƙunshi majami'u da ke kafe a ko'ina cikin duniya. Allah kuma ya kafa dokoki masu ƙarfi a cikin Littafi Mai-Tsarki waɗanda ke jagorantar yadda za'a yi zaɓen dattiɓai da shugabanni (1 Timatawus 3). Mata ba zasu yi koyaswa ko kuma su riƙe matsayi a cikin majami'a ba. Ba za'a ƙara kiyaye dokokin alamun da ke cikin Tsohon Alkawali waɗanda aka ba 'ya'yan Isra'ila ba. A maimakonsu, an gabatar da sababbin dokoki guda biyu waɗanda zasu taimaka wajen

4.Ana gayyatarka, ka rubuto a aika maka kyautar littattafai *Karshen Zamanin Ikkilisiya* da kuma *Alkama da Zawan* domin samun ƙarin bayani a kan ƙarshen zamanin Ikkilisiya.

koyas da yadda Bishara take. Waɗannan dokokin sune baftisma ta ruwa da kuma jibin Ubangiji. An kafa doka game da fitar da mutum daga cikin majami'a ( 1 Korantiyawa 5). Allah ya zaɓi ranar lahadi ta zama ranar da za'a kiyaye, wadda kuma za'a mora domin ayyuka iri dabam dabam na ruhaniya. Dokokin da ke cikin Littafi Mai-Tsarki kuma sune zasu jagoranci kowacce majami'a da za'a kafa a ko'ina cikin duniya.

Babban aikin da aka ba majami'un nan da Allah ya kafa shine su kai Bishara ko'ina cikin duniya. Mun riga mun ga cewa tun ma kafin a gama rubuta Littafi Mai-Tsarki, an rigaya an fara aikawa da masu wa'azi zuwa ƙasashen da ke maƙwabtaka da su (Ayyukan Manzanni 13).

A wajen shekara ta A.D. 95, Allah ya kammala rubutun Littafi Mai-Tsarki, kuma daga nan, ba wani labari da ya fito daga Allah wanda ke bayyana yadda majami'un nan suke ci gaba a duniya a matsayin tarihin majami'un. Sai dai kuma, tun kafin zamanin Ikklisiya ya fara, Allah ya yi anabcin yadda zamanin Ikklisiyar zai kasance.

Mutum na iya zaton cewa tun da zamanin Ikklisiya ya fara a cikin shekara ta A.D. 33 da zargi, inda fiye da mutane 3,000 suka sami ceto a cikin rana ɗaya (Ayyukan Manzanni 2), zamanin Ikklisiya zai zama da babbar nasara. Amma, Littafi Mai-Tsarki yayi anabcin cewa ba haka Allah ya shirya ba. Cikin baƙin ciki, mun koya daga cikin Littafi Mai-Tsarki cewa tun ma kafin a kammala rubuta Littafi Mai-Tsarki (wajen A.D. 95), akwai manya manyan alamu da suke nuna cewa lallai zamanin Ikklisiya ba zai ƙarasa da nasara ba.

### Littafi Mai-Tsarki ya san Ikklisiya za ta bijire

A cikin Wahayin Yahaya 2 da Wahayin Yahaya 3, Allah ya faɗa mana yanayin ruhaniyar Ikklisiyoyi guda bakwai. Wannan yanayin nasu ya kasance haka ne bayan wajen shekaru 30 da kafa su. Alal misali, Ikklisiyar dake a Afisus ta bar ƙaunar ta ta fari (Wahayin Yahaya 2:4-5). Ka tuna cewa, ƙaunar Ubangiji shine kiyaye dokokinsa (Yahaya 14:21-23). Sabili da haka, Allah yayi iƙirarin cewa zai kawas da fitilarsu, wadda ta zama alamar hasken Bishara, domin sun daina yin biyayya da umurnin Allah. Allah ba zai ƙara yin amafani da Ikklisiya ya aika da Bishara cikin duniya ba.

A cikin Galatiyawa 1:2-9, Littafi Mai-Tsarki ya faɗi cewa, tun kafin a kammala rubutun Littafi Mai-Tsarki, Ikklisiyar da ke Galatiya ta fara bin wata bishara wadda ba bisharar da ke cikin Littafi Mai-Tsarki bace. A cikin Wahayin Yahaya 2:13, Littafi Mai-Tsarki yace Ikklisiyar Pargamus, Ikklisiya ce wadda Shaiɗan ke mulki a ciki. Wannan aya ta yi magana akan 'mazaunin' Shaiɗan. A cikin Littafi Mai-Tsarki, wannan kalma 'mazauni' yadda aka yi amfani da ita anan, tana nuna mulki ko sarauta. Haka kuma a cikin Wahayin Yahaya 3:1-4, Littafi Mai-Tsarki ya ambaci cewa Ikklisiyar da ke a Sardisu, ta rigaya ta mutu, ko da yake tana da sauran masu bi na gaskiya ƙalilan a cikin ta.

A cikin Matiyu 13:24-30, Littafi Mai-Tsarki ya bada labarin zawan da alkama. Alkama kwatanci ne na masu bi na gaskiya da ke cikin Ikklisiyoyi. Zawan kwatanci ne na marasa bangaskiya waɗanda ke nuna kamar su masu bi na gaskiya ne, har abin ya kai matsayin da sai a rana ta ƙarshe ne Allah zai bada hanyar da za'a iya ware alkama daga zawan ɗin. Wannan na nuna cewa dukan tsawon zamanin Ikklisiya, za'a sami zawan, waɗanda har yanzu suna bautar Shaiɗan, amma kuma suna nuna ƙwazo a cikin Ikklisiya. Ta haka, Shaiɗan zai yi mulkin Ikklisiya ta wurin su, ko da yake, a baki, Kristi ne ke mulkin Ikklisiya.

Tuni ma, Allah yayi anabci a cikin Ishaya 9:1-4 cewa zamanin Ikklisiya ba zai zama da nasara ba. Mun karanta a wurin cewa:

> Ba sauran baƙin ciki ga wadda take shan azaba. Da an ƙasƙantar da ƙasar kabilan Zabalun da na Naftali, amma nan gaba wannan jiha za ta sami daraja, tun daga Bahar Maliya, zuwa gabashin ƙasar a wancan sashe na Urdun, har zuwa Galili kanta, wurin da baƙi ke zaune. Jama'ar da suka yi tafiya cikin duhu, sun ga babban haske! Suka zauna a inuwar mutuwa, amma yanzu haske ya haskaka su. Ka ba su babbar murna, ya Ubangiji, Ka sa su yi farin ciki. Suna murna da abin da ka aikata, kamar yadda mutane ke murna sa'adda suke girbin hatsi, ko sa'adda suke raba ganima. Gama ka karya karkiyar da ta nawaita musu. Da kuma sandan da ake dukan kafaɗunsu da shi. Kai ne, ya Ubangiji, ka kori al'ummar da ta zalunci jama'arka, ta kuma zambace su, daidai da yadda da ka kori rundunar sojojin Madayana tuntuni.

A cikin waɗannan ayoyin, Allah ya kira haske wanda ke haskakawa a sashen Urdun, 'Galili' ( Ka kuma duba Matiyu 4:15-16). Wannan na nufin, dukan ƙasashen duniya zasu kasance ƙarƙashin hasken Bishara. Hasken kuwa shine Ubangiji Yesu wanda shine hasken duniya (Yahaya 1:7-10).

Domin hasken Bishara yana haskakawa ko'ina cikin duniya, dole ne a sami babban canji cikin shirin Allah a watsa Bishara zuwa ga duniya mai cike da duhu na ruhaniya, idan kuma har wannan duhun zai tsara wannan babban duhun (Ishaya 9:2). Haske ne wanda zai kawo mutane daga ko'ina cikin duniya waɗanda zasu nuna a waje cewa su masu bi na gaskiya ne, kamar yadda Ishaya 9:3 ta faɗa, 'Ka ba su babbar murna.' Ma'ana, mulkin Allah cikin wannan duniya zai inganta, ya kuma ƙasaita.

Sai dai kuma, har yanzu a wannan aya, Allah ya ce bai ƙara farin cikin girbi ba. Murnar girbi ita ce murna da ke zuwa yayin da aka ba mutum sabon rai, ya kuma zama mai bi na gaskiya (Luka 15:10). Idan babu murnar girbi, wannan ya nuna cewa girbin masu bi na gaskiya ƙalilan ne. Gaskiyar shine, mun ga wurare da dama a cikin Littafi Mai-Tsarki inda aka yi anabcin cewa ba za'a sami girbi na masu samun ceto ba.

Haɗe kuma da dukan wuraren da muka ga Littafi Mai-Tsarki yayi magana, mun karanta a cikin Ishaya 5 cewa Allah ya kwatanta zamanin

Ikklisiya da wata gonar inabi da Allah ya shuka ya kuma gyara ta da kyau. Amma wannan gonar inabi bata bada 'ya'ya ba. Sai ta fitar da inabin jeji. Ta fannin ruhaniya, inabin jeji yana daidai da waɗanda suka ƙirƙirowa kansu wata bishara tasu ta kansu maimakon su yi biyayya da Bishara wadda ke cikin Littafi Mai-Tsarki. A cikin binciken mu nan gaba, zamu ga cewa shirin Allah ne cewa zai hallaka wannan gonar inabin sabili da wannan muguntar da suka aikata.

A ayoyi da yawa cikin littafin Ishaya, Irmiya Ezikiyel da sauransu, zamu iya ganin cewa Allah ya nuna zafin fushinsa a bisa ƙasashen Isra'ila da na Yahuda domin nacewa da suka yi wajen aikata mugunta. Hakika, a ƙarshe, an hallaka su. Asiriyawa sun hallaka Isra'ila a shekara ta 709 kafin zuwan Kristi, Babilawa kuma suka lalata Yahuda a shekara ta 587 kafin zuwan Kristi.

Allah yayi amfani da Isra'ila da Yahuda waɗanda a zamaninsu, sune ke wakiltar mulkin Allah a nan duniya, kamar yadda majami'u suka zama wakilan mulkin Allah a zamanin Ikklisiya. Yayinda muke karanta waɗannan littattafan na Tsohon Alkawali, muna ganin abin da Allah ya san zai faru a zamanin Ikklisiya, musamman ma ga ƙarshen zamanin Ikklisiyan.

Shi yasa, Allah ya koyas da cewa a zamanin Ikklisiya za'a kafa Ikklisiyoyi ko ina a cikin duniya, wanda zai nuna kamar zamanin Ikklisiya yana samun nasara. Amma gaskiyar ita ce, 'yan kaɗan ne daga cikin waɗanda ke cikin majami'un suke samun ceto, watau suke zama masu bi na gaskiya.

An bayyana wannan tunanin a cikin Romawa 9:27, inda Allah yake ambaton abin da aka rubuta a Ishaya 10:22-23.

> Romawa 9:27: **Game da Isra'ila, Ishaya ma ya ɗaga murya ya ce, 'Koda ya ke yawan Isra'ilawa ya kai kamar yashin teku, duk da haka, kaɗan ne za su sami ceto.**

> Ishaya 10:22-23: **Ko da yake yanzu akwai jama'ar Isra'ila da yawa, yawansu kuwa kamar yashin teku,, duk da haka, sai kaɗan ne za su komo. An tanada wa jama'a halaka, sun kuwa cancanci halakar. Hakika a ƙasar duka, Ubangiji Allah Mai Runduna zai kawo halaka kamar yadda ya ce zai yi.**

## Matsalar Shaiɗan a cikin Ikklisiya

Wani babban dalilin da yasa aka kasa samun nasara ta ruhaniya a zamanin Ikklisiya shine Shaiɗan. A lokacin da Kristi ya hau giciye, an ba Shaiɗan naushi mai hallakaswa. An koro shi daga sama (Wahayin Yahaya 12:7-11), an kuma ɗaure shi domin kada ya ruɗi duniya har sai zamanin Ikklisiya ya cika, wanda aka kwatanta da shekaru dubu (Wahayin Yahaya 20:1-3). Dole ne mu gane cewa an yi amfani da shekarun nan 1000 a matsayin kwatanci

ne kawai na ruhaniya wanda ke nuna 'cika.' Ainihin shekarun da yayi a ɗaure shine 1955, (daga A.D. 33 zuwa 1988).

Daure Shaiɗan na nufin ba zai iya hana shirin da Allah yayi na ceton waɗanda yayi shirin ya ceta tun daga farkon zamani ba. Amma wai domin an ɗaure shi, wannan bai hana shi yin yawo yana ruri kamar zaki yana neman wanda za ya cinye ba (1 Bitrus 5:8). Watau, ko da yake Ikklisiya shirin Allah ne na kai Bishara zuwa ko'ina cikin duniya, duk da haka, Shaiɗan zai hana ta ta iya taka wata rawar gani. Zai hana Ikklisiyar ta yi wani tasiri ta wajen shuka zawan ko ƙaya a cikinsu. (Matiyu 13:24-30. Watau, Shaiɗan yana aiki kamar 'Mala'ikan haske' yana kawo ma'aikatansa a matsayin 'Masu wa'azin adalci' a cikin majami'u (2 Korantiyawa 11:13-15).

A cikin Wahayin Yahaya 6:4. an nuna shi a matsayin mahayin jan doki, ɗauke da babban takobi, wanda shine takobi na Ruhu, Littafi Mai-Tsarki, wanda zai yi amfani da shi ya ɗauke salama daga duniya. Watau, zai yi amfani da kalmomi daga Littafi Mai-Tsarki don ya ƙarfafa koyaswarsa ta ƙarya.

Idan muka haɗa waɗannan ayoyin a Littafi Mai-Tsarki a hankali, zamu iya koyon cewa, hakika, daga waje, zamanin ikklisiya yayi nasara ƙwarai da gaske, domin majami'u sun yi ta bata labarin cewa ɗinbin mutane suna samun ceto. Amma a gaskiya, mutane ƙalilan ne cikin waɗanda ke zumunta a majami'un suka sami ceto na gaskiya.

Zamu iya cewa babbar albarkar da aka samu a zamanin Ikklisiya ita ce ta bugawa da kuma rarraba miliyoyin Littattafi Mai-Tsarki a ko'ina cikin duniya. An rarraba Littafi Mai-Tsarki, hasken Bishara, ko'ina a cikin duniya, ko da yake yawan mutanen da suka zama masu bi na gaskiya kaɗan ne.

Wannan shi ya sa annabcin da aka yi a Matiyu 7:21-23 zai cika sosai ranar da Allah zai zuba fushinsa a bisa duniyar da bata da ceto. Abin baƙin cikin shine, wannan zai rutsa da dukan waɗanda suke cikin Ikklisiya ko'ina a cikin duniya a ranar da aka yi fyaucewa, watau, ranar da za'a fyauce dukan masu bi na gaskiya zuwa saduwa da Ubangiji a cikin sama. A cikin wannan ayar, Allah ya ce:

> **Ba duk mai ce mini, 'Ya Ubangiji, ya Ubangiji,' ne zai shiga mulkin sama ba, sai dai wanda ya yi abin da Ubana da ke cikin Sama ke so. A ranan nan da yawa za su ce mini, 'Ya Ubangiji, ashe, ba mu yi annabci da sunanka ba? Ba mu fitar da aljannu da sunanka ba? Ba mu kuma yi ayyukan al'ajibi masu yawa da sunanka ba? Sa'annan zan ce musu, Ni ban taɓa saninku ba. Ku rabu da ni, ku masu yin mugun aiki.'**

Daga matsayinmu a yau, idan muka duba baya muka yi nazari akan zamanin Ikklisiya, zamu ga cikar anabcin rashin nasarar zamanin Ikklisiyar da Allah yayi. Gaskiya ne ta fara da alamar nasara a cikin shekara ta A.D. 33, a ranar fentakos inda wajen mutum 3,000 suka sami ceto. Amma kamar yadda muka gani, an sami masu koyaswa ta ƙarya a cikin majami'un tun ma

kafin a kammala rubutun Littafi Mai-Tsarki. Haka kuma, Shaiɗan ya fara mulki a cikin Ikklisiyoyi da dama ta wurin shuka zawan a cikin su. Ikklisiyoyin da ke cikin Wahayin Yahaya 2 da 3 sun zama wakilan dukan Ikklisiyoyin da aka kafa a zamanin Ikklisiyar dake cikin Sabon Alkawali.

Haka kuma, idan muka bincike tarihin Ikklisiya, ba zamu yi karo da inda aka sami cikakkar biyayya da Littafi Mai-Tsarki ba. Tarihin Ikklisiya na cike ne da rashin biyayya da Littafi Mai-Tsarki. Inda rashin biyayyar ya fi tsanani shine lokacin sakewa wanda ya faru a turai wajen shekaru ɗari huɗu ko ɗari biyar da suka wuce. Bisa ga tarihi, a wancan lokacin, ɗarikar Katolika ce tafi kowace ɗarika ƙarfi. Wannan ɗarika tayi ƙaurin suna wajen ƙetare dokokin Littafi Mai-Tsarki har abin ya kai ga waɗansu mutane kamar su Martin Luther da John Calvin suka fita daga cikin Ikklisiyar suka kuma zama jagororin ɓallewa daga Ikklisiyar. Da yawa daga cikin Ikklisiyoyin da suka ɓalle daga Roman Katolikan sun yi ƙoƙari su yi biyayya da koyaswar Littafi Mai-Tsarki.

Sai dai ba'a yi nisa ba, sai da yawa daga cikin waɗannan Ikklisiyoyin da suka ɓalle ɗin suka shiga koyas da bishara irin ta mutum mai cewa wai kowa zai iya karɓar Yesu ya zama Mai-cetonsa, da kuma cewa irin wannan karɓar Yesun yana iya sa mutum ya sami ceto. Idan ka duba yawancin taruruka na farkawa da aka yi ta yi a wancan lokaci suna kafe ne a bisa irin wannan bisharar. Abin baƙin cikin shine, wannan bishara ba Bisharar Littafi Mai-Tsarki ba ce. Duk da haka, Allah ya ceci waɗansu mutane a zamanin Ikklisiyar.

### Shin ko dukan Litafi Mai-Tsarki cikakkar Maganar Allah ce?

Ganin cewa a cikin Ikklisiyoyin da suka ɓalle daga Roman Katolika an sami bambamce bambamce na koyaswa da suka shafi ɓangarori da dama na Littafi Mai-Tsarki ya nuna cewa kowace ɗarika takan zaɓi waɗansu ayoyi ne na Littafi Mai-Tsarki waɗanda suke so, sai su kafa koyaswar su ko bangaskiyarsu a kan waɗannan ayoyin. Kowace ɗarika na iƙirarin cewa ayoyin da suka zaɓa cikakku ne marasa kuskure kuma. Wannan shi ya sa sai ka ga kamar koyaswar tauhidin da suka ɗauka suka zamar da su tushen bangaskiyar su, waɗanda kuma suke kafe a daidatawar abin da suka fahimta da shi daga cikin ayoyin da suka zaɓa ɗin abin dogaro akai ne. Sai ka ga kamar da gaske ne koyaswar su na kafe ne akan cikakkar maganar Allah, watau Littafi Mai-Tsarki.

Sai dai kuma abin dake da kamar gaskiya da kuma abin dogaro, ba lallai haka ɗin yake ba. Abin takaicin shine, sau da yawa, akwai kuskuren fahimtar ayoyin da suka zaɓa domin waɗannan masana tauhidin basu bincike Littafi Mai-Tsarki ba. Basu bincike Littafi Mai-Tsarki a hankali suna gwada aya da aya domin su tabbatar cewa matsayin nan da suka ɗauka daidai yake ba. Zaka ga kamar sun ɗauka cewa dukan Littafi Mai-Tsarki cikakke ne, sai dai, sun sa dogaron su a ayoyin da suka zaɓa ne kawai

domin su ƙarfafa koyarwarsu. Ta wurin yin haka, suna musun ikon da kowace ayar Littafi Mai-Tsarki take da ita.

Abin da wannan kuskuren gaskantawa da Littafi Mai-Tsarkin ya haifar kuwa shine, aikawa da bisharar ceto wadda ta yi nisa da gaskiya. Wannan shi ya sa a cikin dukan zamanin Ikklisiya, an yi ta samun banbance banbancen fahimtar koyaswar Littafi Mai-Tsarki tsakanin ɗariku dabam dabam. A misali, Baptist suna jayayya akan koyaswar Littafi Mai-Tsarki da Lutheran, Lutheran da Presbyterians, Presbyterians da Baptist, da dai sauransu.

Mun sani cewa game da kowace koyaswar Littafi Mai-Tsarki, Littafi Mai-Tsarki bashi da kuskure, sabili da haka, akwai amsa guda ɗaya wadda ita ce gaskiya. Sabili da haka, idan ra'ayoyi sun bambanta game da wata koyaswa guda ɗaya, dole za'a sami ɗarika ɗaya ce take koyas da abin da ke na gaskiya, dukan sauran kuma suna koyas da koyaswa ta ƙarya ne.

Sai dai kuma, idan dukan waɗannan ɗarikun suka gaskanta cewa dukan Littafi Mai-Tsarki bashi da kuskure, kuma dole ne tushen bangaskiyarsu ya fito daga ikon Littafi Mai-Tsarki shi kaɗai, to mutum zai iya ɗauka cewa dukan ɗarikun zasu koyas da abu ɗaya daidai da yadda kowace Ikklisiya take koyas da wannan koyaswar.

Haɗe da wannan kuma, akwai sassa dabam dabam na Ikklisiyoyi kamar su Roman Katolika, Mamons, Seventh Day Adventist, da kuma Ikklisiyoyin Karismatic na zamanin nan namu waɗanda suke ikirari a fili cewa koyaswar su na kafe ne a bisa Littafi Mai-Tsarki haɗe da wani wahayi da yazo daga Allah a baya-bayan nan, watau, saƙonnin da aka samu bayan an gama rubuta Littafi Mai-Tsarki. Sabili da haka, daga wajen abin da suke faɗa ma, suna nuna kenan suna da wani tsari wanda ke tafiyar da yadda suke fahimtar Littafi Mai-Tsarki wanda ya sha bambam da ikon Allah, wanda shine Littafi Mai-Tsarki shi kaɗai (Wahayin Yahaya 22:18-19). Dole ne mu gane cewa ba za'a taɓa samun wani ƙari a bisan abin da ke cikin Littafi Mai-Tsarki ba tun da aka kammala shi wajen shekaru 1,900 da suka wuce.

Kamar yadda muka nuna a baya, Allah ya sani ya kuma yi anabci game da dukan waɗannan abubuwan, kuma dole anabcin nan ya cika kamar yadda Allah ya faɗa cewa, 'Baka ...da...murna... a cikin...girbi' (Ishaya 9:3) Ko da yake, watau majami'un dake ko'ina cikin duniya, zasu yi yawa kamar yashin teku, 'yan kaɗan ne zasu sami ceto (Romawa 9:27).

## Zamanin Ikklisiya zai kai ga ƙarshe

Allah yayi anabcin cewa a ƙarshe, zamanin Ikklsiya zai kai ga ƙarshe, daga nan Allah zai kammala girbin zaɓaɓɓunsa, waɗannan da Allah ya zaɓa su sami ceto (Afisawa 1:3-6), ta wurin kawo Bishara ga mutanen da ke waje da shugabancin wata Ikklisiya.

Idan muka dubi Littafi Mai-Tsarki, sai mu ga cewa Littafi Mai-Tsarki ya koyas da cewa za'a yi tsanani na ƙarshe, wanda a cikin Matiyu 24:21 ake kira 'Matsananciyar wahala.' Ayar ta ce:

**A lokacin nan za a yi wata matsanciyar wahala irin wadda ba a taɓa yi ba tun farkon duniya har ya zuwa yanzu, ba kuwa za a ƙara yi ba har abada.**

Wani abu mai muhimmanci shine, a yau, zamu iya waiwayar baya wayen shekaru 2,000 na tarihi wanda ya biyo bayan kammala rubutun Littafi Mai-Tsarki. Kamar yadda muka gani a baya, tarihin da aka samu wanda ba daga cikin Littafi Mai-Tsarki ba, amma wanda ya shafi tarihin Ikklisiyoyi yana koya mana cewa zamanin Ikklisiya bai yi wata nasara daidai da yadda Littafi Mai-Tsarki ya yi anabcin cewa zai faru ba.

Wannan shine ya kawo mu ga wata babbar tambaya. Masu binciken Littafi Mai-Tsarki sun gane cewa duniya zata kai ga ƙarshe, a wannan lokacin ne kuma waɗanda basu da ceto zasu ɗanɗana fushin Allah, waɗanda ke da ceto kuma zasu sami barata, su kasance tare da Kristi a sabuwar sama da sabuwar duniya. Haka kuma, da yawa sun ɗauka cewa wannan zai faru ne a lokacin da Kristi zai dawo kamar ɓarawo da dare. Watau, ba zamu iya sanin daidai lokacin da duniya zata ƙare ba. Wannan ya faru lokatai dabam dabam a cikin tarihi, in da Kristi suka fuskanci tsanani a wurare dabam dabam a duniya, akwai waɗanda suka yi ikirarin cewa zasu iya ƙiyasce shekarar da Kristi zai dawo. Hakika, a dukan lokatan da wannan ya faru, iƙirarin su ya tabbata ba gaskiya ba. Wannan ya faru ne domin ba su kafa matsayinsu a bisa binciken da aka yi a hankali akan dukan abubuwan da Littafi Mai-Tsarki ya faɗa game da dawowar Kristi ba.

A gaskiya ma, cikin dukan zamanin Ikklisiya, Ikklisiyoyi sun ɗauka cewa Ikklisiya zata ci gaba da kasancewa har zuwa ranar tashin duniya, farat ɗaya sai tashin duniya ya zo yayinda Kristi ya bayyana kamar ɓarawo da dare.

Wata babbar koyaswa da ta sha bamban da wannan ta ɓullo a ƙarnin da ya wuce inda koyaswar nan da aka fi sani da 'kafin shekaru dubu' ta shigo, musamman ma a cikin ɗarikar Baptist. Koyaswar na cewa Kristi zai zo kamar ɓarawo da dare ya fyauci Ikklisiya, watau, ya kwashe dukan mutanen da ke cikin Ikklisiya zuwa sama. A wannan lokacin, ko kuma jim kaɗan kafin faruwar wannan, za ayi shekaru bakwai na babban tsanani. Biye da wannan shekarun bakwai, Kristi zai dawo cikin jiki yayi mulki na shekaru 1,000 daga cikin birnin Urushalima. Bayan wannan shekarun 1,000, sai ƙarshen duniya ya zo. Wannan koyaswar, wadda bata akan gaskiya ko kaɗan, tana iya yiwuwa domin akwai ayoyi da dama musamman ma a cikin Wahayin Yahaya, waɗanda suka yi magana akan ƙarshen duniya sai dai suna da wuyar fahimta. Sai a kwanakin nan namu ne muka fara samun fahimtar wuraren da Littafi Mai-Tsarki yayi magana akan ƙarshen duniya.

# Sura ta 3.
# Shirin Allah na jinkirta fahimtar yadda zamanin Karshe zai kasance

Hakika Littafi Mai-Tsarki ya umurce mu da cewar ba zai yiwu mu fahimci wani abu game da kwanakin ƙarshe ba sai lokacin da duniya tayi ƙusan ƙarewa. A misali, akwai ayoyi da dama a cikin littafin Daniyel da suka yi magana akan ƙarshen duniya, sai dai Allah ya umurci Daniyel a sura 12:9 cewa:

> **Sai yace, 'Yi tafiyarka, Daniyel, gama an rufe wannan magana, an kuma kulle ta har ƙarshen lokaci.'**

Ma'ana, masu bi na gaskiya ba zasu fahimci wani abin kirki daga cikin abubuwan da suka shafi ƙarshen zamani ba sai an zo dab da ƙarshen. Shirin Allah ne cewa idan an zo dab da ƙarshen duniya, a lokacin ne masu bi na gaskiya zasu fara fahimtar maganganun da suka shafi ƙarshen zamani domin su kuma su sanar da wannan ga duniya.

Wani abin da Allah yayi domin ya ƙara ɓoye wannan shine, ya bar dukan Ikklisiyoyi su riƙe su kuma koyas da koyaswa irin ta mutum, watau, hanyoyin fassara Littafi Mai-Tsarki wanɗanda ke kafe bisa ra'ayoyin mutane, waɗanda suka sa zukatan masana tauhidi suka kasa fahimtar abubuwa da Littafi Mai-Tsarki ya koyas. Ka tuna cewa mun ga wannan abin baƙin cikin a baya.

Littafi Mai-Tsarki ya faɗa mana a fili cewa Kristi bai koyas da komai ba sai da misalai (Markus 4:34). Misali wani labari ne wanda yake da ma'ana ta ruhaniya. Watau, Littafi Mai-Tsarki gaba ɗayansa, littafi ne na ruhaniya. Maganar Allah ce, kuma Kristi shine Kalmar Allah (Yahaya 1:14). Domin Allah ne ya rubuta, dukan labarbaru na tarihi, maganganun da aka rubuta a ciki, da abubuwan da aka nuna a ciki, Allah ne ya shirya ya kuma tsara kowace kalma da aka rubuta a ciki domin ya koyar da wata gaskiya ta ruhaniya.

Gano gaskiya ta ruhaniya na bukatar binciken Littafi Mai-Tsarki mai zurfi, ana kwatanta aya da aya (1 Korantiyawa 2:13). Har wayau, ana kuma bukata Allah Ruhu Mai-Tarki ya buɗe idanun zuciyar mai neman gaskiyar. Kamar yadda muka gani a baya, ba shirin Allah bane ya bayyana gaskiya da yawa da ke ƙunshe a Littafi Mai-Tsarki, watau, ya buɗe idanun masu neman gaskiya, sai a ƙarshen zamani. Domin ya tabbatar da wannan makantar a zamanin Ikklisiya, Allah bai zaɓi ya buɗe idanun ruhaniyar masu koyas da Littafi Mai-Tsarki a zamanin Ikklisiya waɗanda ke warwatse ko cikin duniya ba. Shi yasa a misali, basu iya gane cewa suna binciken Littafi Mai-Tsarki ta karkatattar hanya ba.

Ana kuma iya bada wani misali na yarda cikin dukan zamanin Ikklisiya, Allah ya hana Ikklisiyoyi fahimtar abubuwa da yawa dake rubuce a Littafi Mai-Tsarki. Waɗanda Allah ya buɗewa idanun ruhaniyar su, sun iya

gane cewa dukan kalmomin suna rubuce a cikin harshen Littafi Mai-Tsarki na farko, sun fito ne daga bakin Allah, domin haka, gaskiya ne kuma abin dogaro akai ne. Yana yiwuwa masu juyawa suyi kuskuren juyawa, amma kalmomin Helinancin ko na Yahudancin da aka juya basu da wani kuskure ko kaɗan.

Damuwar da aka samu ta zargin ainihin juyin Helinanci da na Ibraniyancin ya kahu ne bisan lambobin Littafi Mai-Tsarki. A misali, masana tauhidi sun kasa danganta tsaron mulkin wani sarki kamar yadda aka rubuta shi a wata aya ta Littafi Mai-Tsarki, idan aka kwatanta ta da wata ayar. Sabili da haka, sun tsaya akan cewa ba wuya akwai kuskuren rubutu, watau, kila a wani lokaci, lokacin da ake kwashe ainihin rubutun Littafi Mai-Tsarki, mai kwafewar yayi kuskuren ya canza waɗansu haruffa daga cikin lamba ta ainihin, sabili da haka, sai lambar ta zama dabam da lambar da ke cikin juyi na asalin, kuma wannan kuskuren ya ci gaba yayin da ake samun ƙarin littattafan. Sai suka ce, sabo da wannan dalilin, ba zai yiwu mu gaskanta da kowace lamba da ke rubuce a cikin Littafi Mai-Tsarki ba.

Ɗaukar Littafi Mai-Tsarki ta wannan hanyar na nuna cewa ba zamu iya dogaro ga wani sashi na Littafi Mai-Tsarki ba. Idan har irin wannan kuskuren zai iya faruwa da wata lamba a cikin Littafi Mai-Tsarki, to zai iya faruwa da kowace kalma dake rubuce cikin Littafi Mai-Tsarki, domin haka dole ne mu ce babu wani sashi na Littafi Mai-Tsarki da zamu iya cewa bashi da kuskure.

Sai dai kuma, domin su ƙara nanata ayoyin da suke yin amfani da su wajen koyas da abin da suke koyaswa, masu koyas da Littafi Mai-Tsarki suna shaida cewa Littafi Mai-Tsarki cikakke ne kuma bashi da kuskure. Sai dai kuma a gaskiya, su ma da kansu basu gaskanta cewa haka yake ga kowace aya dake cikin dukan Littafi Mai-Tsaki ba. Idan da sun gaskanta cewa Littafi Mai-Tsarki cikakke ne, da basu yi maganar wani kuskuren kwafewa ba. Ba su gane cewa Allah ya kare kalmar sa yadda kuskuren kwafewa ba zai taɓa faruwa ba. Domin Kristi yayi magana da misalai da gangan domin ya ɓoye waɗansu gaskiya, kuma domin Allah ya ƙyale masana tauhidi na Ikklisiya su yi shakkar waɗansu kalmomin dake cikin Littafi Mai-Tsarki, akwai gaskiya da yawa a cikin Littafi Mai-Tsarki da har yanzu suke a ɓoye.

Akwai misalai guda biyu daga cikin hanyoyi da yawa na yadda Allah ya zaɓi ya bar waɗansu gaskiya da ke cikin Littafi Mai-Tsarki a ɓoye har zuwa lokacin da ya zaɓi ya bayyana su. Dole ne mu gane cewa babu wani mahaluƙin da zai iya cewa ya iya fahimtar Littafi Mai-Tsarki ta wajen saninsa, iyawarsa, tsarkin sa ko kuma adalcinsa. Dole ne mu gane cewa Allah ne kaɗai zai iya buɗe idanun mu mu iya ganin gaskiyar da ke ɓoye a cikin Littafi Mai-Tsarki. Kuma ba shakka yana da shirin sa game da lokacin da zai yi hakan.

Dole ne mu tuna cewa Allah ya kammala rubutun Littafi Mai-Tsarki wajen shekaru 2,000 da suka wuce. Amma shirin Allah ne cewa ba za'a fahimci gaskiya da yawa dake cikin Littafi Mai-Tsarki ba sai a kwanaki na

ƙarshe. Duk da haka, tun kusan shekaru 2,000, masu bi na gaskiya masu ƙwazo, ɗaliban Littafi Mai-Tsarki na gaske suna da Littattafai Masu Tsarki a hannuwansu, kuma sun yi ta ƙoƙarin su fahimci Littafi Mai-Tsarki sosai.

Sabili da haka, zamu iya ganin dalilin da ya sa Allah ya rubuta Littafi Mai-Tsarki ta wata hanya mai wuya. A misali, mun san dalilin da ya sa Allah ya bar Ikklisiyoyi suka manne wa karkatattun hanyoyin fassara Littafi Mai-Tsarki. Domin muna ƙarshen zamani, kuma yanzu ne Allah ya shirya ya bamu ƙarin sani na gaskiyar, domin mu iya fahimtar Littafi Mai-Tsarki fiye da ɗaliban Littafi Mai-Tsarkin da suka gabace mu.

## Yanzu muna zamanin fahimta

Yanzu, mun kawo wannan lokacin. Sabili da haka, ayoyin da a da suka zama da duhu, yanzu muna iya fahimtar su. Sabuwar gaskiya tana fitowa daga cikin Littafi Mai-Tsarki kusan kowace rana. Wannan ya haifar da fahimtar shirin Allah game da ƙarshen duniya. Ta wurin yin amfani da hanyar nan ta kwatanta aya da aya, da kuma fahimtar cewa dole ne mu nemi gaskiyar da ke ɓoye a cikin kowane misali, da kowace magana, da kuma kowane labari na tarihi dake rubuce a cikin Littafi Mai-Tsarki, Allah yana buɗe idanun mu mu fahimci gaskiya iri dabam-dabam wadda aka hana wa masu binciken gaskiyar Littafi Mai-Tsarki da suka gabace mu. Yanzu muna iya fahimtar yadda tsarin abubuwa da suka shafi ƙarshen duniya suke. Wannan iya fahimtar ya fito ne domin muna zamanin da Allah yake buɗe idanun masu bi na gaskiya waɗanda suke binciken Littafi Mai-Tsarki a hankali suna neman gaskiya.

Bari Littafi Mai-Tsarki ya tuna mana cewa shirin Allah ne wata rana masu bi na gaskiya su fahimci wannan. Ka tuna da abin da Allah ya faɗa a cikin Mai hadisi 8:5-7:

> **Muddin ka kiyaye umarnin sarki, gidanka lafiya, mai hikima yakan yi abu, ya kuma san lokacin yi da hanyar da ta dace da yinsa. Akwai lokacin da ya dace, da hanyar da ta dace na yin kowane abu, ko da yake wahalar mutum ta yi masa yawa. Ko ɗaya daga cikinmu ba wanda ya san abin da zai faru, wanene zai faɗa mana?**

A cikin waɗannan ayoyin, Allah yana koya mana cewa, mutum a cikin yanayinsa, ba shi da wani sani lokacin mutuwarsa ko kuma yadda shirin hukumcin Allah ga duniya na ƙarshen zamani zai kasance. Sai dai kuma, a cikin rayuwar mai bi na gaskiya, mutumin da ke da zuciyar mai hikima, shirin Allah ne cewa wannan mutumin zai iya sanin lokacin shari'ar.

Gaskiyar ma ita ce, masu bi na gaskiya zasu san lokatai da yawa daga cikin Littafi Mai-Tsarki, sai dai, a zamanin mu ne kawai masu bi na gaskiya suke samun sanin wannan gaskiyar. Shi yasa, a misali, a zamanin mu ne kaɗai masu bi suka iya sanin jeren kwanakin tarihi wanda ya fara daga halitta a cikin shekara ta 11,013 B.C. daga cikin Littafi Mai-Tsarki.

A cikin 1 Tassalonikawa 5:2-6, an sake nanata wannan furucin dake cikin Mai hadisi sura 8:

> **Lokacin da mutane ke cewa, 'Muna zaman salama da zaman lafiya,' wuf, sai halaka ta auko musu, kamar yadda naƙuda ke kama mace mai ciki, ba kuwa hanyar tsira. Amma, ai ba a cikin duhu kuke ba 'yan'uwa, har ranan nan zata mamaye ku kamar ɓarawo. Domin duk mutanen haske kuke, na rana kuma. Mu ba na dare ko na duhu ba ne. Ashe saboda haka kada mu yi barci yadda waɗansu ke yi, sai dai mu zauna a faɗake, da natsuwa.**

Waɗannan ayoyin suna koya mana cewa ga waɗanda suke dogaro ga saninsu na Littafi Mai-Tsarki, ko kuma hikima ta rayuwar wannan duniya wadda ta ƙunshi ra'ayin cewa bai kamata su ji tsoron ranar shari'a ba, Kristi zai zo kamar ɓarawo da dare. Basu da sani ko kuma ba su yarda da jeren lokacin da Littafi Mai-Tsarki ya bayas ba.

A wani gefen kuma, waɗanda suke tsaro suke kuma a natse, watau, masu kaifin tunani domin Allah ya basu sabon rayayyen ruhu, za su san yadda da kuma lokacin dawowar Kristi.

Amos 3:7 ya ƙara buga ƙusa a kan wannan inda Allah ke cewa:

> **Hakika Ubangiji ba yakan aikata kome ba sai da sanin bayinsa annabawa.**

Da tunanin waɗannan kalmomin a zuciya, mun sani cewa an bamu ikon fahimtar al'amura da suka shafi kwanakin ƙarshe. Ba shakka, bai zama dole waɗannan gaskiyar wadda muka gaskanta cewa ta shafi ƙarshen duniya ta fito daga cikin Littafi Mai-Tsarki ba, sai dai, dole ne a yi mawafuka da sharuɗɗan Littafi Mai-Tsarki.

Littafi Mai-Tsarki ya faɗa mana a fili cewa Kristi zai zo kamar ɓarawo da dare (2 Bitrus 3:10; 1 Tassalunikawa 5:2). Ikklisiyoyi sun yi ta koyas da wannan a cikin zamanin Ikklisiya. Bisa ga ƙoƙarinsu na fahimtar Littafi Mai-Tsarki, Masu koyas da Littafi Mai-Tsarki cike da tsoron Allah sun yi daidai yayinda suka yi ta nanata cewa dole ne mu maida hankali a kan ceton mu domin bamu da tabbacin cewa zamu kasance cikin masu rai gobe. Haɗe da wannan kuma, Ikklisiyoyi da yawa sun yi ta koyas da cewa dole ne mu gane cewa ƙarshen duniya da kuma dawowar Kristi domin shari'a na iya faruwa a kowane lokaci.

Sai dai kuma, kamar yadda muka nuna, babu wani bayyanannen sanin jeren lokacin tarihi a zamanin Ikklisiya. Ba wanda ya iya sanin shekarar da aka kafa duniya, ko shekarar da ruwan tsufana na zamanin Nuhu ya faru, ko shekarar da aka yi wa Ibrahim kaciya, ko shekarar da aka yi wa Yesu baftisma, da dai sauransu.

Rashin cikakken sanin lokacin da abubuwan da suka wuce suka faru, da kuma rashin sanin lokacin da Kristi zai dawo, duka shiri ne na Allah.

Daniyel 12 ta nuna mana wannan, inda muka karanta cewa an umurci Daniyel, wanda aka ba damar sanin abubuwan da zasu faru a zamanin ƙarshe da ya 'rufe kalmomin, ya kuma hatimce littafin sai zamani na ƙarshe' (Daniel 12:4).

Amma yanzu muna zamani na ƙarshe, kuma Allah ya buɗe idanun mu don mu fahimci muhimman kalamun nan kamar irin wanda ke rubuce cikin Mai hadisi 8:5-6 da Amos 3:7.

Sabili da haka, mun rigaya mun gani a baya, Littafi Mai-Tsarki ya koya mana a cikin 1 Tassalunikawa 5:2-6 cewa mutane da yawa a zamanin mu zasu nace cewa Kristi zai zo kamar ɓarawo da dare, sai dai zasu tashi su ga kansu suna fuskantar fushin Allah.

Domin a yau muna goshin ƙarshen duniya, waɗannan ayoyin suna da muhimmanci matuƙa. A cikin kwanakin mu, ta wurin jinƙan Allah, mun iya buɗe jerin lokaci na tarihi ta wurin binciken Littafi Mai-Tsarki a hankali. Ba buɗe mana sadarwar mai yawa da ta ƙunshi jerin lokuta na abubuwa da suka faru a da waɗanda ke rubuce cikin Littafi Mai-Tsarki kaɗai yayi ba, amma Littafi Mai-Tsarki ya bayyana mana abubuwan da dole zasu faru a ƙarshen duniya.

Ba zamu yi mamaki ganin abin ya zama haka ba. A lokacin da Allah ya hallaka duniya a zamanin Nuhu, ya tabbatar da cewa mutanen wannan zamanin suna da cikakken sanin cewa wannan mummunan abun, watau hallaka duniya da babban ruwa, zai faru, haka kuma, ya faɗa masu daidai ranar da abin zai faru. Ba sassaƙa babban jirgin kawai Nuhu yake yi ba, wata sassaƙa da ta zama abin magana a dukan duniya, amma Nuhu da kansa 'Mai-wa'azin adalci' ne (2 Bitrus 2:5). Kwana bakwai kafin ruwan ya fara, Allah ya faɗawa Nuhu daidai ranar da ruwan zai fara (Farawa 7:4,10,16).

Haka kuma, lokacin da Allah yake shirin hallaka mugun birnin Nineveh, Allah ya aiki annabi Yunana ya gargaɗi birnin da cewa, a cikin kwanaki 40, daga randa Nuhu ya fara gargaɗin birnin, za'a hallaka birnin (Yunana 3:4).

Haka kuma, dole ne mu gane cewa a yau, Allah yana bada labarin daidai yadda ƙarshen duniya zai kasance. Dole ne wannan sadarwar ta fito daga cikin Littafi Mai-Tsarki shi kaɗai. Littafi Mai-Tsarki na yau bai sha bamban ba ko kaɗan da Littafi Mai-Tsarkin da aka kammala wajen shekaru 1,900 da suka wuce. Sai dai domin ba nufin Allah ba ne ya fitar da wannan shirin har sai zamani na ƙarshe, wannan sanin na abubuwan da zasu faru a kwanaki na ƙarshe ya zauna a ɓoye a cikin kalmomin Littafi Mai-Tsarki. Sabili da haka, masu binciken Littafi Mai-Tsarki da naciya na wancan lokacin basu iya fahimtar wannan ba.

Duk da haka, shirin Allah ne tun da farko cewa a kusa da ƙarshen zamani, duniya zata sami fahimtar jerin lokatai na kwanakin ƙarshe. Tunda dukan shaidun Littafi Mai-Tsarki suna nuna cewa yanzu muna kwanaki na ƙarshe, muna da tabbacin cewa wannan muhimmiyar sanarwar zata samu a garemu a yau, kuma dole ne mu sanar da ita ga dukan duniya.

Ta wurin binciken dukan sanarwar da Littafi Mai-Tsarki yake bayaswa game da abubuwan tarihin da ke rubuce cikin Littafi Mai-Tsarki, muna iya fahimtar jerin kwanakin abubuwan da zasu faru a nan gaba har zuwa rana ta ƙarshe ta kasancewar duniya. Zamu iya zana waɗansu gaskiya da Littafi Mai-Tsarki ke koyar mana, waɗannan kuwa sun haɗa da:

1. Littafi Mai-Tsarki ya tantance abubuwa. Ba a rubuta shi ta hanyar da zai karfafa ƙididdigewa ko wani dogon tunani ba (2 Bitrus 1:20). An rubuta shi kamar wani littafi na injiniyoyi inda ake bayyana gaskiyar zallan ta.

2. Kowace lamba da ke rubuce a cikin Littafi Mai-Tsarki bata da kuskure ko kaɗan. Ko da yake lambar na iya yin wuyar fahimta, ba zamu ɗauke ta a matsayin kuskure ba.

3. An bayyana ainihin lokacin da abubuwa suka faru na tarihi a cikin Littafi Mai-Tsarki. Misali, Isra'ila ta shafe shekaru ɗari huɗu da talatin a Misira daga ranar farko har zuwa ranar ƙarshe. Isra'ila ta yi tafiya a cikin jeji na tsawon shekaru arba'in daga Misira zuwa ƙasar Kan'ana daga farko zuwa ƙarshe.

4. Sau da dama, amma ba kowanne lokaci ba, Allah yana amfani da waɗansu lambobin Littafi Mai-Tsarki domin bayyana wata gaskiya ta ruhaniya. Yesu Kristi ya jadada muhimmancin ruhaniya da lambobi suke da shi a Matta sura goma sha takwas aya ashirin da ɗaya zuwa ashirin da biyu. Lokacin da Bitrus ya yi tambaya cewa sau nawa ne zai gafartawa ɗan'uwansa, Yesu ya yi amfani da lambobi wajen bayyana amsar sa. Ya faɗa a aya ta ashirin da biyu cewa:

**...Ba sau bakwai na ce maka ba, sai dai bakwai har saba'in.**

Da yake ya kamata mu gafartawa juna kowanne lokaci, mun ga Yesu yana amfani da lambobi wajen bayyana gaskiya ta ruhaniya. Za a iya ambaton waɗannan lambobin kai tsaye su kaɗai ko kuma a cikin waɗansu lambobi. Wannan yana taimakawa ainun wajen danganta al'amura da suka faru shekaru dabam dabam. Ga jerin yawancin lambobin nan.

2- Waɗanda aka umurce su su watsa bishara
3- Nufin Allah
4- Nisan lokaci ko kuma tazarar da Allah yake ambato ta fannin ruhaniya.
5- Kafara, wanda yake jaddada shari'a da kuma ceto.
7- Cikar nufin Allah.
10-Cikar abinda ake magana a kai.
11-Zuwan Kristi na farko, shekaru dubu goma sha ɗaya bayan halitta.

12-Daidaituwar abinda ake magana a kai.
13-Karshen duniya, bayanin abinda ka fara shekaru dubu goma sha uku bayan halitta.
17-Sama
23-Fushin Allah ko shari'a
37-Fushin Allah ko shari'a
40-Gwaji
43-Fushin Allah ko shari'a

Wani misali na yadda zamu iya fahimtar gaskiya ta ruhaniya ta wurin fasa wata babbar lamba na samuwa a cikin Yahaya ashirin da ɗaya. A nan, Littafi Mai-Tsarki yayi magana akan kama kifi guda ɗari da hamsin da uku. Tarun bai fashe ba. An kawo dukan kifayen gaci, wanda ya ke kwatancin sama, ba tare da an yi amfani da jirgin ruwa ba, wanda ke kwatancin majami'u. A fannin ruhaniya, kifin kwatanci ne na dukan masu bi na gaskiya, zaɓaɓɓu, waɗanda za'a ceta daga jahannama, wadda aka kwatanta da teku, bayan zamanin Ikklisiya ya ƙare. Za'a iya raba lambar nan ɗari da hamsin da uku wadda tayi daidai da uku sau uku sau goma sha bakwai. A fannin ruhaniya, lambobin nan na nunin cewa ɗari da hamsin da uku na bayyana shirin Allah (3) na kai dukan waɗanda Allah ya ceta daga fushin Allah zuwa sama (17). Ta haka, wannan lamba ɗari da hamsin da uku na taimakon mu mu iya ganin gaskiyar dake ɓoye a cikin wannan abin da ya faru a tarihi.

5. Wani lokaci, Littafi Mai-Tsarki yakan jawo hankalinmu ga wata lamba wadda ke anabcin wani abu mai zuwa. Alal misali, Daniyel sura goma sha biyu aya ta sha biyu, Allah yayi magana akan mutum mai albarka wanda ya jira har na kwanaki dubu ɗaya da ɗari uku da talatin da biyar. Mun gane cewa wannan anabci ne na zuwan Yesu, wanda aikinsa na ceto ya fara ranar ashirin da shida ga watan Satumba A.D 29, lokacin da aka shaida shi a matsayin Ɗan rago na Allah. Wannan aikin ya ci gaba har zuwa ashirin da biyu ga wata Mayu A.D. 33, ranar Pentakos, lokacin da aka zubo da Ruhu Mai-Tsarki aka kuma fara zamanin Ikklisiya. Tazarar dake tsakanin waɗannan abubuwan biyu kwanaki dubu ɗaya da ɗari uku da talatin da biyar ne daidai yadda Daniyel sura goma sha biyu aya goma sha biyu ta anbata.

6. Dole ne mu gane cewa fahimtar gaskiyar abin da ke cikin Littafi Mai-Tsarki na faruwa ne a daidai lokacin da Ruhu Mai-Tsarki ya ga cewa lokacin fahimtar wannan gaskiyar yayi. Dole ne Allah ya buɗe zukatanmu da idanunmu na ruhaniya kafin mu iya sanin gaskiyar. Sabili da haka, ya kamata a kowanne lokaci a same mu muna addua domin samun wannan ganin na ruhaniya. Wannan kuma haka yake ga sanin jeren lokatai na al'amuran da suka shafi ƙarshen zamani.

7. A cikin Kolosiyawa sura biyu aya goma sha shida da goma sha bakwai, Allah ya faɗa mana cewa ranakun idi, hoto ne na abubuwa masu zuwa. Wannan ayar ta ce:

> **Saboda haka, kada ku damu in wani ya zarge ku kan abinda kuke ci ko abinda kuke sha, ko kuwa kan rashin kiyayewar wani idi, ko tsayawar wata, ko Asabar. Waɗannan kam isharori ne kawai na abinda zai auku, amma Almasihu shine ainihinsu.**

Sabili da haka, zamu iya sa zuciyar ganin bayyanuwar shirin Allah a ranakun idodi. A misali, an giciye Kristi a ranar da ya kamata ayi bikin ƙetarewa. A ranar Pentakos ne aka zubo da Ruhu Mai-Tsarki aka kuma kafa zamanin Ikklisiya. Za mu iya ganin irin wannan abin har ya zuwa rana ta ƙarshe ta kasancewar duniya, wadda ta yi daidai da rana ta ƙarshe ta idin bukkoki.

A cikin binciken Littafi Mai-Tsarkin mu, zamu sami taimako mai yawa idan muka riƙe waɗannan abubuwan, zasu kuma taimaka mana ƙwarai wajen fahimtar Littafi Mai-Tsarki.

Domin muhimmancin wannan lamba ta bakwai ɗin, wadda ke magana akan dangantakar idodin dake cikin Littafi Mai-Tsarki da kuma abubuwan dake faruwa cikin jere-jeren shirin Allah, zai yi kyau a ƙara jaddada wannan maganar. Ta wurin yin haka zamu iya gane tabbacin dake tsakanin al'amura na tarihi. A nan gaba, zamu ga cewa wannan tabbacin ya ci gaba har rana ta ƙarshe ta kasancewar duniya.

**An danganta muhimman datsin lokatai da bukukuwa da suka zama alamu**

Kamar yadda muka gani a baya, yawancin muhimman datsin lokatai suna da mawafaka da waɗansu bukukuwa waɗanda Isra'ilawa ke yi a cikin Tsohon Alkawali. Tsarin Kalandar Littafi Mai-Tsarki tana kafe ne a yawan kwanakin dake tsakanin wani sabon wata zuwa wani, wanda ya sa kwanakin watan Littafi Mai-Tsarki ya zama ko kwana ashirin da tara, ko kuma talatin. Ta wurin binciken kwanakin Littafi Mai-Tarki a hankali, mun iya gane cewa rana ta fari ta kowace shekara ta kan fara ne kusa da farkon faɗuwar ruwa, amma ba kasafai yakan fara a wajen kwana goma sha huɗu kafin saukar ruwan sama ba, wannan yayi daidai da ashirin da ɗaya ko ashirin da biyu ga watan Maris.

Kamar yadda muka gani a baya, Allah ya kafa bukukuwa da dama waɗanda suka yi daidai da shirin Allah na ceto. Waɗannan bukukuwan duka alamu ne na abubuwa masu zuwa. Waɗannan bukukuwan sun haɗa da:

1. Idin ketarewa, ranar goma sha huɗu ga watan ɗaya.

2. Pentakos, wanda kuma ake kira idin girbi, kwana hamsin bayan asabaci ta bakwai, wadda kuma tayi daidai da ranar idin ketarewa kuma ranar asabaci ta fari bayan idin ketarewa.

3. Ranar farko ta watan bakwai rana ce mai muhimmanci wadda masana tauhidi ke kira Idin busa ƙahoni. Idan muka gyara wannan, za'a iya kiran ranar, Idin Jubili. Kahonin da za'a busa a wannan ranar ba ƙahonin azurfan da Littafi Mai-Tsarki ya ambata bane. A wannan ranar, ƙahonin raguna ne za'a busa. Idan aka juya wannan da kayau, Littafi Mai-Tsarki ya kira wannan ranar sujada (Littafin Lissafi 29:1; Firistoci 23:24).

4. Kowace shekara ta biyar, shekara ce ta jubili, wadda ke nanata cewa za'a yi shelar bishara (yanci) ga dukan duniya. An fara shekarun jubili a cikin shekara ta 1407 B.C. lokacin da 'Ya'yan Isra'ila suka shiga ƙasar Kan'ana, kuma an kafa cewa za'a yi wannan bikin bayan kowace shekara hamsin (Firistoci 25:8-13). Ta haka, 7 B.C., shekarar da aka haifi Yesu, ta zama shekara ta jubili. Haka kuma, A.D 1994, wadda ta zo shekaru 2,000 bayan 7 B.C., ita ma shekara ce ta jubili.

5. Akan kira rana ta goma ta watan bakwai, ranar kafara. Ita ma akan kirata ranar jubili (Firistoci 25:9), kuma wannan bikin ya maida hankali ne wajen kawo gafarar da Yesu zai yi ga dukan waɗanda ya zo domin ya ceta.

6. Daga rana ta goma sha biyar zuwa rana ta ashirin da biyu na watan bakwai shine idin bukkoki, wanda kuma shine idin tattarawa.

Abu mafi muhimmanci anan shine, kowace rana ta bukukuwan nan tayi daidai da wani yanki na shirin Allah na ceto. Idan muka harhaɗa dukan abinda muka samu daga Littafi Mai-Tsarki waɗanda suka taimaka mana wajen iya jera kwanakin tarihi har ya zuwa ƙarshen zamani, zamu iya ganin abubuwa kamar haka.

1. Akwai shaidu masu girma dake nuna cewa ba wuya an haifi Yesu wanda shine manufar jubili a ranar biyu ga watan Oktoba shekara ta 7 B.C. Wannan shekarar, shekarar jubili ce. Ranar biyu ga watan Oktoba ta 7 B.C. rana ce ta kafara, ranar da ake busa ƙahon raguna. Ta haka, da ranar kafara da shekara ta 7 B.C, duka suna da mawafuka da jubili. Ka tuna cewa jubili na nuni ne na cewa dole ne ya yaɗa Bishara ga dukan duniya. Kuma Yesu ya zo wannan duniya ne domin ya gama dukan shirye-shirye domin a iya kai Bishara ga dukan duniya. Ta haka, muna iya ganin dangantakar dake tsakanin lokacin haihuwar Yesu, wanda shine tushen jubili, da kuma shekara da ranar da hankalin kowa ya koma ga jubili.

2. Datsi na gaba na shirin Allah na ceto shine ranar da Yesu ya fara aikinsa na Mai-Ceto. A wannan ranar ne aka gabatar da shi ga duniya a

matsayin Ɗan Rago na Allah wanda yazo domin ya ɗauki zunubin duniya duka. Idan muka dubi kalandar mu ta yanzu, wannan ranar ita ce ranar ashirin da shida ga watan Satumba shekara ta 29 A.D. Idan kuma muka dubi kalandar Littafi Mai-Tsarki, ita ce rana ta fari ta wata na bakwai, wadda rana ce ta idin jubili (wadda a cikin kuskure, masana tauhidi ke kira idin busa ƙaho). Hakika zamu iya ganin kamannin dake tsakanin farkon hidimar Yesu, wadda ta zama jubili a garemu, da kuma idin jubili.

3. Yesu, Ɗan ragon hadaya na Allah, ya sha hukumci, kamar yadda dokar Allah ta bukata, ta hanyar da yayi daidai da yadda ya kamata waɗanda ya zo domin ya ceta su sha, yayinda yake biyan bashin zunubansu. Wannan babban hukumcin ya fara ranar alhamis a gonar Getsamani, ya kuma ci gaba har kusan faɗuwar rana ranar juma'a. Wannan mummunan abin ya faru a daidai lokacin da Littafi Mai-Tsarki ya umurta a fara kiyaye idin ƙetarewa. Bisa ga kalandar Littafi Mai-Tsarki, wannan juma'ar itace ranar goma sha huɗu ga wata na fari. A cikin kalandar mu kuma, ita ce ranar ɗaya ga watan Afrilu A.D. 33.

4. Kalandar Littafi Mai-Tsarki ta nemi a kiyaye idin Pentakos a ranar Lahadi ashirin da biyu ga watan Mayu A.D. 33 idan aka kwatanta wannan kiran da kalandar mu ta yau. A wannan ranar ne za'a kawo nunar fari. A wannan ranar kuma, watau ashirin da biyu ga watan Mayu na shekara ta A.D. 33, aka zubo da Ruhu Mai-Tsarki, aka kuma shigar da nunar fari na zamanin Ikklisiya zuwa cikin mulkin Allah. Ka tuna, mun karanta a cikin Ayyukan Manzanni 2:41 cewa mutane wajen 3,000 suka sami ceto a wannan ranar.

5. A kowace ranar Pentakos wadda ta fara tun daga A.D. 33 har zuwa 1988, na jaddada shigo da nunar fari. Sabili da haka, ya kamata zamanin Ikklisiya ya ƙare ne a jajibirin Pentakos ta 1988. Wannan ranar kuwa ita ce ranar ashirin da ɗaya ga watan Mayu 1988. Watau kenan, zamanin Ikklisiya ya ci gaba har tsawon shekaru 1,955 daidai.

6. Yayinda muke ci gaba da wannan binciken, zamu gane cewa zamanin Ikklisiya ya tsaya ranar ashirin da ɗaya ga watan Mayu na shekara ta 1988. Wannan ranar tayi daidai da lokacin da Allah ya fara shirya Ikklisiyoyinsa har ma da duniya baki ɗaya domin abin da Littafi Mai-Tsarki ke kira 'Babban tsanani.' Zamu kuma koyi cewa a cikin kwanaki 2,300 na farkon waɗannan kwanaki 8,400 na tsananin, ba wanda zai sami ceto.

7. Sai dai kuma, kamar yadda zamu gani a cikin wannan binciken, bayan kwanaki 2,300 da fara wannan babban tsananin, babban shirin Allah na ceto wanda shine shiri na ƙarshe ya fara. Wannan ranar kuwa ita ce ranar bakwai ga watan Satumba 1994. A wannan ranar ne Allah ya fara zubo da Ruhunsa Mai-Tsarki, sabili da haka, ɗinbin mutane a ko'ina a duniya zasu ci gaba da samun ceto har na tsawon shekaru goma sha bakwai.[5]

Hakika, ba wanda ya fahimci wannan babban abin da Allah yayi a lokacin da yake yinsa. Amma Littafi Mai-Tsarki ya tabbatar mana cewa wannan abin ya faru. Bisa ga kalandar Littafi Mai-Tsarki, ranar bakwai ga Satumba ita ce rana ta fari ga wata na bakwai, ranar da ake kiyaye idin jubili. A wannan shekara, 1994, lokacin da wannan babban abin ya faru, shekara ce ta jubili daidai kamar 7 B.C., lokacin da aka haifi Yesu, ita ma shekarar jubili ce . Anan, mun sake ganin dangantakar dake tsakanin shirin Allah na ceto da kuma ranakun idin da ke cikin Littafi Mai-Tsarki.

## Shinfiɗaɗɗun al'amura da suka shafi shiri na ceto

Ta wurin binciken Littafi Mai-Tsarki a hankali, mun iya gane muhimman matakan shirin ceton duniya da Allah ya shinfiɗa. Kowane abu yana shinfiɗe ne a bisa kyakkyawan shiri da kuma jeren lokaci wanda ke bayyane a cikin shari'ar Allah watau Littafi Mai-Tsarki. Ga waɗansu misalai:

1. Isra'ila na cikin Masar har shekaru 430 (Fitowa 12:40-41). Waɗannan shekarun kuwa sune 1877 B.C. zuwa 1447 B.C.

2. Bayan 'Ya'yan Isra'ila sun bar Masar a cikin shekara ta 1447 B.C., sun yi shekaru 40 daidai kafin suka kai kogin Urdun, wanda da tsallakashi, sai a shiga ƙasar Kan'ana.

3. Kamar yadda Daniyel 12:12 ta yi anabci, kwanakin da Kristi yayi yana aikinsa na Mai-Ceto, kwana 1,335 ne daidai. Ya fara aikinsa ranar 26 ga watan Satumba A.D. 29 lokacin da aka sanar da shi a matsayin Ɗan rago na Allah (Yahaya 1:29). Bayan kwanaki 1,335, ranar 22 ga watan Mayu A.D 33, aka zubo da Ruhu Mai-Tsarki wanda ya shigo da zamanin Ikklisiya.

---

5 A cikin Ezekiyel 39:29, mun karanta cewa, **"Ba kuma zan ƙara kawar da fuskata daga gare su ba, sa'ad da na saukar da Ruhuna a kan jama'ar isra'ila, ni Ubangiji na faɗa"** maganar nan , **"Ba kuma zan ƙara kawar da fuskata daga gare su ba"** yana nuna shirin ceton Allah na ƙarshe, da ya zo a ƙarshen lokacin babban tsanani. Mun san wannan gaskiya ne, domin shirin Allah na ceto, a lokacin shekaru 1,480 da Isra'ila suka wakilci mulkin Allah, da kuma a lokacin shekaru 1,955 na zamanin Ikkilisiya, lokacin da dukan Ikkilisiyai suke wakiltar mulkin Allah, dukan zamanan biyu sun ƙare inda Allah ya juya masu baya. Sai a lokacin taruwa ta ƙarshe, a lokacin babban tsanani na ƙarshe ne, Allah ba zai sake juya masu baya ba. Ka kuma duba Joel 2:28-32, inda Allah yake Magana game da aiko da ruhu Mai-Tsarki. An ambaci waɗannan ayoyin a cikin Ayyukan Manzanni 2:17-21. A Joel sura ta 2, an maida hankali kan saukowar Ruhu Mai-Tsarki lokacin tsanani. A cikin Ayyukan Manzani 2, an maida hankali ne kan zuwan Ruhu Mai -Tsarki a lokacin Fentikos a shekarar A.D 33 da kuma babban tsanani.

4. Zamanin Ikklisiya ya ɗauki shekaru 1,955 domin ya fara ne a ranar 22 ga Mayu A.D. 33 Ya kuma ƙare ranar 21 ga Mayu A.D 1988.

5. Shekaru 13,000 ne daidai daga halitta wadda aka yi a shekara ta 11,013 B.C zuwa ƙarshen zamanin Ikklisiya, wanda kuma shine ya buɗe babin shirin Allah na ceto na ƙarshe kafin shari'a. Mun kuma gane cewa wannan ya fara ne a shekara ta 1988.

6. Shekaru 7,000 daidai daga ruwan tsufana na zamanin Nuhu wanda ya lalata dukan abin da yake a duniya a shekara ta 4990 B.C., zuwa shekara ta 2011, wadda kamar yadda muka sani, ita ce ranar da Allah zai hallaka wannan duniya ya kuma sake halittar sabuwar sama da sabuwar duniya.

7. Zamu iya gani, kamar yadda aka anbata a Daniyel 8:14 cewa kwanaki 2,300 ne ke tsakanin farkon tsananin wanda aka fara ranar 21 ga Mayu 1988, zuwa ranar da aka zubo da Ruhu Mai-Tsarki, wanda ya faru ranar 7 ga Satumba 1944, wanda kuma shine rana ta farko ta shekaru goma sha bakwai ɗin nan na babban girbin waɗanda zasu zama masu bi na gaskiya.

Waɗannan ne waɗansu daga cikin kwanakin dake nuna cewa Allah ya tsara yadda zai ɓullo da shirin ceton duniya.

**Allah yayi amfani da Haikali domin ya nuna wata gaskiya ta ruhaniya**

Dole ne mu tuna cewa wani lokaci, Littafi Mai-Tsarki yakan yi amfani da wani abu da ya faru a tarihi domin ya nuna fushin Allah ko kuma jinƙansa. A misali, Littafi Mai-Tsarki ya bayyana hukumcin Allah a bisan duniya a zamanin Nuhu. Yayi amfani da ruwa domin ya hallaka mutum. Sai dai kuma, a 1 Bitrus 3:20, yayinda Allah yake magana akan wannan ruwan, ya nuna cewa akwai rayuka takwas da ruwan ya ceta. Haka kuma, Isra'ilawa sun ratsa ta cikin Jan teku lafiya, wannan yana nuna ceto. Sai dai kuma, sojojin Masarawa sun hallaka a cikin Jan teku, wannan na nuna hukumcin Allah a bisan miyagu. Ta haka, Allah yana nuna fushinsa da jinƙansa a cikin faruwar abu ɗaya.

Haka kuma, Allah yayi amfani da shahararren haikalin da Sulemanu ya gina domin ya nuna hukumcin Allah ya kuma nuna cetonsa. Wannan haikalin yana kama da haikalin dake Shilor, wanda yake nuna ginuwar mulkin Allah a zamanin Ikklisiya. Sai dai, daga baya Allah ya hallaka haikalin da ke a Shiloh da kuma haikalin da Sulemanu ya gina sabili da muguntar Isra'ila da Yahuda. Haka kuma a zamanin nan namu, Allah ya kawo hukumcinsa a bisan Ikklisiyoyin zamaninmu. Haikalin ya zama kwatancin Ikklisiyoyin zamanin mu. A yau, ba ko Ikklisiya ɗaya da ke cikin shirin Allah

na ceto. Haikali, wanda yake kwatanci dukan zamanin Ikklisiya ya rigaya ya kawu. Ba wani dutsen da aka bari a bisan wani (Matiyu 24:1-3).

Amma, Allah yayi amfani da haikalin Sulemanu domin ya yi kwatancin kyakkyawan shirin ceton Allah wanda ke faruwa a yau. Yayi wannan a cikin Littafi Mai-Tsarki yayinda yake bayyana ƙaddamar da haikalin. Dukan abubuwan da suke dangantaka da ƙaddamar da haikalin sun faru ne a wata na bakwai na kalandar Littafi Mai-Tsarki (1 Sarakuna 8:2). Littafi Mai-Tsarki ya ambaci wata na bakwai a matsayin ƙarshen shekara (Fitowa 23:16; 34:22). Idan aka bi tarihin duniya, a zamanin nan namu ne muke a ƙarshen shekara,[6] Sabili da haka, ya kamata mu gane cewa dukan abubuwan da suka faru a ƙaddamar da haikalin Sulemanu, suna tsira yatsa ne ga abubuwa na Bishara dake faruwa a zamanin nan namu, zamanin girbi na ƙarshe.

**Abubuwan da suka shafi haikali sun bada sanarwar muhimman lokatai**

Game da ƙaddamar da haikalin Sulemanu, Allah yayi amfani da wata hanya mai ban sha'awa domin ya nuna cewa ƙarshen duniya zai zo kwana ɗaya kafin ranar da muke sa zuciya zai faru. Ta wurin yin haka, Allah yana nuna mana daidai lokacin da duniya zata ƙare. Kafin mu iya fahimtar wannan, dole ne sai mun fara lura da yadda Allah yayi amfani da kalmomin nan 'rana ta ƙarshe.'

Yayinda muke binciken waɗannan kalmomin 'rana ta ƙarshe', zamu ga cewa a wurare takwas ne kaɗai aka ambaci waɗannan kalmomin a cikin Littafi Mai-Tsarki. Huɗu daga cikin waɗannan wuraren suna cikin Yahaya sura shida, inda Allah yake magana akan ba dukan masu bi na gaskiya sababbin jikuna a rana ta ƙarshe (Yahaya 6:39,40,44,54). Haka kuma a Yahaya 11:24, an yi amfani da waɗannan kalmomin 'rana ta ƙarshe'. A wurin, mun karanta cewa Marta na tsaye a bakin kabarin ɗan'uwanta da ya mutu, watau Li'azaru, tayi wannan furuci bisa ga jagorancin Ruhu Mai-Tsarki:

> ...Na sani zai tashi a tashin matattu a ranar ƙarshe.

> **An sake ambaton wannan a Yahaya 12:48 inda Kristi ke cewa: Wanda ya ƙi ni, bai kuma karɓi maganata ba, yana da mai hukumta shi, maganar da na faɗa, ita za ta hukunta shi a ranar ƙarshe.**

Sauran wurare biyun da aka yi amfani da waɗannan kalmomin suna da muhimmanci in an dangantasu da idin bukkoki. An ambaci wannan a Yahaya 7:37 da Nehemiya 8:18.

---

6.Abu ne mai muhimmanci da Allah ya yi Magana a kan ɗaukar Anuhu zuwa sama yana da shekaru 365, ba tare da ya ga mutuwa ba. (Farawa 5:23-24). Babu shakka ba kawai wannan misalin na fyaucewa ta farko ya faru da mai bi na gaskiya a shekarar da tayi daidai da kwanakin da ke cikin shekara ɗaya (kwanaki 365), na tarihin duniya ba.

Idin bukkoki na faruwa a lokaci ɗaya da idin tattarawa. Hakika waɗannan idodin na da dangantaka da ƙarshen duniya. Sabili da haka, baya ganin cewa Allah yayi amfani da waɗannan kalmomin 'rana ta ƙarshe' yayinda yake magana akan idin bukkoki bai zamar mana abin mamaki ba. Shi ya sa, ya kamata rana ta ƙarshe ta idin bukkoki ta nuna mana ranar da duniya zata ƙare.

A cikin kalandar bukukuwan Littafi Mai-Tsarki, waɗannan idodin da suke tafiya tare, idin bukkoki da idin tattarawa, akan yi su har kwana bakwai, faro daga 15 ga wata na bakwai. Littafi Mai-Tsarki ya kira ranar dake biye da wannan watau rana ta bakwai ɗin 'ranar taruwa' (Firistoci 23:36) da kuma 'asabaci' (Firistoci 23:39). Ta haka, idin bukkoki yana ƙunshe da kwana takwas faro daga ran 15 ga wata na bakwai zuwa ranar 22, kuma wannan ranar ta ƙarshe, akan kiyayeta kamar asabaci.

Sai dai kuma, shirin Allah ne ya nuna mana cewa idan muka danganta waɗannan kwanakin da ƙarshen duniya, ya kamata a gane cewa kwana na takwas ɗin nan yana matsayin kwanaki biyu ne ta yarda kwana na takwas ɗin nan zai ƙunshi rana ta 23 ga watan bakwai na kalandar Littafi Mai-Tsarki.

Allah ne da kansa ya tsara wannan a cikin sadarwar da muka samu a cikin Littafi Mai-Tsarki dangane da ƙaddamar da haikalin Sulemanu, wanda muna ganin yayi kama sosai da abubuwan dake faruwa a ƙarshen duniya. A cikin Tarihi ta biyu, Allah ya bayyana yadda aka ƙaddamar da haikalin Sulemanu. Abubuwan da aka yi sun haɗa da:

1. Abin ya faru a wata na bakwai (2 Tarihi 7:10)

2. Keɓe bagadin ya ɗauki kwana bakwai (2 Tarihi 7:9)

3. Daga nan sai suka kiyaye idin bukkoki (idin Littafi Mai-Tsarki) kwana bakwai (2 Tarihi 7:8-9). Watau kwanaki goma sha huɗu sun wuce ke nan (1 Sarakuna 8:65).

4. Kwana na takwas ya biyo kwanakin idin nan bakwai, a cikinsa kuma aka yi taro (2 Tarihi 7:8-9)

Ya kamata a kiyaye wannan rana ta takwas ɗin a matsayin ranar Asabaci (Firistoci 23:39), inda ba za'a yi wani aiki ba, kuma za'a ƙayyade irin tafiyar da mutum zai yi. Bisa ga Ayyukan Manzanni 1:12, tazarar dake tsakanin dutsen Zaitun da Urushalima, wanda bai kai rabin mil ba, shine tazarar da aka yardar wa mutum yayi tafiya a ranar Asabaci. Abin sha'awa anan shine mun karanta a cikin 1 Sarakuna 8:66 cewa:

> **A rana ta takwas ya sallami jama'ar, su kuwa suka yabi sarki. Sa'an nan suka kama hanyar gidajensu suna murna, suna farin ciki saboda**

**dukan alherin da Ubangiji ya yi wa bawansa Dawuda, da jama'arsa, Isra'ilawa.**

Rana ta Takwas, 21 ga Oktoba 2011

Kamar yadda muka gani, ya kamata wannan rana ta takwas ɗin ta zama ran 22 ga watan bakwai, kuma an kiyaye wannan ranar a matsayin Asabaci. Mutane sun zo daga ko'ina a cikin ƙasar Isra'ila (1 Sarakuna 8:65). Ta yaya za'a sa su suyi tafiya mai nisa a ranar da aka keɓe a matsayin Asabaci? Allah ya warware wannan matsala ta wurin nuna cewa rana ta takwas ɗin nan zata ci gaba har rana ta gaba. Wannan ƙarin rana ta gaban ita ce ranar 23 ga wata na bakwai. Mun karanta a cikin 2 Tarihi 7:10 cewa:

**A ranar ashirin da uku ga watan bakwai, sai sarki ya sallami jama'a su koma gidajensu, suna ta murna da farin ciki a zuciyarsu saboda alherin da Ubangiji ya nuna wa Dawuda, da Sulemanu, da kuma jama'arsa Isra'ila.**

Ka lura da kamar waɗannan kalmomin da ayar dake cikin 1 Sarakuna 8:66 (wadda muka karanta a baya). Ka tuna da cewa 1 Sarakuna na magana ne a kan kwana na takwas, wanda shine rana ta 22 ga wata, yayinda 2 Tarihi 7:10 na magana ne akan rana ta 23 ga wata.

Wannan bayanin dake nuna cewa ƙaddamar da haikalin da kuma kiyaye idin bukkukokin (idin Littafi Mai-Tsarki), suna da mawafuka da cikar shirin Allah na hukumta duniya. Wannan na nufin cewa ya kamata a ɗauki 2011 kwana na takwas na idin bukkoki (idin Littafi Mai-Tsaki), a matsayin kwana biyu. Yayinda kwana na takwas (22 ga watan bakwai), shine 20 ga Oktoba, ya kamata a kiyaye wannan ranar kamar yadda suka yi a 2 Tarihi 7:10, a rana ta 23 ga wata na bakwai, wadda ita ce ranar 21 ga watan Oktoba 2011. Shi yasa muka gane cewa 21 ga Oktoba 2011 ita ce rana ta ƙarshe da kasancewar duniya.

Mu sake waiwayar idin bukkoki

Idan muka bincike ƙaddamar da haikalin Sulemanu, zamu gane cewa bikin ya ƙunshi idin bukkoki. Mu kuma gane cewa wannan ya taimaka mana gane lokacin da duniya zata ƙare. Amma mene ne yasa ake kiransa idin bukkoki?

Mun gane cewa kalmar Helenancin da aka juya 'bukka' dangane da wannan idin, ita ce kalmar nan babban tanti, ko rumfa. Haka kuma zamu iya gane cewa wannan kalmar tana da mawafuka da girgije da kuma wutar dake rufe alfarwar har na shekarun nan 40 da 'Ya'yan Isra'ila suka yi suna yawo a jeji a hanyarsu daga Masar zuwa ƙasar Kan'ana. Haka kuma, zamu gane cewa girgijen da kuma wutar suna madadin shari'ar Allah ne, ta haka, bukkar tana wakiltar shari'ar Allah. Sabili da haka, idin bukkoki, idi ne na dokar Allah ko kuma Littafi Mai-Tsarki. Idin bukkoki (idin Littafi Mai-

Tsarki), yana nanata ɗaukakar Allah ne kamar yadda ɗaukakar littafin shari'ar Allah, watau Littafi Mai-Tsarki yake.

Wani nassi na Littafi Mai-Tsarki da yake taimaka mana fahimtar wannan kalmar shine Ishaya 4:5-6. A wurin mun karanta cewa:

Sa'an nan akan Dutsen Sihiyona, da akan dukan waɗanda suka tattaru a can, Ubangiji zai aika da girgije da rana, hayaƙi da hasken harshen wuta kuma da dare. Darajar Ubangiji za ta rufe, ta kuma kiyaye birnin duka. Ɗaukakarsa za ta inuwantar da birnin daga zafin rana ta sa ya zama lafiyayyen wurin da aka kare daga ruwan sama da hadari.

Waɗannan ayoyin suna koyar da abubuwa kamar haka:

1. 'A kan Dutsen Zaitun'. Wannan na magana ne akan dukan mulkin Allah, wanda muke zama magadansa lokacin da muka sami ceto.

2. 'Dukan waɗanda suka tattaru a can' Wannan kalmar ɗayantaka ce wadda ke nuni akan babban taro wanda ya ƙunshi dukan cetattu.

3. 'Girgije da rana, hayaƙi da hasken harshen wuta kuma da dare' Wannan na magana ne akan shari'ar Allah, watau Littafi Mai-Tsarki, wanda ke nunawa mutane hanya.

4. 'Ɗaukakarsa zata inuwanta' wannan yana nufin ɗaukakar mulkin Allah wanda girgije ne da rana, da dare kuma wuta a matsayin marfi.

5. Za ta inuwantar da birnin daga zafin rana ta sa ya zama lafiyayyen wurin da aka kare daga ruwan sama da hadiri' Girgijen da wutar, watau, Maganar Allah, marfi ne wanda ke rufe yana kuma samar da mafaka daga fushin Allah, wanda aka kwatanta da ruwan sama da kuma hadari.

Mun koya a baya cewa girgijen da wutar suna magana ne akan Maganar Allah. Zamu iya ganin wannan idan muka yi la'akari da cewar Littafi Mai-Tsarki ya jaddada cewa girgijen da wutar suna yiwa 'Ya'yan Isra'ila jagora shekaru arba'in ɗin da suka yi a jeji. A misali, mun karanta a cikin Littafin Kidaya 9:21-23 cewa:

> Wani lokaci girgijen yakan zauna a bisa alfarwar daga maraice zuwa safiya ne kawai, sa'an nan ya tashi, su kuma sai su tashi. Amma idan girgijen ya yini, ya kwana, sa'an nan ya tashi, su kuma sai su tashi. Ko kwana biyu ne girgijen yayi, yana zaune a bisa alfarwar ko wata guda, ko fiye, sai Isra'ilawa su yi ta zamansu a zangon, ba za su tashi ba. Amma in ya tashi, su kuma sai su tashi. Da umarnin Ubangiji suke sauka, da umurninsa kuma suke tashi, suna bin faɗarsa, yadda ya umarci Musa.

A cikin Littafin Lissafi 9:15-23, Allah ya danganta girgije da rana da kuma wuta da dare da umurnin Allah. Kuma umurnin Allah shine Littafi Mai-Tsarki.

Dole ne mu gane cewa idan bamu da ceto, shari'ar Allah zata sa fushin Allah ya faɗa a bisanmu. Amma idan muna cikin zaɓaɓɓu na Allah, (kuma zamu iya sani ko muna ciki ko babu, idan mun karɓi sabon ruhunmu), to bamu ƙarƙashin hukuncin hallaka ta har abada wadda ke zuwa sakamakon zunubi. Watau, shari'ar ba zata iya kashe mu ba kuma. A maimakon haka, shari'ar ta zamo tabbacin cewa Allah ya bamu rai na har abada tabbatacce a cikin Kristi. Shari'ar Allah ta ɓoye mu daga fushin Allah. Kuma shari'ar Allah, watau Littafi Mai-Tsarki na yi mana jagora, yana nuna mana yadda zamu yi rayuwa wadda zata ɗaukaka Allah.

Ta haka muka koyi cewa idin bukkoki yana nuni ne ga Littafi Mai-Tsarki inda Allah ya bayyana babbar ɗaukakarsa. Sabili da haka, ya fi zama daidai a kira 'idin bukkoki' 'idin Littafi Mai-Tsarki'. Ana kiyaye idin Littafi Mai-Tsarki daidai lokacin da ake kiyaye idin tattarawa. Akan yi idin tattarawa ne daidai lokacin da ake yin girbi na ƙarshe na shekara. Ta fannin ruhaniya, wannan na nuna cewa idin Littafi Mai-Tsarki yana ɗaukaka Littafi Mai-Tsarki. Wannan maida hankali ga ɗaukakar Littafi Mai-Tsarkin ya ƙara fitowa fili yayinda Allah yake kawo babban girbi na mutane waɗanda suke samun ceto a ƙarshen duniya.

An yi anabcin wannan babban tattarawas a cikin Romawa 9:28. A wurin, Littafi Mai-Tsarki ya ce:

> **Domin Ubangiji zai zartas da hukumcinsa a duniya, ya gama shi tashi ɗaya.**

Wannan na magana ne akan gajartar lokacin da muke ciki, wanda a nan gaba zamu koya daga cikin Littafi Mai-Tsarki cewa ɗan gajeren lokacin nan shine shekaru 17 na ƙarshe a tarihin duniya. Mabuɗin muhimmancin waɗannan shekaru 17 ɗin shine Kalmar nan Maɗaukakiya ta Allah, wadda, ta wurinta Allah yake ceton ɗinbin mutane waɗanda ba mai iya ƙirgawa a yau (Wahayin Yahaya 7:9). Shelar Bishara ga duniya ta ƙarshe wadda ke faruwa yau ba zata yi tuntuɓe ko rauni ba. Zata ci gaba ba tare da wani aibi ba har ta kai ga ƙarshenta, a cikin ɗan ƙanƙanen lokaci, Kristi zai komo ya fyauce masu bi na gaskiya, zaɓaɓɓu, a ko'ina cikin duniya zuwa gareshi a cikin sabuwar sama da sabuwar duniya.

## Sura ta 4.
## Mun fara binciken mu na tsarin lokacin ƙarshe.

Yanzu zamu jera gaskiyar da muka samu daga Littafi Mai-Tsarki wadda ke kaimu ga fahimtar jeren lokacin ƙarshe na tarihi.

Cikin shekaru 2,000 da suka wuce, lokacin da cikakken Littafi Mai-Tsarki ya ke a hannu, masu bi na gaskiya sun himmatu wajen binciken Littafi Mai-Tsarki domin gano abin da zai faru da duniya a nan gaba, da kuma lokacin da waɗannan abubuwan zasu faru. Dukansu suna sane da gaskiya guda ɗaya, wannan gaskiyar kuwa ita ce, lokaci na zuwa da tarihin wannan duniya zai kai ga ƙarshe. Wannan kuma zai faru ne daidai da lokacin da Yesu zai dawo a matsayin Mai shari'ar adalci a bisa duniya, da dukan fyaucewar masu bi na gaskiya zuwa sabuwar sama da sabuwar duniya, inda zasu yi mulki tare da Kristi har abada.

Sai dai kuma, kafin lokacin nan, za'a shiga wani lokaci na wani babban tsanani. An yi ta kuskuren ɗaukar wannan lokacin ya zama wani lokaci da za'a tsanantawa masu bada gaskiya ga Kristi. Gaskiyar dai ita ce, wannan lokaci ne da ba za'a iya fahimtarsa ba sai ta fannin ruhaniya.

Anyi ta binciken surorin Littafi Mai-Tsarki kamar su Matiyu 24 da Markus 13 domin akwai alamun cewa waɗannan surorin sun yi magana sosai akan tsananin dake zuwa kafin komowar Kristi. Gaskiya ne a cikin waɗannan surorin Allah ya bamu ɗan hasken da zai taimakemu mu fara kafa harsashin da ya danganta abubuwan da suka wuce a cikin Littafi Mai-Tsarki da kuma ƙarshen tarihi. Wata alamar tana cikin Markus 13:28, inda Allah ke cewa:

> **Ku yi koyi da itacen ɓaure. Da zarar rassansa sun fara sakuwa, suna toho, kun san damina ta yi kusa ke nan.**

Ba'a fara fahimtar wannan ayar ba sai wajen shekaru 60 da suka wuce, a 14 ga Mayu 1948. A wannan lokacin ne itacen ɓauren Littafi Mai-Tsarki, ƙasar Isra'ila, ta zamo ƙasa mai zaman kanta a cikin ƙasashen duniya. Wannan ya zama kamar wata mu'ujiza domin cikin dukan lokacin nan, tun daga shekara ta 70 lokacin da Romawa suka lalata Urshalima haɗe da haikalin, Isra'ila bata ƙara zama ƙasa mai cin gashin kanta ba. Sai dai, kamar a mafarki, ranar 14 ga watan Mayu 1948, Isra'ila ta sake zama ƙasa mai zaman kanta.

Nan take, Krista da dama suka danganta wannan abin da ya faru da anabcin nan na itacen ɓaure wanda ke cikin Markus 13:28. Sun iya ganewa cewa Allah ya kwatanta ƙasar Isra'ila da itacen ɓaure da kuma tohon ɓauren wanda shine Isra'ila ta sake zama ƙasa.[7]

---

7.Misali, ana kwatanta Isra'ila da itacen ɓaure da Kristi ya la'anta, yadda ba zai sake bada 'ya'ya ba (Markus 11:12-21).

Domin wannan ayar ta nanata, idan itacen ɓauren ya fara toho, dukan abubuwan da aka ambata a Matiyu 24 da Markus 13, zasu faru, dole ne mu gane cewa Allah ya bada wata alama dake nuna cewa ƙarshen duniya ya kusa.  Wannan ya faru ne domin in an bincike Matiyu 24 da Markus 13 na nuna cewa waɗannan abubuwan suna da dangantaka da babban tsananin (Matiyu 24:21), wanda ke biye da komowar Kristi (Matiyu 24:29-31).

Wata alamar da Allah ya bayar kuma tana samuwa a cikin Wahayin Yahaya 7:9-14. A wurin, Allah yayi magana akan ɗinbin taron mutane waɗanda ba mai iya ƙirgawa, waɗanda zasu fito daga cikin babban tsananin. Haka kuma, a cikin Luka 21:22, nassin da shima yana magana ne akan babban tsananin, Allah yayi magana akan wannan tsananin a matsayin lokaci na ɗaukar fansa. Hukumcin da Allah zai zuba a kan miyagu, lokaci ne na ɗaukar fansa. A lokacin babban tsananin, Allah ya fara shirya mutanen duniya da kuma Ikklisiyoyi domin cikar hukumcin Allah.

Aya ta gaba dake taimaka mana ita ce Matiyu 24:22 inda muka karanta cewa:

> **Ba don an taƙaice kwanakin nan ba, da ba ɗan adam ɗin da zai tsira. Amma sabili da zaɓaɓɓun nan, za a taƙaita kwanakin.**

Bisa ga alama wannan ayar tana cewa wannan lokacin babban tsananin, lokaci ne da Allah zai fara ɗaukar fansa a bisan 'yan adam. Sai dai kuma, sabili da zaɓaɓɓu na Allah da yawa, waɗanda Allah ya zaɓa domin su sami ceto (Afisawa 1:3-6), ba su rigaya sun sami ceto ba, an gajarta wannan lokacin na tsanani. Ma'ana, wannan lokaci na babban tsananin nan yana da dangantaka da shirin hukumcin Allah, sai dai kuma, wannan lokacin yana da dangantaka da wani babban shiri na ceto. Ta yaya zamu iya haɗa waɗannan ra'ayoyin?

Daga cikin binciken yadda abubuwa suka riƙa tafiya a cikin tarihi da kuma abin da Kolossiyawa 2:16-17 ke koyaswa, mun gane cewa dukan waɗannan na haɗe ne da waɗansu ranakun bukukuwa. Alal misali, shekarar jubili na ƙarfafa 'yanci (ceto) ga dukan duniya.  gaskiyar ita ce, da alamar dukan shaidun dake cikin Littafi Mai-Tsarki na nunin cewa an haifi Yesu, wanda shine tushen jubili, a cikin shekara ta 7 B.C., a ranar kafara, a lokacin da ake busa ƙahon jubili (Firistoci 25:9).[8]

Haka kuma, mun koyi cewa an shaida Yesu Ɗan rago na Allah ranar 26 ga Satumba A.D. 29, wanda bisa ga kalandar Littafi Mai-Tsarki, wata na bakwai ne, wanda shi ma ake kira ranar jubili (Littafin Ƙidaya 29:1). Domin Kristi, jubili, yazo an kuma sanar da shi, an kafa ginshiƙin shelar bishara ga dukan duniya. Mako bakwai bayan lahadin da Yesu ya tashi daga matattu, an

8.Waɗansu lokatai ana fassara Kalmar nan ta Ibraniyanci "teruah" a matsayin ƙahonni". Amma a cikin Littafin Faristoci 25:9, dangane da ranar fansa, mun ga an fassara wannan Kalmar "teruah" daidai a matsayin ranar "jubili". Saboda haka zai fi dacewa a fassara  "ranar busa ƙahonni" da "ranar Jubili".

zubo da Ruhu Mai-Tsarki wanda ya zama farkon shelar Bishara zuwa ga duniya duka.

Bisa ga alama, idan akwai wani ɓullowar babban ceto, ba wuya wannan zai sami wata dangantaka da shekarar jubili. Sabili da haka, daga cikin shekarun da ke biye da 1948, wacce shekara ce zata zama shekarar jubili? Tsakanin shekarar jubili zuwa wata shekarar jubilin shekaru 50 ne. Hakika daga 1948, shekara ta 1994 ce zata zama shekara ta gaba. Shekaru 2,000 ne tsakanin shekarar jubili ta 7 B.C. lokacin da aka haifi Kristi, wanda kuma shine tushen jubili.

Hakika jubili na da dangantaka da shirin ceto na Allah. Amma Littafi Mai-Tsarki ya tabbatas mana cewa shekarar jubili na tsakiyar babban tsananin, wanda kuma ya zama lokaci ne na shiri domin hukumcin Allah na ƙarshe. Ta yaya waɗannan abubuwan da suka saɓawa juna zasu faru tare har su kuma sami wata dangantaka da 1994?

Anabcin dake cikin Daniyel 8 zai zama da taimako ƙwarai. A Matiyu 24, inda muka ji game da babban tsananin, Allah ya umurcemu da mu nemi ƙarin sanarwa daga cikin littafin Daniyel. Matiyu 24:15-16 na cewa:

> **Don haka sa'ad da kuka ga mummunan aikin saɓo mai banƙyama wanda Annabi Daniyel ya faɗa, an tsai da shi a wuri Mai-Tsarki (mai karatu fa ya fahimta), to sai, waɗanda ke ƙasar Yahudiya su gudu su shiga duwatsu.**

A Daniyel sura 8, Allah yayi magana akan wani lokaci mai kwanaki 2,300 wanda wani sarki zai yi mulki. Zai sa a kawas da hadayu na rana-rana a kuma musanyasu da abin ƙyama da kuma ayyukan saɓo a cikin haikalin (Daniyel 8:12-14). Ta fuskar ruhaniya, wannan na nufin za'a musanya Bishara ta gaskiya da bishara ta shaiɗan. Abu mai muhimmanci game da waɗannan kwanakin 2,300 shine, a cikin Daniyel 8:17, Allah ya ce: **'wannan wahayi yana a kan lokoci na ƙarshe ne.'**

Mun riga mun gani cewa shekara ta 1994 shekara ce ta jubili wadda ta mai da hankali akan shelar Bishara ga duniya duka. Shin ko wannan shekarar ita ce ƙarshen kwanaki 2,300 da aka yi magana akai a cikin Daniyel sura 8, lokacin da za'a aikata wannan babban abin saɓon?

Idan haka ne, idan kuma kwana 2,300 kafin 1994 ya zama shekara ta 1988, ko 1988 zai zama shekarar da babban tsananin ya fara? Wannan yana iya nufin cewa, kashi na farko na babban tsananin, kusan ba wanda ya sami ceto. Sai kuma wannan na iya nufin cewa a shashe na ƙarshe na babban tsananin, ɗinbin mutane, wanda ba mai iya ƙirgawa, zasu sami ceto (Wahayin Yahaya 7:9-14).

Yayinda muke tattauna wannan, ya kamata mu lura da cewa a cikin Ayyukan Manzanni 7:11, an yi amfani da kalmomin nan 'matsananciyar wahala' yayinda ake magana kan Yakubu da dukan 'ya'yan Isra'ila lokacin da suka bar ƙasar Kan'ana zuwa Masar domin su guje wa shekaru bakwai na yunwa. Mun sani cewa wannan mummunan abu ne ga Yakubu. Kalmomin

nan ‘matsananciyar wahala’ daidai suke da kalmomin Helinancin da aka juya zuwa ‘babban tsanani’ a Matiyu 24:21.[9]

Yana da muhimmanci mu gane cewa Yakubu yaje Masar a lokacin wannan babban tsananin a cikin shekara ta 1877 B.C. Shekarar da muke dubawa a cikin Matiyu 24:21 dangance da babban tsananin, shekarar jubili ta 1994 ce. Tsakanin shekarun nan 1877 da 1994, shekaru 3,870 ne. 1,877+1,994-1= 3,870. (Tun da ba shekara ta 0, idan muna bin kalandar Tsohon Alkawali zuwa Sabon Alkawali, dole ne mu cire shekara ɗaya). Idan kuma ka duba, 3,870 yana daidai da 3X1,290.

Bisa ga alama wannan lambar 1,290 tana da muhimmanci, domin akwai wani lokacin da aka kori Isra’ilawa daga ƙasar alkawali. Mutanen Babila sun lalata Urushalima da kuma haikalin kwata-kwata. Wannan ya faru ne a shekara ta 587 B.C.; lokacin da fushin Allah na shekara 70 ya sabko a bisa Yahuda. Waɗannan shekaru 70 sun fara ne a cikin shekara ta 609 B.C, suka kuma ƙare a shekara ta 539 B.C., lokacin da Medis da Persiya suka ci birnin Babila. Wannan mugun abin lalata Urushalima da Haikalin, ya faru ne a cikin shekara ta 587 B.C. Abu ne mai muhimmanci ganin cewa lambar nan 1,290 ta haɗa waɗannan shekaru da muke nazari akai (1877 B.C., 587 B.C da 1994 A.D.)

1877 B.C. zuwa 587 B.C shekaru 1,290 ne

587 B.C. zuwa 1994-1 shekaru 2,580 ne wanda yayi daidai da 2X1,290

1877 B.C zuwa 1994-1 shekaru 3,870 ne wanda yayi daidai da 3X1,290

Littafi Mai-Tsarki yayi amfani da wannan lamba dangane da abubuwa na ruhaniya da suka faru a waɗanan lokatai guda uku. Littafi Mai-Tsarki ya jaddada amfanin lambar nan 1,290 a cikin Daniyel 12:11 inda ya ce:

**Tun daga lokacin da za a hana miƙa hadayar ƙonawa ta yau da kullum, a kafa abin banƙyama wanda ke lalatarwa, za a yi kwana dubu da ɗari biyu da tasa’in.**

---

9.Ana samun Kalaman nan “babban tsanani sau huɗu kawai a cikin Littafi Mai-Tsarki. Ana samunsu a cikin Matta 24:21 da Ruya Ta Yohanna 7:14, da muka riga muka bincike, da kuma Ayyukan Manzanni 7:11 da Ruya Ta Yohanna 2:22. A cikin Luka 21:23 Allah ya zaɓi kalaman Helenanci da aka fassara a matsayin “wahalar gaske” yayinda ake Magana a kan zamani ɗaya.

Dole ne mu tuna cewa wani lokaci, Allah ya kan yi amfani da kwana ɗaya domin ya wakilci shekara guda. A misali, a cikin Littafin Kidaya 14:34, Allah ya nuna cewa Isra'ilawa zasu kasance a cikin jeji har shekara 40, daidai da kwanaki 40 ɗin da magewayan suka yi suna zagaya ƙasar Kan'ana. Sabili da haka, mun sani cewa kwana 1,290 da aka yi magana akai a cikin Daniyel 12:11 na matsayin shekaru 1,290 ne. Allah yana danganta mugun lokacin nan da ya zamar wa Yakubu dole ya fita daga ƙasar alkawali ya tafi Masar, da watsar da Yahuda, da kuma wani mugun abu da ya faru a cikin shekar jubili ta 1994. Wanne mugun abu ne wannan?

Mun sani cewa an yi amfani da ƙasar Kan'ana a cikin Littafi Mai-Tsarki domin a yi kwatancin mulkin Allah. Don haka, barin Kan'anan da Yakubu da iyalinsa suka yi, yana daidai da barin mulkin Allah. Haka kuma, kora daga Urushalima da kuma sanin cewa an lalata haikalin, yana daidai da watsar da mutum daga mulkin Allah. Amma menene ya zama kwantancin mulkin Allah a 1994? Mun sani cewa a dukan zamanin Ikklisiya, dukan majami'u suna wakiltar mulkin Allah domin sune wuraren da Allah ya kafa domin su wakilci mulkinsa. Sune masu lura da Littafi Mai-Tsarki, sune kuma ke da alhakin aikawa da Bishara zuwa kowane lungu na duniya.

Babban tsananin da ya faru a zamanin Yakubu (Ayyukan Manzanni 7:11-12) ya ƙunshi shekaru bakwai na yunwa, amma a wannan lokacin, yunwa mafi munin ta faru ne a shekaru biyu na ƙarshe, lokacin da ya zamar ma Yakubu dole ya bar ƙasar alkawali (1877 B.C.). Lokacin da aka urmurci Yakubu ya bar ƙasar Kan'ana, abin yana kama da an umurce shi da ya bar mulkin Allah ne. Ba abin da zai fi wannan zafi. Wannan na nufin an sadaukar da ƙasar alkawali, ƙasar Kan'ana, ga arna waɗanda ke cikin mulkin Shaiɗan kenan. Sabili da haka, wannan yana kama da an miƙa wa Shaiɗan sarautar mulkin Allah ke nan. Sabili da haka, shekaran nan ta 1877 B.C. ta zama muguwar shekara, shekara ta baƙinciki.

Haka kuma, shekarar da tafi kowace muni a cikin miyagun shekaru 70 na 'Ya'yan Isra'ila ita ce shekara ta 587 B.C., lokacin da aka lalata Urushalima da kuma haikalin, waɗanda suma suna wakiltar mulkin Allah ne. Bisa ga umurnin Allah, a wannan shekara, sarkin Babila wanda yake wakiltar Iblis, ya lalata haikalin da kuma Urushalima (Ishaya 14). Haka kuma, wannan ma ya nuna kamar mulkin Allah a nan duniya ya zo ga ƙarshe.

Waɗannan abubuwa guda biyu suna kwatancin abin da ya faru a shekarar jubili ta 1994. Ikklisiyoyi a ko'ina sun zama wakilai na mulkin Allah har na shekaru 1,955, kamar yadda ƙasar Kan'ana take a zamanin Yakubu, kamar kuma yadda Yahuda, ƙasar Isra'ila, Urushalima da haikalin suke a wancan zamanin.

Zamu gane cewa tun kafin 1994, Allah ya gama amfani da Ikklisiyoyi a matsayin wakilan mulkin Allah. Ta haka, shekarar nan ta jubili ta 1994 muguwar shekara ce ga Ikklisiyoyi. Allah ya ci gaba da ceton ɗinbin mutane a ko'ina a cikin duniya, sai dai kuma, Ikklisiyoyin sun kasance a ƙarƙashin mulkin Shaiɗan. Gaskiya ne cewa Allah ya gama yin amfani da Ikklisiyoyi su zama wakilan mulkin Allah har abada. Yanayin ya zama kamar yadda yake a

1877 B.C., lokacin da ƙasar Kan'ana ta koma ƙarƙashin mulkin arna, da kuma a shekara ta 587 B.C., lokacin da Yahuda ta koma ƙarƙashin mulkin sarkin Babila.

Shekaran nan ta 1877 B.C. ta raba mawuyacin lokacin da Yakubu ya shiga kashi biyu, kamar yadda 587 B.C. ta raba shekaru 70 na tsananin da Isra'ila suka shiga kashi biyu. Haka kuma, shekara ta 1994 ta raba babban tsananin zamanin mu kashi biyu, lokacin da ya fito fili cewa Allah ba zai ƙara yin amfani da Ikklisiyoyi su wakilci mulkin Allah ba har abada.

Tun da waɗannan zamanin tsanani na shekara bakwai da kuma shekara saba'in alamu ne na tsananin zamanin mu, muna sa zuciyar wannan tsananin na yanzu ma zai sami wata dangantaka da lamba bakwai. Mun rigaya mun gani cewa kashi na farko na wannan babban tsananin yayi daidai da kwanakin nan 2,300 na Daniyel sura 8. Domin wahalar da Yakubu ya fuskanta ta shekaru bakwai ce, kuma tsananin da Yahuda ta shiga ta ƙunshi shekaru 70, dole ne mu sa zaton tsawon lokacin wannan tsananin na yanzu zai ƙunshi lamba bakwai. Zai iya zama kwanaki 7,000 ko kila ma 7 x 12 x 100, wanda zai yi daidai da kwanaki 8,400. Ta fannin ruhaniya, lambar nan 100 na nuna 'kammalawa', lambar nan 12 kuma na nuna 'cikar abu.' A nan gaba, zamu ga cewa kwanakin tsananin nan, kwanaki 8,400 (shekaru 23), akwai kuma ƙarin sadarwa daga Littafi Mai-Tsarki da ya tabbatas da wannan. Abin sha'awan shine, kwanaki 8,400 ne ke cikin shekaru 23, kuma yawancin lokaci, lambar nan 23 tana da dangantaka da fushin Allah.

Haka kuma, nan ba zamu ga yadda dukan waɗannan lambobin shekaru 7, shekaru 70, da kwana 8,400 suka rabu biyu ba. Kamar yadda muka rigaya muka gani, an raba shekarun nan bakwai na tsananin Yakubu kashi biyu. Baƙincikin rabuwa da ƙasar Kan'ana ya faru ne a cikin shekaru biyu na farkon waɗannan shekarun bakwai (Farawa 45:6-8). Sabili da haka, kashi na farko, bakwai guda biyu ne, ko kuma kashi 28.6 cikin ɗari na dukan tsawon lokacin. Haka kuma, tsananin Yahuda ya fara a cikin shekara ta 609 B.C. lokacin da Sarki Josiah ya mutu, wannan tsananin kuma ya ci gaba har shekara ta 539 B.C. lokacin da Medes da Persia suka ci Babilawa da yaƙi. An kasa waɗannan shekaru 70 ɗin biyu, kashi na farko shekaru 22 ne. 22 yana daidai da kashi 31.4 bisa ɗari na shekaru 70.

Ka tuna cewa tsananin Yakubu da tsananin Yahuda wani abu ne da tsananin wannan zamanin ke kwaikwaya. Sabili da haka, zamu sa ran cewa tsananin nan na zamanin mu zai zo kusa da 28.6% ko kuma 31.4% na dukan tsawon lokacin tsananin. Hakika, kwana 2,300 27.4% ne na kwana 8,400. Zamu iya ganin yadda waɗannan suke tafiya tare da wajen kurkusan da 27.4% yayi da 28.6% da kuma 31.4%. A nan gaba, zamu ga wasu shaidu daga Littafi Mai-Tsarki dake nuna mana cewa kwanakin nan 2,300, wani kaso ne daga cikin kwanakin nan 8,400 na wannan babban tsananin.

Mun gane cewa kwana 8,400 ya ƙunshi lamba bakwai (7 x 12 x 100). Da alamar kuma an raba kwanakin kashi biyu, kashi na ɗaya shine 30% na tsawon lokacin. Kuma domin shekaru 23, wanda yawancin lokaci Littafi Mai-Tsarki ke dangantawa da fushin Allah, tsawonsu kwana 8,400 ne, wannan ya

sa muke ƙarfafa tunanin cewa tsawon lokacin babban tsananin kwana 8,400 ne.

Mun karanta a cikin 1 Bitrus 4:17 cewa:

> **Don lokaci ya yi da za'a fara shari'a ta kan jama'ar Allah, In kuwa ta kanmu za a fara, to me zai zama ƙarshen waɗanda ba su bi bisharar Allah ba?**

A wannan aya, Allah yana magana ne akan lokacin shiri na Allah domin kawo hukumci mai zuwa, kuma zai fara ne daga Ikklisiyoyi. Sabili da haka, tsawon lokacin nan na kwanaki 8,400 (shekaru 23) na iya zama wannan lokacin.

Ta haka, kwanakin nan 2,300 waɗanda suka yi daidai da babban tsananin nan sun kuma yi daidai da Wahayin Yahaya 8:1, inda Littafi Mai-Tsarki ke cewa:

> **Sa'adda Ɗan Ragon ya ɓamɓare hatimi na bakwai, aka yi shiru a sama kamar rabin sa'a.**

Lokacin nan na rabin sa'a, lokaci ne wanda ba mai samun ceto, ko ina a cikin duniya, da kuma cikin Ikklisiyoyi. Zamu iya sanin wannan domin mun karanta Luka 15:10:

> **Haka nake gaya maku, abin farinciki ne ga mala'ikun Allah in mai zunubi guda ya tuba.**

Idan mutane basu samun ceto, sama takan yi shiru domin babu murna a can. Ta haka muke gane cewa a ƙarshen zamanin Ikklisiya, akwai kwanaki 8,400 (shekaru 23) wanda yake farawa da kwanaki 2,300, inda ake shirya duniya, musamman ma Ikklisiyoyi domin ranar shari'a.

A misali, wannan shi ya sa a Wahayin Yahaya 13:7 da 8 muke karanta cewa dabban (Shaiɗan) wanda ya fito daga cikin teku (fushin Allah), wanda kuma yayi nasara bisa tsarkakan (ya kore su daga Ikklisiyoyi), ya kuma yi mulki a bisa duniya.

Sai dai kuma, kamar yadda muka rigaya muka gani, shekaran nan ta 1994, shekara ce ta jubili, lokacin da aka zubo da Ruhu Mai-Tsarki (Ezekiyel 39:25-29; Yowel 2:28-32), kuma lokacin ne ya kamata a fara watsa Bishara ko'ina cikin duniya. Zamu so mu yarda cewa da alama Allah zai sake yin amfani da Ikklisiyoyi. Sai dai kuma, muna koyon cewa majami'un da suke warwatse cikin duniya suna kama da haikalin, kuma Allah ya tabbatas mana cewa lokaci na zuwa wanda za'a lalata haikalin har ba wani dutsen da zai rage a bisan wani (Matiyu 24:1-3). Ba inda aka ce mana za'a sake gina haikalin da aka lalata a Matiyu 24, bayan ana tattaka shi. Watau, Allah ba zai sake yin amfani da Ikklisiya domin ya kai Bishara ga duniya ba.

Babban tsananin zai ci gaba har na kwana 8,400, wanda yayi daidai da shekaru 23. Wannan na nufin, faro daga 1994, shekarar jubili, Allah yayi amfani da wata hanya domin aikawa da Bishara zuwa ga duniya. Bai ƙara yin amfani da majami'u ba. Ko da yake shekara ta 1994 shekara ce da ke gabatar da sabon salon watsa Bishara ga duniya duka, amma ga Ikklisiyoyi, ta zama muguwar shekara. Wannan ya faru ne domin tun daga wannan lokacin, Ikklisiyoyi sun shiga zamanin babban tsanani na fushin Allah wanda zai ɗauki kwanaki 8,400.

## Ranar ƙarewar zamanin Ikklisiya

Kama daga farko zuwa yanzu, abin da muka koya na nuna mana cewa shekarar jubilin nan ta 1994 ita ce ƙarshen kwanakin nan 2,300, lokacin da ba wanda yake samun ceto a ko'ina cikin duniya. Wannan ya taimaka mana gane ƙarshen zamanin Ikklisiya, wanda dole ne yayi daidai da farkon shekarun nan 23 (kwana 8,400) na babban tsanani.

Kwanaki 2,300 sun fi shekaru shida tsawo kaɗan. Sabili da haka, ƙarshen zamanin Ikklisiya ya faru ne shekaru shida kafin shekara ta 1994. Sabili da haka, dole ne wannan ya faru a shekara ta 1988 ne.

Domin mu iya gane daidai ranar da zamanin Ikklisiya ya kai ga ƙarshe a shekara ta 1988, dole ne mu tuna cewa an danganta zamanin Ikklisiya da idin makonni wanda kuma ake kira ranar Pentakos. Ana kiyaye wannan ranar ne a ranar Lahadi ta bakwai bayan asabaci ta farko wadda ke zuwa bayan idin ƙetarewa. A ranar ne ake kawo nunar fari zuwa cikin haikali. Wannan na maida zuciyar girbi daga ko'ina cikin duniya, girbin masu bi na farko waɗanda ake kawowa kan mulkin Allah. Farkon zamanin Ikklisiya shine ranar Pentakos na shekara ta 33 A.D. Idan muka juya wannan ranar zuwa kalandar mu ta yanzu, wannan ranar zata zama ranar 22 ga Mayu A.D. 33.

A kowace shekara yayinda ranar Pentakos ta zagayo, tana nuna ci gaban shigo da nunar fari a kowace shekara. Sai dai kuma, a shekara ta 1988, shigo da nunar fari wanda ranar Pentakos ke nunawa, ya kai ga ƙarshe. Tun da ranar Pentakos ta 1988 ta faɗi kan ranar 22 ga watan Mayu, to rana ta ƙarshe ta zamanin Ikklisiya zata kasance ranar da ta zo kafin ranan nan ta 22 ga Mayu, watau ran 21 ga Mayu ke nan. Watau zamanin Ikklisiyar da ya fara ran 22 ga Watan Mayu shekara ta 33, ya ci gaba tun daga wannan shekarar har zuwa 1988, wanda yayi daidai da shekaru 1,955. Wannan ma wani nuni ne na yadda Allah ya tsara yadda abubuwa suke tafiya a tarihi.

Sabili da haka, 21 ga Mayu 1988 ne ranar da zamanin Ikklisiya ya zo ga ƙarshe, wanda kuma ya zama farkon babban tsanani. Ya kamata kwanakin nan 2,300 waɗanda suka zama kashi na farko na babban tsananin sun kai ga ƙarshe ranar 7 ga watan Satumba 1994. Wani abin sha'awa anan shine, bisa ga kalandar Littafi Mai-Tsarki, 7 ga Satumba 1994 ranar idin

jubili ce. Ka tuna da cewa kalmar nan jubili na da nasaba da shelar Bishara zuwa ga dukan duniya.

Biye da kwanakin nan 2,300, akwai kwanaki 6,100 (8,400 - 2,300 = 6,100) waɗanda suka rage na shekaru 23 (kwanaki 8,400) na babban tsanani. Sabili da haka, waɗannan kwanakin 6,100 zasu ƙare ne ranar 21 ga watan Mayu 2011.

Mun rigaya mun ga cewa ranar da duniya zata ƙare bisa ga abin da muka koya daga idin bukkoki (Idin Littafi Mai-Tsarki) shine 21 ga Oktoba 2011. Bayan babban tsananin, za'a yi waɗansu kwanaki 153 na ƙarshe, wanda a nan gaba zamu gani cewa sune ranar shari'a, lokacin da Allah ke kammala hukumcinsa bisa waɗanda basu da ceto.

Ta wurin jinƙan Allah, mun iya gane jeren kwanaki na tarihi har ya zuwa ƙarshen duniya wanda kuma mun samu ne daga cikin Littafi Mai-Tsarki. Yanzu zamu duba mu kuma ga cewa Littafi Mai-Tsarki ya bada shaidu akan rashin kuskuren wannan jeren kwanakin.

Wata doka mai muhimmanci wadda ta taimaka mana wajen cimma wannan na samuwa ne a cikin Kolossiyawa 2:16-17, inda Allah ke cewa:

> **Saboda haka, kada ku damu in wani ya zarge ku kan abin da kuke ci, ko, abin da kuke sha, ko kuwa kan rashin kiyayewar wani Idi, ko tsayawar wata, ko Asabar. Waɗannan kam, isharori kawai na abin da zai auku, amma Almasihu shine ainihinsu.**

A cikin waɗannan ayoyin masu wayar da kai, Allah ya nuna cewa lokatan da ake kiyaye bukukuwan da dokokin suka ƙayyade, suna nuni ne ga keɓaɓɓun lokatai na abubuwa masu zuwa. Sabili da haka, nan da nan sai muka gane abin da yasa aka giciye Yesu, Ɗan Rago na Allah, ranar 14 ga wata na fari (Nisan 14), na kalandar Littafi Mai-Tsarki, wadda rana ce ta idin ƙetarewa. Haka kuma, zamu iya gane dalilin da yasa aka zubo da Ruhu Mai-Tsarki aka kuma ƙaddamar da zamanin Ikklisiya wajen makoni bakwai da saukar Ruhu Mai-Tsarkin, a daidai ranar da Isra'ilawa ke bikin Idin Pentakos.

Wani muhimmin anabci dake cikin Littafi Mai-Tsarki wanda muka rigaya muka gani a baya shine Markus 13:28-19, inda Allah ke umurtarmu cewa:

> **Ku yi koyi da itacen ɓaure. Da zarar rassan sa sun fara sakuwa, suna toho, kun san damuna ta yi kusa ke nan. Haka kuma sa'ad da kuka ga waɗannan abubuwa na aukuwa, ku sani ya kusato, a bakin ƙofa ma yake.**

An yi ta kwatanta al'ummar Isra'ila da itacen ɓaure. Bayan kasancewarsu ba ƙasa ba 'yancin kai har na wajen shekaru 2,000, farat ɗaya sai ga Isra'ila ta sake zamowa ƙasa mai cin gashin kanta a cikin ƙasashen duniya. Masana Littafi Mai-Tsarki da yawa sun danganta wannan muhimman abin da ya faru da cikar wannan anabci na Markus 13. Tun da abin ya faru ran 14 ga watan Mayu 1948, waɗannan ayoyin suna koya mana cewa dukan

abubuwan dake rubuce a cikin Markus 13, suna kusa da faruwa a cikin shekarun dake biye da 1948.

Wata alama da zata taimaka mana gane jeren lokatan da zai kai ga ƙarshen duniya shine, shekara ta 1994, shekara ce ta jubili. A baya, mun koyi cewa an haifi Yesu, wanda shine tushen jubili, a shekara ta 7 B.C., wadda ita ma, shekara ce ta jubili. Ka tuna, jubili na nuni ne na cewar za'a yi shelar 'yanci (ceto) ga dukan duniya.

Idan aka bincike Markus 13, da ayoyin da suka yi tafiya tare da shi kamar su Matiyu 24, Luka 17 da Luka 21, zamu ga cewa waɗansu abubuwa kamar haka zasu faru a ƙarshen tarihin duniya:

1. Lokaci zai zo inda dukan Ikklisiyoyi a ko'ina cikin duniya, waɗanda aka kwatanta da haikalin Allah, zasu zo ga ƙarshe. **'Ba wani dutsen da za'a bari nan akan ɗan'uwansa.'** (Matiyu 24:2). Shaiɗan wanda ake kira **'Aikin saɓo mai ban ƙyama'** (Matiyu 24:15), zai rinjayesu.[10]

2. Wannan zai zama lokacin babban tsanani lokacin da za'a kori masu bi na gaskiya a kuma umurcesu da su fita daga cikin Ikklisiyoyi. Zai zama lokaci na saɓo a cikin Ikklisiyoyi ƙwarai, yayinda Shaiɗan ya shiga cikin mafiya yawansu yana aikata mu'ujuzai (Matiyu 24:24)

3. An kwatanta wannan zamanin tsananin da shekaru bakwai na abin da Yakubu ya fuskanta a cikin shekara ta 1877 B.C. inda Allah ya umurce shi da ya fita daga ƙasar alkawali ya koma Masar.

4. An kuma kwatanta shi da shekaru 70, daga 609 B.C. zuwa 539 B.C., inda Yahudawa suka fuskanci hukumcin Allah. Waɗannan shekarun 70 sune daga 609 B.C., lokacin da aka kashe sarki mai kirki na ƙarshe watau Josiah, har zuwa 539 B.C. lokacin da Medes da Persia suka ci Babila da yaƙi, suka kuma yardaswa Yahudawan dake bauta su koma Urushalima. A tsakiyar wannan mugun lokacin da Isra'ilawa suka fuskanta, a cikin shekara ta 587 B.C., Babilawa suka lalata Urshalima haɗe da haikalin da Sulemanu ya gina kwata-kwata.

5. Koda yake bai yi ƙarfi sosai ba, zamu iya ganin cewa an kwatanta shi da watanni bakwai ɗin da alfarwar tayi a Shiloh, lokacin da Filistiyawa suka ƙwace sanduƙin Ubangiji suka tafi da shi ƙasarsu. Wannan ya faru ne daga 1068 zuwa 1067 B.C.

---

10. Ana gayyatar ka, ka rubuto domin a aika maka kyautar littattafai *Karshen Zamanin Ikkilisiya* da kuma *Alkama da Zawan,* waɗanda suka yi bayani sosai dangane da ƙarshen zamanin Ikklisiya.

Sabili da haka, bisa ga alama lambar nan bakwai na taka rawar gani a cikin wannan babban tsananin da muka karanta akai cikin Matiyu 24.

Mun kuma koyi cewa ba wuya, lambar nan 23 na da wata dangantaka da babban tsananin. An yi ta amfani da wannan ayar a cikin Littafi Mai-Tsarki domin a nuna fushin Allah, kuma zamanin babban tsananin lokaci ne wanda Allah ke shirya Ikklisiyoyi da kuma duniya baki ɗaya domin fushin Allah, wanda zai bi bayan wannan lokacin. Lambobin nan 7 da 23 sun zama da muhimmanci idan muka duba cewa kwanakin nan 8,400 na daidai da shekaru 23. Lambar nan 8,400 na daidai da 7 x 12 x 100, ta haka, lambobin nan 7 da 23 duka sun sami shiga a cikin kwanakin nan 8,400, wanda yayi daidai da shekarun nan 23 wanda kuma shine lokacin babban tsananin.

Mun gane cewa waɗannan kwanakin 8,400 na lokacin tsananin ya kasu kashi biyu. Bisa ga abin da muka koya daga Wahayin Yahaya 8:1, a cikin kashi na farkon, ba wanda yake samun ceto a duniya. Mun gani cewa wannan kashin na farko yayi daidai da kwanaki 2,300 da ke rubuce a Daniyel 8:13-14.

Mun kuma gane cewa a sashe na biyu na babban tsananin, babban taron jama'a wanda ba mai iya ƙirgawa, zasu sami ceto daga ko'ina cikin duniya (Wahayin Yahaya 7:9-14). Wannan zai faru ne ba daga cikin Ikklisiya ba domin Ikklisiya tana ƙarƙashin fushin Allah har a wannan lokacin.

Mun kuma koyi cewa idin bukkoki (idin Littafi Mai-Tsarki) wanda alama ce ta wani abu mai zuwa, ya zama alama ce ta rana ta ƙarshe. Domin dole ne rana ta ƙarshen ta yi daidai da ƙarshen duniya, dole ne lokacin da Littafi Mai-Tsarki ya tsayar na idin bukkoki yayi daidai da ƙarshen duniya.

Akwai wata magana mai wuya da bai kamata mu manta da ita ba, watau abin da Markus 13:24-26 ya faɗa, inda yake cewa:

> **Amma a lokacin nan, wato bayan tsabar wahalan nan, za'a duhunta rana, wata kuma ba zai yi haske ba. Taurari za su riƙa faɗowa daga sararin sama, za'a kuma girgiza manyan abubuwa dake sararin sama. A sa'annan nan ne za'a ga Ɗan Mutum na zuwa cikin gajimare, da ikon mai girma da ɗaukaka.**

Dole ne mu ƙara koyan wani abu game da wannan lokacin.

Idan muka taƙaita dukan abubuwan da muka gani zuwa yanzu, zamu iya cewa yadda abubuwa zasu tafi zuwa ƙarshen duniya zai zama kamar haka.

1. Zamanin Ikklisiya wanda ya fara a shekara ta 33, zai ƙare wajen shekara ta 1948, lokacin da Isra'ila zata sake zama ƙasa mai zaman kanta a duniya.

# Sura 5.
# Abinda muka fahimta game da tsarin lokaci na tarihi daidai ne?

Mun kai ga wannan babbar tambayar. Ta yaya zamu iya tabbatar da ainihin lokacin da abubuwa suka faru? Wannan batu ne mai girma, babu shakka zamu so Allah ya ƙara bamu tabbaci, idan lallai wannan fahimtar abinda zai faru a zamanin ƙarshen daidai ne.

Littafi Mai-Tsarki ya kuma bada rahoton wani abu mai muhimmanci da ya faru da ya shafi shirin Allah na ceto. Watau mutuwa da tashin Ubangijinmu Yesu Almasihu. Idan ba za a bamu cikakken tabbacin cewa Almasihu ya tashi a matsayin shaidar cewa ya biya dukan bashin zunuban zaɓaɓɓun ba, za a barmu da rashin tabbas dangane da dukan shirin Allah na ceto.

Zamu karanta Ayyukan Manzanni 1:1-3 domin tabbatar da wannan.

> **Ya Tiyofalas, tarihin nan na farko wanda na rubuta, ya shafi dukan abubuwan da Yesu ya fara yi, da kuma waɗanda ya fara koyarwa, har ya zuwa ranar da aka ɗauke shi aka kai shi sama, bayan ya yi umarni ta wurin Ruhu Mai-Tsarki ga manzannin da ya zaɓa. Ya bayyana kansa gare su a raye bayan shan wuya tasa, tare da tabbataswa masu yawa, masu ƙarfi kuma yana bayyana gare su a kai a kai har kwana arba'in, yana zancen al'amuran mulkin Allah.**

Allah ya kuma faɗa a cikin 1Korantiyawa15:3-8 cewa:

> **Jawabi mafi muhimmanci da na sanar da ku shine wanda ya karɓo cewa, Almasihu ya mutu domin zunubanmu, kamar yadda litattafai suka faɗa, cewa an binne shi, an tada shi, a rana ta uku, kamar yadda littatafai suka faɗa, ya kuma bayyana ga Kefas, sa'annan ga sha biyun, sa'annan ya bayyana ga yan'uwa fiye da ɗari biyar a lokaci guda, waɗansunsu kuma suna nan har zuwa yanzu amma waɗansu sun yi barci.Sa'annan ya bayyana ga Yakubu sa'annan ga dukan manzanni. Daga ƙarshe ya bayyana gare ni, ni da nake kasasshe, marar cancanta.**

Littafi Mai-Tsarki ya koyar a fili cewa nufin Allah ne cewa a bada tabbacin tashin Almasihu yadda ba za a sami saɓani ba. Dukan wanda ya nace kan musunta wannan gaskiyar yana da hikima ne a ganin idonsa kawai, yana kuma gani kamar ya fi Allah sani.

Abin mamaki shine yayinda Allah ya buɗe idanunmu ga sanin abubuwan da zasu faru na ƙarshe a tarihin duniya, Allah ya kuma bamu shaidu da dama da suka tabbatar mana da cewa mun fahimci lokacin da kuma abubuwan da zasu faru a ƙarshen tarihin duniya.

Kawo yanzu mun tsara lokacin da abubuwan da zasu faru a ƙarshen zamani. Da yake suna da muhimmancin gaske zamu sake bayyana su a takaice. Mun tarar da waɗannan ranaku.

1. Tashin Yesu daga matattau ya faru ne ranar 14 ga wata na farko cikin shekara 33 A.D. Watau Nisan 14, A.D. 33 na kalandar Littafi Mai-Tsarki, wannan kuma shine 1 ga watan Afrilu, A.D. 33, ta kalandar zamaninmu.

2. Zamanin Ikklisiya ya fara ne bayan fentekos, wadda ta faru ranar 22 ga watan Mayu shekara 33 A.D.

3. Zamanin Ikklisiya ya ƙare kana aka fara kwanaki 8,400 na tsanani a jajibirin fentekos cikin shekara ta 1988, watau 21 ga watan Mayu, 1988.

4. Kwanaki 2,300 na farko a lokacin tsanani ya fara ranar 21 ga watan Mayu, 1988, ya kawo ga ƙarshe ranar 7 ga watan Satumba, 1994.

5. Kashi na biyu na zamanin tsanani, wanda ya ƙunshi kwanaki 6,100 (8,400-2,300=6,100), ya fara ranar 7 ga watan Satumba 1994, ya kuma kawo ga ƙarshe ranar 21 ga watan Mayu, 2011.

6. Watanni biyar na ƙarshe a tarihin duniya zasu fara ranar 21 ga watan Mayu 2011 zai kuma kawo ga ƙarshe ranar 21 ga watan Oktoba 2011.

Kawo yanzu muna da jerin lokutan da muhimman abubuwan da zasu kai ga ƙarshen duniya zasu faru. Mun kuma nuna bayanan da muka samu daga cikin Littafi Mai-Tsarki da suka sa muka kai ga yin imani da haka.

Amma yanzu muna so mu yi nazarin ranakun da aka bayyana a waɗannan lokutan bisa ga waɗansu bayanan da Littafi Mai-Tsarki ya bamu. Zamu tarar cewa Allah ya yi mana ƙarin bayani da zamu iya sani, ba tare da wata shakka ba ko kaɗan, cewa wannan tsarin lokacin daidai ne. Yanzu zamu duba daki daki mu nuna yadda waɗannan lokutan suka yi daidai da juna.

Zamu fara da tsawon zamanin Ikklisiya da ya fara ranar 21 ga watan Mayu A.D.33, ya kuma kai ga ƙarshe ranar 21 ga watan Mayu, 1988. Zamanin Ikklisiya ya haɗa da ranar 22 ga watan Mayu ta A.D. 33, da kuma ranar 21 ga watan Mayu, 1988. Wannan yana nufin ya ci gaba na tsawon shekaru 1,955 (1988-33=1.955) zuwa ƙarshe. Kalaman nan "zuwa ƙarshe" sun yi daidai da tsarin lokutan ayyukan da Allah ya yi a baya. Misali, Isra'ila ta shafe shekaru 430 a Masar zuwa ranar ƙarshe (Fitowa 12:40-41). Za a gani bisa ga abinda aka rubuta a cikin Littafi Mai-Tsarki cewa daga ranar da Isra'ila ta bar Masar zuwa ranar da Isra'ila ta isa Tekun Urdun tayi shirin ƙetarewa, kwanaki 40 ne.

Banda haka kuma, sabili da Almasihu ya yi magana cikin karin magana, zamu ga waɗansu kalamai ko lambobi na dabam (waɗanda suma kansu kalmomi ne), da zasu iya kasancewa da ma'ana yadda suke ko kuma wata ma'ana ta ruhaniya. Ta haka sau da dama, lambar nan 3 tana jadada nufin Allah. Wannan zai kasance wurin da za a sake bayyana ma'anar ruhaniya da Allah yake jadadawa ta wajen amfani da lambobi.

2- Waɗanda aka basu umurni su yaɗa Bishara

3- Nufin Allah

4- Nisan lokaci ko abinda Allah yake magana a kai cikin ruhaniya

5- Kafara, wanda yake jadada shari'a da ceto

7- Cikawar nufin Allah

10- Cikar abinda ake magana a kai

11- Zuwan Almasihu na farko shekaru 11,000 bayan halitta

12- Cikar dukan abinda ake magana a kai.

13- Karshen duniya, bayanin abinda ya faru shekaru 13,000 daidai bayan halitta.

17- Samaniya

23-Fushin Allah ko shari'a.

37- Fushin Allah ko shari'a.

40- Gwaji

43-Fushin Allah ko shari'a.

Banda haka kuma mun koya daga Littafi Mai-Tsarki cewa idan za a iya raba lamba babba zuwa ƙananan lambobi wanda kowannensu yake da muhimmanci na ruhaniya, wannan zai taimake mu mu gane ma'anar ruhaniya ta babbar lambar. Zamu iya samun tabbacin cewa lambar tana samar da ma'ana ta ruhaniya da zata taimake mu mu fahimci abinda ake magana a kai a wurin.

An bayyana wannan tsarin dukan tsawon shekaru 1,955 na zamanin Ikklisiya. Za a iya raba lambar zuwa 5 x 17 x 23. Kowanne ɗaya daga cikin

lambobin nan uku kuma yana da ma'anar ruhaniya mai girma da tayi daidai da halin zamanin Ikklisiya. Mun karanta a cikin II Korantiyawa 2:14-16 cewa:

> **Amma godiya ta tabbata ga Allah, shi da kullum yake yi mana jagaba mu ci nasara, albarkacin Almasihu, ta wurinmu kuma yake baza ƙanshin nan, na sanin Almasihu a ko'ina. Don kuwa, a gun Allah mu ne ƙanshin Almasihu a cikin waɗanda ake ceto, da waɗanda suke a hanyar hallaka. Ga na ƙarshe ɗin, ƙanshin nan wurin mutuwa ne, mai kaiwa ga hallaka, ga na farkon kuwa, ƙanshin rai ne mai kaiwa ga rai. To, wa zai iya ɗaukar nauyin waɗannan abubuwa?**

Waɗannan ayoyin suna koya mana cewa Bishara tana kawo mana ceto da kuma mutuwa. Ana danganta ceto da sammaniya (17), Mutuwa kuma da fushin Allah (23). Ka tuna lambar nan 5 cikin ruhaniya tana nuna biyan bashin zunubanmu. Saboda haka shekarun Ikklisiyan na 1,955 lokacin da ya kamata a kai bishara ko'ina a duniya, ya bayyana a fili yadda Bishara ta ke: saboda haka 1,955 ya yi daidai da 5 x 17 x 23. Ta haka shekarun zamanin Ikklisiya suke da tushe a fansa ko kafara (5), abinda ya kawo sammaniya (17), ya kuma kawo fushin Allah (23). Wannan wani abu ne da ya faru haka kawai? Ba haka kawai ya faru ba. Ya yi daidai da tsarin da muka bayyana yanzu.

### Cikar shekaru 13,000 na kafawar Duniya

Ya kamata a faɗi wani abu guda ɗaya dangane da shekara ta 1988. Shekara ta 1988 ta kasance cikar shekaru 13,000 na tarihin duniya haka kawai ne? Mun koya daga cikin Littafi Mai-Tsarki cewa an halicci duniya a cikin shekara ta 11,013 B.C. Idan muka ƙara 11,013 kan 1988 muka ɗebe 1 (domin babu shekara 0 daga kalandar Tsohon Alkawari zuwa kalandar Sabon Alkawari), adadin shine 13,00. Babu shakka ƙarshen zamanin Ikklisiya, wadda tayi daidai da cika shekaru 13,000 na kafawar duniya, ya nuna cewa Allah yana bin wani taƙamammen tsari ne.

Wannan bayanin ya zama da ban sha'awa idan muka gane cewa daga lokacin halitta (11,013 B.C.), zuwa shekarar da aka yi ruwan tsufana (4990 B.C), lokacin da hukumcin Allah ya sauko bisa duniya duka, shekaru 6,00 ne daidai da shekaru 23. Ka tuna lambar nan 23 sau da dama tana nuna fushin Allah. Haka kuma daga shekara 4990 B.C. Har zuwa shekara 33 A.D lokacin da Almasihu ya daure hukumcin Allah, shekaru 5,000 ne da shekaru 23 daidai. Yanzu mun koyi cewa shekara ta 2011 ce zata kasance shekara ta ƙarshe, kuma shekara 11,013 B.C zuwa shekara ta 2011 tana daidai da shekaru 13,000 da 23. Waɗannan duka sun faru ne haka kawai? Ka tuna mun ce ya yiwu shekara ta 2011 ce zata kasance shekara ta ƙarshe domin mun gane cewa ya yiwu lokacin tsananin zai ɗauki kwanaki 8,400 ne watau shekaru 23 cur. Idan kuma aka tara 23 da 1988 za a sami 2011 a matsayin ƙarshen duniya.

Shekaru 23 na ƙarshe da suka fara ranar 21 ga watan Mayu, 1988 zamani ne na tsanani wanda ya kasance farkon shirin shari'a a na ƙarshen zamani a duk faɗin duniya. Yana da muhimmanci cewa 21 ga watan Mayu, 1988, ya ƙarasa da zamanin Ikklisiya, a lokacin da zamanin tsanani ya fara. Bisa ga annabcin Littafi Mai-Tsarki a cikin I Bitrus 4:17, ''Don lokaci ya yi da za a fara shari'a ta kan jama'ar Allah''. Mun koyi cewa shekara ta 1988 da ranar 21 ga watan Mayu, 1988, tayi daidai da tsarin lokaci na tarihi.

Lokaci mai muhimmanci na bayanin abubuwan da suka faru na tarihi shine shekarar 1994. Mun koyi cewa ranar 7 ga watan Satumba 1994 daidai yake da kwana 2,300 bayan 21 ga watan Mayu, 1988. Ka tuna mun bayyana cewa shekara ta 1994 shekara ce ta ranar busa ƙaho. Watau shekara ce da Allah ya ƙayyade domin yaɗa Bishara ga dukan duniya. Yanzu mun koyi cewa ranar 7 ga watan Satumba 1994 ce ranar fari ga watan bakwai (Tishri 1), ta kalandar Littafi Mai-Tsarki.

Tishri 1 ranar bukin idi ce da ake kira ''abin tunawa,...taruwa mai-tsarki''(Levitikus 23:24) da kuma ''ranar busa ƙaho''.(Littafin Lissafi 29:1).[11] Wannan ranar ce aka sanar da shi a matsayin ''Ɗan Rago na Allah wanda ya ɗauki zunuban dukan duniya.'' (Yohanna 1:29), A cikin A.D. 29, bisa ga kalandarmu ta zamani, ranar ita ce 29 ga watan Satumba. Kuma bisa ga kalandar Littafi Mai-Tsarki, wannan ranar ita ce Tishri 1, wadda ta kasance ranar busa ƙaho, kamar yadda ranar 7 ga Satumba 1994 ta kasance ranar busa ƙaho.

Kalmar nan ''Bukin Busa ƙaho'' tana magana a kan bada 'yanci ga duniya (Levitikus 25:10). Dalili ke nan ake fassara ''teuah'' a matsayin ''Ranar busa ƙaho'' dangane da ranar fansa. Almasihu ne tushen fansa, da kuma bukin busa ƙaho. Saboda haka ranar 26 ga watan Satumba A.D. 29 lokacin da Yohanna mai-baftisma ya gabatar da shi kamar yadda muka karanta a cikin Yohanna 1:29 ''Duba ga Ɗan Rago na Allah'' ya kasance wata shaida ta ɗaukaka ga duniya cewa Almasihu ne ''ranar busa ƙaho'' wanda ya zo da Bisharar ceto.

Haka kuma a shekarar bukin busa ƙaho 1994 ranar 7 ga watan Satumba, za a sake yaɗa Bishara ga dukan duniya. Kuma a ranar 26 ga watan Satumba ta A.D. 29 da 7 ga Satumba 1994, ranar bukin ta Littafi Mai-Tsarki ita ce rana ta fari ga watan bakwai. Babu shakka, kamar yadda aka fassara ''teruah'' a matsayin ranar ''bukin busa ƙaho'' a Leviticus 25:9

---

11. A cikin Livitikus 23:24 da kuma Littafin Lissafi 29:1, Allah ya yi Magana a kan bukin rana ta fari ta watan bakwai. A cikin ayoyin biyu, an fassara kalmar Ibraniyanci "teruah" da "busa ƙahonni". An fassara kalmar nan "teruah" a matsayin "ihu" ko kuma "gangami" " ko ƙara" lokuta da dama a cikin Littafi Mai-Tsarki. Amma ba a taɓa fassara ta da "busa ƙaho" ba sai a cikin waɗannan ayoyin biyu kawai. Sai dai a cikin Levitikus 25:9, da ta yi Magana a kan ranar kafara, an fassara ta da "jubili".

dangane da ranar fansa, zamu iya ganin wannan a cikin Leviticus 23:24 da kuma Littafin Lissafi 29:1, dake magana a kan "abin tunawa game da busa ƙahonni" mun fahimci cewa za a iya fassara ta a matsayin "ranar tunawa game da busa ƙahonni" Saboda haka ya kamata a kira wannan bukin da masu ilimin tauhidi ke kira "bukin sarewa." bukin busa ƙaho".

Ka tuna mun koyi cewa ranar 7 ga watan Satumba 1994, ya ƙare ne cikin kwanaki 2,300 na farko na kwanaki 8,400 na ranar tsanani. Ranar 7 ga watan Satumba, 1994. babban taron da ba wanda zai iya ƙirgawa, a duk faɗin duniya, ya fara zuwa cikin mulkin Allah. Ranar ce karo na biyu a tarihin duniya, aka zubo da Ruhu Mai-Tsarki. Da wata rana ce ba ranar 7 ga watan Satumba, 1994 ba, ba za a danganta shi da ranar bukin Tishri 1 ba, da ya kasance "alamar abubuwan dake tafe"(Kolosiyawa 2:16-17). Wannan abin ɗaukakar, bukin ranar 7 ga watan Satumba 1994 (Tishri 1, 1994), shine ya mamaye ya kuma zama farkon kwanakin 6,100 na ƙarshen zamanin ceto.

Amma shekara ta 1994, lokacin da Allah ya fara aiwatar da kwanaki 6,100 na gagarumin shirinsa na ceto a duk faɗin duniya, shekara ce mai ban tsoro ga ikklisiyai a duk faɗin duniya. An zubo da Ruhu Mai-Tsarki yadda waɗanda basu cikin Ikklisiya, waɗanda basu da wata alaƙa da wata ikklisiya a ko'ina cikin duniya, ɗumbin mutane, da babu wanda zai iya ƙirgawa, zasu sami ceto. Haka kuma a cikin, ikklisiyar za a ci gaba da shirin shari'a. Shaiɗan wanda aka kafa a cikin dukan Ikkilisiyai a farkon lokacin tsanani zai ci gaba da mulki, Allah zai ci gaba da aika masu da "wata babbar ɓatar basira don su gaskanta ƙarya" (II Tasalonikawa 2:11). Allah zai ci gaba da shirya waɗanda suke cikin Ikklisiyai domin hukumci.

Wannan wani labari ne mai-ban tsoro ga Ikklisiyai. Su da kansu basu gane da wannan ba. Sun yi imani da cewa suna bautawa Almasihu da aminci. Amma Littafi Mai-Tsarki ya bayyana mana gaskiya. Ba za a sake samun wata damar ceto ƙarƙashin ikon Ikklisiya ba.

Ka tuna, a farkon wannan nazarin, mun bayyana munin wannan matsanancin halin yayinda muke nazarin tsarin abubuwan da zasu faru na tarihi a lokacin tsananin da Littafi Mai-Tsarki ya bayyana. A shekarar 1879 B.C. Yakubu ya fara shan tsanani (Ayyukan Manzanni 7:11) domin matsananciyar yunwa da aka yi fama da ita a ƙasar. Bayan shekaru biyu, cikin shekarar 1877, an umurci Yakubu ya tafi ya zauna a Masar tare da iyalinsa gaba ɗaya. Zasu bar ƙasar alkawari da Allah ya ba kakansu Abraham, shekaru 215 da suka shige. Da yake ƙasar alkawarin tana kwatancin mulkin Allah, kamar an umurce shi ya fita daga mulkin Allah ke nan. Kamar yadda a cikin shekarar A.D. 1988 Allah ya bada Ikklisiya ga mulkin shaiɗan, haka kuma a cikin shekarar 1877 B.C, aka bada ƙasar alkawari, ƙasar Kan'ana ga miyagu su yi mulki a wurin. Wannan babu shakka lokaci ne na ƙunci.

Allah ya danganta wannan tsananin da tsananin da Ikkilisiyai zasu fuskanta, kamar yadda a cikin shekarar 1994, a fili yake cewa Allah ya gama da su, yana shirya su domin shari'a. Idan muka sake duba waɗannan lambobin da suka danganta ƙuncin zamanin Yusufu da na wannan zamanin,

zamu tarar  an jadada batun ruhaniya na waɗannan al'amuran. Idan muka ƙara shekara ta 1877 da 1994 muka ɗebe 1, zamu sami 3,870 a matsayin yawan shekaru tsakanin waɗannan mawuyatan abubuwan da suka faru. Lambar nan 3,870 da aka kasa zuwa 3 x 1,290, ko 10 x 3 x 3 x 43. Lamba 43 tana nuna shari'a, Saboda haka yawan shekarun sun danganta waɗannan abubuwan guda biyu, dake nuna cikar(10) nufin (3 x3) Allah na saukar da hukumci (43). An ruɓa lambar nan uku ba kawai domin nuna muhimmancin nufin Allah ba, amma domin mu cika shi. (Farawa 41:32).

Mun koya a farkon wannan binciken cewa, Allah ya danganta matsanancin lokacin ƙunci da Ikklisiya, inda shaiɗan yake mulki a yau, da irin ƙuncin da Isra'ila ta fuskanta na tsawon shekaru 70. Ya fara da mutuwar sarki Josaya a shekara ta 609 BC, ta kuma ci gaba na tsawon shekaru 70 sai da aka kashe sarkin Babila a shekarar 587 B.C shine abu mai ban tsoro na farko da ya auku. Tuni a cikin shekara ta 609 B.C., lokacin da aka kashe Josaya sarkin Isra'ila na ƙarshe, Isra'ila ta faɗa ƙarƙashin mulkin sarakunan al'ummai waɗanda suke kwatancin mulkin shaiɗan bisa Ikklisiyai. Sai dai, a cikin shekara ta 587 B.C, lokacin da aka lalata Urushalima gaba ɗaya duk da haikali. Sarki Nebukanezar, sarkin Babila, wanda yake a matsayin shaiɗan a cikin Littafi Mai-Tsarki, ya zama mai mulki bisa ƙasar Isra'ila baki ɗaya. Wannan mawuyacin abu ne ainun!

Wannan mawuyacin lamarin marar daɗi kuma wani tsari ne da Allah ya bayar na tsananin da za a fuskanta a zamaninmu. An danganta wannan ma da shekara ta 1994 ta mugun tsananin wannan zamanin da tsawon shekarun dake tsakaninsu. An lalata Urushalima a shekara ta 587 B.C. Idan muka tara 587 da 1994, muka kuma ɗebe 1, zamu sami 2,580, wanda yake 2 x 1,290, ko 10 x 3 x 2 x 43. Da yake ta fuskar ruhaniya lamba 2 tana wakiltar waɗanda suka kawo Bishara, saƙon ruhaniya na waɗannan shekarun 2,580 shine cikar (10) nufin(3)Allah kan Ikklisiyai, da Allah ya umurta su kai Bishara ga duniya (2), cewa za'a hukunta su (43).

Abin sha'awa, kuma mai taimako, shine Allah ya danganta waɗannan tsananin na Yakubu, da Isra'ila da kuma zamaninmu da ayar nan cikin Daniyel 12:11, inda Allah yace:

> **Daga loton da za a kawas da ƙonanniyar hadaya marar-fasawa, an kafa kuma abin ƙyama mai-halataswa, za a yi kwanaki dubu da ɗari biyu da tassa'in.**

Tun wannan lokacin Littafi Mai-Tsarki ya yi amfani da rana ɗaya wajen bayyana shekara (Ezekiyel 4:6), mun sani zamu iya fahimtar wannan a matsayin shekaru 1,290. Tsawon shekaru 1,290 tsakanin ƙuncin da Yakubu ya fuskanta na shekara ta 1877 B.C da na Isra'ila a cikin shekara ta 587 B.C. Banda haka kuma akwai tsawon shekaru 3 x 1,290 tsakanin ƙuncin da Isra'ila ta fuskanta na shekara ta 587 B.C. da tsananin zamaninmu na shekarar 1994.

Idan ka yarda ka kula da yadda waɗannan al'amuran suka shiga daidai da juna, ya nuna cewa, babu shakka fahimtarmu game da lokutan da abubuwa suka faru na tarihi ta ƙara ƙarfafa bisa ga harshen Littafi Mai-Tsarki.

A lokaci na gaba zamu yi nazari a hankali kan ranar 21 ga watan Mayu 2011, wadda ta kasance ranar ta kwanaki 8,400, ko kuma shekaru 23 cikakku na tsanani. Ka tuna mun koyi cewa bayan wannan za a yi kwana 153(watanni 5) da zai kawo ƙarshe ranar 21 ga watan Oktoba 2011. Da yake 12 ga watan Mayu da kuma Oktoba 21 sun faru ne a cikin shekara ta 2011, da muke koyo a shekara ta ƙarshe ta duniya, ya kamata mu yi nazari a kan wannan shekarar a hankali.

**Kwana ɗaya shekaru Dubu Ne.**

Allah ya ja hankalinmu zuwa kan wannan shekarar ta wata hanya mai ƙarfi. A cikin II Bitrus 3:6, Allah ya yi magana game da ruwan tsufanan da ya hallaka duniya baki ɗaya a zamanin Nuhu, muka kuma karanta cewa:

> **Bisa ga wannan fa duniya wanda ta ke a sa'an nan, yayinda ruwa ya sha kanta, ta hallaka.**

Daga nan kuma a aya ta gaba, Allah ya yi magana game da shari'ar da za a yi a ƙarshen duniya. Mun karanta a aya 7 cewa:

> **Amma sammai da suke yanzu, da duniya kuma, bisa ga wannan magana kanta an tanaje su domin wuta, ajiyayyu zuwa ranar shari'a da hallakar mutane masu fajirci.**

Nan da nan kuma bayan waɗannan ayoyin biyu, Allah ya yi wata magana mai-nauyi a II Bitrus 3:8, inda muka karanta cewa:

> **Amma, ƙaunatattu, kada ku manta da wannan abu guda, rana ɗaya a wurin Ubangiji kamar shekara dubu ce, shekara dubu kuma kamar rana ɗaya ne.**

Menene ake magana a kai lokacin da Allah ya ce yana son dukan zaɓaɓɓu, "ƙaunatattu na Allah" da basu san da waɗannan abubuwa ba? Lallai yana da muhimmancin gaske, Allah kuma ya nace cewa suna bukatar sanin wannan. Wannan abin ya shafi lokaci.

Allah ya ce, "rana ɗaya a wurin Ubangiji kamar shekara dubu ce, shekara dubu kuma kamar rana ɗaya ne". Nan da nan mun ga cewa Allah ya yi magana a kan wannan batun sau biyu. Da farko ya ce, "rana ɗaya ...i kamar shekara dubu ce," Daga nan ya maimaita maganar da cewa, "shekara dubu kuma kamar rana ɗaya ne." Wannan ya ƙara jadada muhimmancin

cewa ya kamata dukan masu bi na gaskiya su sani cewa rana ɗaya shekaru dubu ne.

Ka tuna, Fir'auna ya fara yin mafarki a kan shanu bakwai masu ƙiba da suka rame, daga nan ya yi mafarki a kan zangarku bakwai masu kauri suka koma suka zama sirara. Allah ya bada nassi a cikin Littafi Mai-Tsarki game da wannan a cikin Farawa 41:32 inda muka karanta cewa:

> **Maimaitawar mafarkin nan na Fir'auna kuwa, ya nuna cewa Allah zai tabbatar da shi ba da jimawa ba.**

Dokar da Allah ya kafa a wannan ayar ita ce lokacin da Allah ya maimaita magana, yana jadada gaskiyar abinda yake faɗa. An tabbatar da abinda zai faru, kuma zai faru ba da daɗewa ba. Saboda haka ta wajen maimaita magana cewa rana ɗaya kamar shekara dubu ne, Allah yana gaya mana cewa yana da muhimmanci, kuma babu shakka zai faru.

Amma ina dangantakar wannan da II Bitrus 3, wurinda Allah ya yi magana a kan shari'ar duniya baki ɗaya, hukumcin zamanin Nuhu da kuma hukumcin zamaninmu? Idan muka dubi labarin ruwan tsufana baki ɗaya da aka bayar a cikin Farawa 7, zamu sami amsar. Tilas ne mu kula da jirgin, katamfaren jirgin nan da Allah ya umurci Nuhu ya gina. Mun karanta a cikin Farawa 7:1-4 cewa:

> **Sai Ubangiji ya ce wa Nuhu, " Ka shiga jirgin, kai da iyalinka duka, gama na ga a wannan zamani, kai adili ne a gare ni. Daga cikin dabbobi masu tsarki ka ɗauki bakwai bakwai, namiji da mace, marasa tsarki kuwa namiji da mace, da kuma tsuntsayen sararin sama bakwai bakwai, namiji da mace, domin a wanzar da irinsu a duniya duka. Gama da sauran kwana bakwai kana in sa a yi ruwa a duniya yini arba'in da kwana arba'in. Dukan abu mai rai wanda na yi zan shafe shi daga duniya.**

A cikin ruhaniya ruwan tsufanan yana nuna hukumcin Allah a kan masu mugunta na zamanin Nuhu. Jirgin yana misalin kariya daga hukumcin, saboda haka yana wakiltar Mai-Cetonmu, Ubangiji Yesu Almasihu, wanda ya kare mu daga hukumci. Dabbobin suna wakiltar dukan halitta, dake dogara ga Allah domin kuɓuta daga kangin rashin gaskiya (Romawa 8:19-23). Wannan zai faru ne lokacin da Allah ya halicci sabuwar sama da sabuwar duniya.

Saboda haka a cikin Farawa 7, Allah yana cewa 'yan adam duka na duniya suna da kwana bakwai su shiga ƙarƙashin kariyar Almasihu, wanda shi kaɗai zai iya cetonmu daga fushin Allah. Amma saurara. Allah ya nace a cikin II Bitrus 3 cewa tilas ne mu san cewa rana ɗaya kamar shekara dubu ne? Bari mu musanya shekaru 7,000 da kwana bakwai. Saboda haka, Allah yana gayawa Nuhu cewa dukan ɗan Adam dake ko'ina cikin duniya yana da

shekaru 7,000 ya nemi kariya a cikin Kristi, idan suna so su tsira daga fushin Allah.

Wacce shekara ce shekara 7,000 bayan ruwan tsufana na zamanin Nuhu? Zaka gaskanta da shi? Shekaru da dama da suka shige mun koyi cewa an yi ruwan tsufana a shekara ta 4990 B.C, shekaru 7,000 bayan wannan kuma sun kai mu shekara ta 2011. Ka tuna, mun tara shekarun Tsohon Alkawarin muka ɗebe shekara 1, domin babu shekara sifili.

4990 + 2011-1=shekaru 7,000

Saboda haka tilas mu fahimci cewa Allah yana cewa yana bukatar ganin dukan zaɓaɓɓu na Allah zasu sani cewa shekara ta 2011 ita ce zata kasance shekarar da duniya zata shuɗe.

## Watanni Biyar Na Ƙarshe

Sai dai akwai sauran abin faɗa. Tilas ne mu koyi cewa akwai watanni biyar da suka biyo bayan kwanaki 8,400 na zamanin tsanani. Mene ne yake faruwa a wannan lokacin? Waɗannan watannin biyar na ƙarshe da zasu fara ranar 21 ga watan Mayu, 2011, ya shafi shirin Allah na ceto da kuma shirinsa na shari'a. Zamu tarar cewa a rana ta farko ta watanni biyar, da ya kasance rana ta 21 ga watan Mayu, 2011, za a fyauce masu bi na gaskiya su zauna tare da Almasihu har abada. Zamu kuma gane cewa ranar ce za a fara hukumta waɗanda basu da ceto a jahannama.

A cikin Ruya Ta Yohanna 9, Littafi Mai-Tsarki ya yi magana a kan lokacin da jahannama zata fara a duniya. Ya ƙunshi watanni biyar (aya 5 da 10). Surar ta fara da kalmomin nan ''rami marar matuƙa'' (wanda ake dangantawa da jahannama), yana buɗe kuma hayaƙi kamar na kibiritu yana fitowa daga ciki. A wannan lokacin, waɗanda suka yi imani da cewa sun sami ceto domin su malaman Littafi Mai-Tsarki ne, amma basu sami ceto ba, ba a kuma fyauce su ba, suna kan ƙoƙarin koyarwar Littafi Mai-Tsarki irin tasu ta ƙarya. Ana misalta su da fara (aya 11), suna kuma cutar waɗanda suke duniya a lokacin. Sai dai ba zasu taɓa waɗanda suke da hatimin Allah a goshinsu ba.

Maƙasudin jahannama shine domin hallaka ta har abada. Dalili ke nan da ya sa Abaddon da Apollyon suke mulki bisansu (Ruya Ta Yohanna 9:11), sunayen da suke bayyana jahannama. Da yake suna cikin jahannama a waɗannan watannin biyar na shari'ar ƙarshe a duniya, za a hallaka dukan waɗanda basu sami ceto ba har abada. Ba zasu sake rayuwa ba. Za a shafe su da sauran duniya baki ɗaya. Ba zasu iya cutar masu bi na gaskiya waɗanda suke da hatimin Allah a goshinsu ba domin masu bi na gaskiya ba zasu taɓa ɗanɗana jahannama ba. Za a fyauce masu bi na gaskiya (a fyauce su a sama), da zarar an fara watannin nan biyar na ƙarshe.

Mun karanta a cikin Ruya Ta Yohanna 9:4 cewa:

**Aka kuma hana su cutar ciyayin duniya, ko tsiro, ko kowane itace, sai dai mutanen da ba su da hatimin Allah a goshinsu**

A wannan wurin, ciyayin, da tsiron, da itatuwan suna misalin masu bi na gaskiya. A cikin Ruya ta Yohanna 1, Allah ya jadada annoba ta ƙarshe, hukumci na ƙarshe a duniya, a cikin aya ta 1 inda ya ce: ''don su ne iyakacin fushin Allah''

Daga nan kuma aya ta gaba ta tabbatar mana da cewa, dukan masu bi sun tsira a cikin Allah ''kamar bahar na gilas''. Mun karanta a Ruya Ta Yohanna 15:2 cewa:

**Sai na ga wani abu kamar bahar na gilas, gauraye da wuta, na kuma ga waɗanda suka yi nasara da dabbar nan, da sifarta, da kuma lambar sunanta, a tsaitsaye a bakin bahar na gilas, da molayen yabon Allah a hannunsu.**

''Bahar na gilas''ɗin sammaniya ne, kamar yadda aka ambata a cikin Ruya Ta Yohanna 4:2, ...''sai ga wani kursiyi a girke a Sama, da wani a zaune a kai.'' Aya ta shida kuma ta ce, ''A gaban kursiyin kuwa akwai wani abu kamar habar na gilas, garau yake kamar ƙarau.''

Ya yiwu an fyauce masu bi na gaskiya a ranar farko ta watanni biyar na ƙarshe, saboda haka zasu tsira daga mummunan abin da zai faru ga waɗanda ba a fyauce su ba, zai kasance lokacin farincikin gaske da kuma mamaki ga waɗanda aka fyauce.

Wannan lokacin watanni biyar ya ƙunshi kwanaki 153 daidai, daga 21 ga watan Mayu zuwa 21 ga watan Oktoba. Za a iya raba lambar nan 153 ta fannin ruhaniya a matsayin 3 x 3 x 17, kamar yadda aka yi lokacin da muka duba kifaye 153, Saboda haka ta fuskar ruhaniya, tana nuna waɗanda a gare su ya zama nufin Allah (3) ya ɗauke su zuwa sama (17). Lambar nan 3 da aka ruɓata tana nuna cewa babu shakka Allah zai aikata abinda ya faɗa.

## Karin Bayanai Kwarara

Mun tarar da tabbaci mai muhimmanci a kan cewa ranar 21 ga watan Mayu , 2011, ce zata kasance ranar fyaucewa. Bisa ga kalandar Littafi Mai-Tsarki, ranar 21 ga watan Mayu, 2011, ita ce rana ta 17 ga watan biyu. Watau shekaru 7,000 daidai kafin wannan lokacin, ranar 17 ga wata na biyu bisa ga kalandar Nuhu, Allah ya rufe ƙofar jirgin. Mun karanta a cikin Farawa 7:1 da 4 cewa:

**Sai Ubangiji ya ce wa Nuhu, ''ka shiga jirgin, kai da iyalinka duka, gama na ga a wannan zamani, kai adali ne a gare ni... Gama da sauran kwanaki bakwai, kana in sa a yi ruwa a duniya yini arba'in da**

**kwana arba'in da dare arba'in. Dukan abu mai rai da na yi zan shafe shi daga duniya.**

Mun kuma karanta a cikin Farawa 7:10 da 11 cewa:

**Sai bayan kwana bakwai ruwayen suka kwararo bisa duniya. A ranar sha bakwai ga watan na biyu, na shekara ta ɗari shida na rayuwar Nuhu, a ran nan sai dukan maɓuɓɓugai na manyan zurfafa suka fashe, tagogin sammai suka buɗe.**

Muka kuma karanta a aya 13 da 16 cewa:

**A wannan rana Nuhu da 'ya'yansa. Shem, Ham da yafet, da matar Nuhu da matan 'ya'yansa tare suka shiga jirgin... Su waɗanda suka shiga, namiji ne da mace na kowane taliki, suka shiga jirgin kamar yadda Allah ya umarce shi. Sai UBANGIJI ya kulle jirgin daga baya.**

Kalandar zamanin Nuhu ta ɗan banbanta da kalandar Littafi Mai-Tsarki da aka samar daga baya, kasancewa tana da kwana 30 a wata, yayinda kalandar Littafi Mai-Tsarki take da kwanaki 29 da 1/2 a wata, da yake tana tafiya ne da tsayawar wata, Sai dai Allah a cikin Allantakarsa ya danganta lokacin rufe ƙofar jirgin ranar 17 ga wata na biyu, da rufe ƙofa ranar 21 ga watan Mayu, 2011, wadda bisa ga kalandar Littafi Mai-Tsarki ta kasance ranar 17 ga wata na biyu. Wannan ya raba har abada, masu bi na gaskiya a cikin jirgin da dukan waɗanda basu sami ceto ba waɗanda suka hallaka a wajen jirgin. Wannan ya jadada cewa a wannan ranar da za a fyauce masu bi na gaskiya, babu wata damar samun ceto ga waɗanda aka bari a baya. Saboda haka zamu gani kamar akwai shekaru 7,000 daidai daga lokacin da aka rufe ƙofar wata damar samun ceto, a lokacin hallaka duniya na zamanin Nuhu da kuma hallaka duniya baki ɗaya a zamaninmu. Wannan ya faru ne haka kawai?

**Daga Ranar Fansa Zuwa Fyaucewa kwanaki 722,500**

Allah ya sake bamu wani muhimmin bayani kan lokaci da ya ƙara tabbatar da cewa za a yi fyaucewa ranar 21 ga watan Mayu, shekara 2011. Ranar 1 ga watan Afrilu 1, ga A.D,33, aka giciye Ubangiji Yesu domin zunubanmu da zunuban dukan waɗanda ya zo domin ya ceta. Bayan shekaru 722,500 kuma za a yi fyaucewa (21 ga watan Mayu, 2011). Ana iya raba waɗannan lambobin zuwa lambobi masu muhimmanci:

$$(5 \times 10 \times 17) \times (5 \times 10 \times 17) = 722,500$$

Mun koyi ma'anar waɗannan lambobi na ruhaniya. Aikin ceto (5) ya cika (10) lokacin da dukan zaɓaɓɓu suka shiga sama (17). An ruɓa wannan gaskiyar ta wajen maimaita lambobin nan har sau uku, 10 x 5 x 17. An

jaddada wannan ne bisa ga abinda aka faɗa a Farawa 41:31, "...Allah ya riga ya ƙaddara al'amarin, hakika kuwa Allah zai tabbatar da shi ba da jimawa ba."

Mun ga yadda Allah ya danganta lokacin fyaucewa ranar 21 ga watan Mayu, 2011, da lokacin da aka iya shiga sama (fansa), domin lokacin da aka giciye Yesu, ya biya cikakken bashin zunuban waɗanda za a fyauce zuwa sama su zauna tare da Yesu?

A wannan lokacin a nazarinmu, bari mu ɗan dakata mu duba abinda muka koya a sakin layi na baya.

Muna da tabbacin cewa an giciye Almasihu ranar bukin idin ƙetarewa, wanda ya kasance ranar Jumm'a A.D. 33, wadda ta kasance rana ta 14 ga watan farko na kalandar Littafi Mai-Tsarki. Mun kuma hakikanta cewa wannan ranar ce aka hukumta Almasihu domin zunuban dukan waɗanda ya zo domin ya ceta. Domin ya biya zunubansu, an basu tabbacin zuwa sama su yi mulki tare da shi har abada abadin.

Bisa ga bayanan da muke da su a cikin Littafi Mai-Tsarki, mun fahimci cewa, ranar 21 ga watan Mayu, 2011, dukan waɗanda suka sami ceto sakamakon biyan bashin zunubansu da Almasihu ya yi a lokacin da aka giciye shi, zasu sami cikar cetonsu yayinda aka fyauce su zuwa sama. Saboda haka, tabbatacce ne cewa kwanakin watan nan 1 ga watan Afrilu, A.D. 33, da Mayu 21, 2011 suna da alaƙa da juna ta ruhaniya.

Amma kuma mun gane cewa waɗannan kwanakin watan guda biyu, waɗanda suke kimanin shekaru 2,000 tsakani, suna da dangantaka da juna ta yawan kwanakin da ke tsakaninsu da kuma muhimmancin ruhaniya na tsawon waɗannan kwanakin.

Ka sake duba yawan shekarun 722,500. Ba abin mamaki ba ne cewa sun rabu kashi biyu daidai dake da ma'anar gaske ta ruhaniya, 10,5,17? Allah ne kaɗai wanda ya halicci wannan duniyar da dukan tsarinta, zai iya tsara lokacin tarihi ta wannan hanyar mai ban al'ajibi. Tsaya! Ko yana yiwuwa dangantakar waɗannan lokutan biyu ya faru ne haka kawai? Amsar ita ce ba haka kawai wannan ya faru ba.

### Karin Tabbaci

Muna ci gaba da samun waɗansu tabbacin da suka nuna cewa mun kai ga sanin wani lokacin ƙarshe. Kamar yadda muka faɗa, Allah ya ƙara jadada ko tabbatar da wannan ranar 21 ga watan Mayu, 2011, ta wajen sa ranar da aka rufe ƙofa, da ranar da za a yi fyaucewa ta zama rana ta 17 ga wata na biyu na kalandar Littafi Mai-Tsarki. Lambar nan 17 tana da alaƙa da ranar fyaucewa domin cikin ruhaniya, lambar nan 17 tana misalin samaniya. Banda haka kuma lamba 2 (wata na biyu) cikin ruhaniya yana misalin waɗanda aka basu hakin kai Bishara. Ba abin mamaki ba ne cewa za a fyauce su ranar 17 ga wata na biyu? Wannan ya faru ne ba gaira ba dalili?

Mun kuma koyi cewa ranar ƙarshe ta duniya ita ce 21 ga watan Oktoba, 2011 rana ta 23 ga wata na bakwai ta kalandar Littafi Mai-Tsarki.

Lambar nan 23 tana misalin fushin Allah da aka zubo. Lamba 7 (watanni bakwai) yana nuna cikar nufin Allah. Wannan ma ya faru ne ba gaira ba dalili, da cikar hukumcin Allah kan waɗanda basu da ceto ya faru a cikin watan bakwai a ranar da aka ambaci lambar nan 23, wadda ta kasance lambar da ta nuna fushin Allah, ta haka ta nuna muhimmancin cikar fushin Allah bisa marasa ceto?

An jaddada sahihancin wannan lokacin ƙarshen duniyar yayinda muka yi nazarin wannan watan na ƙarshe bisa ga fushin Allah. Lokacin da Allah ya hukumta Yesu, sa'anda yake biyan bashin zunuban zaɓaɓɓu, ya jawo hankalin mu ga sanin cewa, tilas ne a hukumta waɗanda ba zaɓaɓɓu ba. An danganta waɗannan hukumcin biyu da shekaru 1,978 lokacin da aka giciye Yesu (A.D. 33) daga zamani na ƙarshe (A.D. 2011).

2011 – 33 = 1,978

1978 = 2 x 23 x 43

Lamba 2 tana misalin waɗanda suke kawo Bishara.

Lamba 23 tana misalin fushin Allah

Lamba 43 tana misalin hukumci

Saboda haka ta wajen amfani da lamba 1.978, Allah yana jaddada cewa za a hukumta waɗanda aka ba aikin kai Bishara (2) waɗanda har yanzu suke ƙarƙashin fushin Allah (23 da 43).

### Allah ya ci gaba da ɗaukar Matakan Hukumci Yayinda ake Ci Gaba da Ceton Ɗumbin Mutane

Yayinda muke yin nazarin kwanakin watan nan na tsanani, da fyaucewa, da kuma kwanaki na ƙarshe na duniya, mun sake gano wata gaskiya. Mun koyi cewa a cikin kwanaki 6,100 na ƙarshe na kwanaki 8,4000 na tsanani, Allah yana amfani da masu bi na gaskiya waɗanda basu cikin Ikklisiya, domin kawo mutane masu ɗumbin yawa da babu mai iya ƙirgawa zuwa cikin mulkin Allah, tare da dukan waɗanda aka ceta a dukan wannan lokacin. Banda wannan kuma, ana shirya dukan membobin Ikklisiyar nan domin watanni biyar na ƙarshe lokacin da hukumcin Allah na ƙarshe zai afko masu. Amma kuma har wa yau a cikin kwanakin nan 153 na ƙarshe, dukan waɗanda suka sami ceto a cikin kwanakin nan 6,100, idan aka tara da kwanaki 153, yana daidai da kwanaki 6,253. An raba lambar nan 6,253 zuwa muhimman lambobi 13 x 13 x 37.

Lamba 13 ita ce ƙarshen duniya

Lamba 37 ita ce hukumcin Allah na ƙarshe

Ka tuna, Nuhu ya yi kwana 370 a cikin jirgi. Ka tuna kuma Allah ya hallaka sojojin Asiriya 185,000 ƙarƙashin Sennacherib a cikin dare ɗaya (II Sarakuna 19:35), da kuma 185,000 = 1,000 x 5 x 37. Saboda haka mun ga lambar nan 37 tana misalin hallaka da zata faru sabili da hukumcin Allah.

Da lambar nan 6,253 Allah yana tabbatar mana da cewa yayinda akwai ɗumbin mutanen da zasu sami ceto a wannan lokacin, tsarin hukumcin Allah (37) zai cika a ƙarshen duniya (13), Idan ka yarda ka sake duba yadda aka ruɓa lambar nan 13.

A farkon wannan nazarin, mun tarar cewa bisa ga bayanan Littafi Mai-Tsarki, babu tabbas game da lokacin da duniya zata ƙare. Amma, ta wurin amfani da bayanan Littafi Mai-Tsarki a hankali, mun tarar cewa lokacin daidai ne. An jadada shaida a kan shaida. Idan lokacin da aka ƙayyade ba daidai ba ne a ɗaya daga cikin watannin nan, da dama daga cikin shaidun ba zasu zama karɓaɓɓu ba. Babu shakka idan abinda muka koya daga Littafi Mai-Tsarki ba daidai ba ne, ba za a san da dama daga cikin shaidun ba. Zamu iya hakikanta cewa za a yi fyaucewa ranar 21 ga watan Mayu 2011, kuma ranar ƙarshe ta tarihin duniya zata kasance ranar 21 ga watan Oktoba, 2011.

Sai dai waɗannan ba bayanan masu hikima ko kuma masu ilimi bane. Wannan gaskiya ce da ta shafi rayuwar kowanne ɗan adam ( kusan mutane miliyan bakwai) da suke duniya yanzu. Yana iya yiwuwa a kaucewa wannan ranar hukumcin?

# Sura ta Shida.
# Akwai Bege Domina?

Littafi Mai-Tsarki ya bayyana cewa Ubangiji Yesu Almasihu zai zo kamar ɓarawo da dare (II Bitrus 3:10), I Thassalonikawa 5:2). Mun koyi cewa abinda zai faru ke nan dukan zamanin Ikklisiya. Saboda haka bai kamata ɗaliban Littafi Mai-Tsarki da kuma masu ilimin tauhidi su damu kansu da lokacin dawowar Almasihu ba. Zasu maida hankali a kan aikin shailar Bishara ga dukan duniya (Ayyukan Manzanni 1:6-8).

Sai dai, mun koyi wannan kusan ƙarshen duniya, masu bi na gaskiya zasu samu ƙarin haske a kan lokacin da wannan zai faru a tarihi (Kubawar Shari'a 8:5-6; I Tasalonikawa 5:3-5; Ruya ta Yohanna 3:3).

Muna wannan lokacin na tarihi, saboda haka, mun iya sanin ainihin ranar, da watan da shekarar da duniya zata ƙare.

Da yake lokacin ƙarshe ya yi kusa, ya kamata mu damu KO ZAN IYA SA RAI ? Babu shakka akwai bege ga dukan mai rai a yau. Haka ya yiwu ne domin Allah ya tabbatar mana da cewa, a wannan lokacin na tarihi, ɗumbin mutane, da babu wanda zai iya ƙirgawa, suna samun ceto (Ruya ta Yohanna 7:9-14). Saboda haka, ya kamata mu ɗan yi magana a kan shirin ceto na Allah.[12]

A cikin Markus 1:14b-15, Yesu ya bayyana umurnin Allah ga 'yan adam:

> **...Sai Yesu ya shigo ƙasar Galili, yana yin bisharar Allah, yana cewa, "Lokaci ya yi, mulkin Allah ya kusato, Ku tuba, ku gaskanta da bishara."**

Gaskantawa da Bishara kamar yadda wannan ayar ta umarta yana nufin yarda da cewa Bishara ta fito ne daga bakin Allah. Saboda haka, gaskiya ne, mai muhimmancin gaske, da kuma ikon gaske. Dokar Allah ce, Littafi Mai-Tsarki, da ya zama tilas kowa ya yi biyayya da ita, Saboda haka ya kamata wanda ya gaskanta da Bishara ya yi ƙoƙarin yin biyayya da ita iyakar iyawa, muddin ya iya fahimtar Littafi Mai-Tsarki.

Kowanne mutum bisa ga halitta yana iya aikata waɗansu ayyuka na ruhaniya, da ya haɗa da gaskantawa da kuma biyayya ga Littafi Mai-Tsarki. Haka tana yiwuwa ne domin an rubuta dokar Allah a zuciyarmu. (Romawa 2: 14-15), Allah ya kuma bashi lamiri domin ya tantance abinda ke daidai. Ko da ya ke ya mutu a cikin ruhaniya, da jiki da kuma ruhu, yadda bashi da

12. Domin yin bincike mai zurfi a kan shirin Allah na Ceto, ana gayyatar ka, ka kira Family Radio ko kuma ka rubuto, a aika maka kyautar littafin nan *Ina Fata Allah Zai Cece Ni.* Adireshin shine: Family Radio, Oakland, CA 94621, ko kuma ka kira 1-800-543-1495. Ko ka aiko e-mail. Adireshin e-mail ɗinmu shine: familyradio@familyradio.org

hanyar samun rai na har abada, duk da haka tilas ya iya yin biyayya da dokokin Allah. Kowanne mutum, a wani mataki, yana tuba ko kuma ya juya ga barin zunubansa. Saboda haka ya iya yin rayuwar da ta dace. Bisa ga halitta, ya mutu cikin ruhu domin shi zuriyar Adamu ne, iyayenmu na farko. Lokacin da Adamu ya yi zunubi a gonar Addini, ya zama ke nan yan adam baki ɗaya sun yi zunubi domin dukan mu mun fito ne daga jikin Adamu. (I Korantiyawa 15: 22).

Sai dai, ba shi da ikon samun ceto, watau ya sami rai na har abada a cikin jiki da kuma ruhunsa. Haka ta faru ne domin Bishara tana nuna cewa dokar Allah ta bukaci a hukumta mai-zunubi ta wajen mutuwa mai-kunyatarwa. Saboda haka, duk wanda aka yankewa hukumcin irin wannan mutuwar ba zai sake rayuwa ba, ya kuma rasa rai na har abada. Dalili ke nan da ya sa tilas kowanne daga cikinmu ya nemi wanda zai ɗauki gurbinsa ya ɗauki hukumcin a madadinsa.

An bada wannan dokar ta Markus 1;15, ta gaskantawa da Bishara da tuba (a daina aikata zunubi a yi biyayya da Littafi Mai-Tsarki), kimanin shekaru 2,000 da suka shige. Tana cewa, ''Lokaci ya cika.'' A wannan lokacin ne Yesu Mai-Ceto ya zo domin ya biya bashin da dokar Allah ta ƙayyade a madadin waɗanda ya zo domin ya ceta.

Yau, maganar nan cewa, ''lokaci ya cika'' ya yi daidai da shirin Allah na ceto. Yayin da muka yi nazarin gagarumin shirinsa na ceto ga duniya, mun sani cewa akwai mutane iri uku a duniya. Sune:

1. Waɗanda basu taɓa jin maganar Littafi Mai-Tsarki ba a rayuwarsu.

2. Waɗanda suka ji koyarwar Littafi Mai-Tsarki, amma suka yi wa Littafi Mai-Tsarki ba'a, ko kuwa sun zo wurin Littafi Mai-Tsarki da wani ra'ayi nasu.

3. Waɗanda suka gaskanta da Littafi Mai-Tsarki suna kuma marmarin samun ceto, gaba ɗaya bisa ga gaskiyar koyarwar Littafi Mai-Tsarki.

## Waɗanda Basu Taɓa Ji Ba

Dukan tarihin duniya, akwai waɗanda suka yi rayuwa har suka mutu basu taɓa ji ko karanta maganar Littafi Mai-Tsarki ba. Kuma da yake ''bangaskiya ta wurin jawabin da aka ji take samuwa, jawabin da ake ji kuma ta maganar Almasihu take'' (Romawa 10;17), tilas ne mu gaskanta cewa babu wani daga cikin mutanen nan da ya sami ceto. Saboda haka, bai zama tilas Allah ya sa su ji Maganar Allah a wani lokaci a rayuwarsu ba.

## Waɗanda Suka Ji Maganar Allah Amma suka yi Ba'a.

Tun lokacin da Allah ya bada umurni a tuba a bada gaskiya (Markus 1:15), nufin Allah ne cewa a cikin duniya, mutane da yawa zasu ji Bishara.

Dalili ke nan, misalin shekaru 2,000 da suka shige, Yesu ya umarta cewa dukan masu bi na gaskiya su kai Bishara ga dukan duniya (Matta 28:19-20).

Abin baƙin ciki shine halin da mutane da dama da suka ji Bishara suka nuna shine ko dai su yi wa Littafi Mai-Tsarki ba'a, ko kuma su bi dokokinsu a maimakon dokokin Littafi Mai-Tsarki, yayinda suke ƙoƙarin fahimtar gaskiyar Littafi Mai-Tsarki, Waɗanda suke yi wa Littafi Mai-Tsarki ba'a sun hakikanta cewa akwai kuskure a cikin Littafi Mai-Tsarki, saboda haka basu da sha'awa ko niyar yin biyayya da shi. Waɗanda suka zo wurin Littafi Mai-Tsarki da irin fassararsu, ko waɗanda suka ɗora dogararsu ga Ikklisiyarsu ko ɗarikarsu a matsayin mai iko duka, a maimakon dogara ga Littafi Mai-Tsarki, suna kuma yin biyayya da koyarwar da basu yi daidai da ta Littafi Mai-Tsarki ba.

Littafi Mai-Tsarki ya koyar da cewa, waɗanda basu sami ceto ba zasu iya yin ɗan biyayya da dokokin Allah. Wannan gaskiyar ta bayyana begen mutane da dama. Misali, wannan gaskiya ne ga waɗanda suke membobin ikklisiyai dake koya matakan bangaskiya biyar da aka samu daga koyarwar littatafan Dort na tarihi.[13] Abu na farko shine muna bukatar mu gaskanta da cewa kafin mu sami ceto, bamu da wani sukuni. Da yake membobin Ikklisiya sun sani cewa suna rayuwar da ta cancanta, suna yin biyayya da dokokin majami'unsu, sun sani ba za a yi watsi da su gaba ɗaya ba. An koya masu bisa ga shaidar bakinsu cewa hallaka ta har abada zata faru ne kawai ga waɗanda basu da ceto. Saboda haka irin yadda suke rayuwa da kuma aminci ga ikklisiyarsu, da kuma kasancewa an yi masu baftisma a cikin ruwa su kuma membobin ikklisiyarsu ne masu aminci, babu shakka wannan ya tabbatar masu da cewa sun sami ceto. Sun kasa gane cewa alamar ceto ita ce marmarin yin biyayya ga Littafi Mai-Tsarki gaba ɗaya. Saboda haka suna cikin wani hali na rashin ceto domin sun gaskanta da wata koyarwa da bata Littafi Mai-Tsarki ba.

Za a kuma iya ambaton wani misali. A Ikklisiyai da dama, abu mafi muhimmanci game da ceto da ake koyarwa shine karɓar Yesu a matsayin Mai-Ceto da kuma yin baftisma ta ruwa. A cikin waɗannan majami'un, waɗannan ayyukan da kuma yin aminci wajen kiyaye dokokin ikklisiya da rayuwar da ta dace, yana basu tabbacin ceto. Sai dai shirin ceto ne da Littafi Mai-Tsarki ya bayar, inda shaidar ceto shine marmarin yin aminci da dukan abinda ke cikin Littafi Mai-Tsarki.

Saboda haka, Ikkilisiyan zamaninmu da suke cewa suna bin dukan koyarwar Maganar Allah wadda bata da kuskure, Littafi Mai-Tsarki, suna cike

13. Littatafan Dort na tarihi ko kuma koyarwar matakan bangaskiya na tarihi. Matsayar koyarwar addini ce da mabiya ɗarikar Presbiteriyan masu ra'ayin 'yan mazan jiya da kuma Ikkilisiyar Reformed da ke bin koyarwar tauhidi ta John Calvin, wani fitaccen mai ilimin tauhidi da ya yi zamani kimanin shekaru 400 da suka shige.

da irin waɗannan mutanen dake rayuwar da ta dace waɗanda suke cikakken zumunci a Ikklisiya. Waɗannan ƙaunatattun mutanen ba su san cewa har yanzu suna ƙarƙashin fushin Allah ba, balle kuma su ga wani dalilin binciken koyarwar ikklisiyarsu domin sanin cewa ko Ikklisiyarsu tana bin koyarwar Littafin Mai-Tsarki da aminci.

Ya kamata gargaɗin da aka yi a cikin I Thasalonikawa 5:2-4 ya basu tsoro. Haka ta faru ne domin kusan dukan waɗanda suke cikin Ikklisiyai sun gaskanta cewa sun tsira a cikin Almasihu, saboda haka, sun gamsu da gaskanta cewa zai zo kamar ɓarwo da dare. I Thassalonikawa 5:2-4 tana cewa:

> **Domin ku da kanku ku sani sarai, ranar Ubangiji za ta zo ne kamar ɓarawo da dare. Lokacin da mutane suke cewa, "Muna zaman salama da zaman lafiya," wuf, sai halaka ta auko musu, kamar yadda naƙuda take kama mace mai ciki, ba kuwa hanyar tsira. Amma, ai, ba a cikin duhu kuke ba, 'yan'uwa, har da ranar nan za ta mamaye ku kamar ɓarawo.**

Wannan halakar da zata faru farat ɗaya zata kasance tana magana da ranar hukumcin da ta kusa ne kawai. Abin baƙin ciki ne cewa waɗannan ƙaunatattun mutanen har yanzu suna ƙarƙashin cikakken fushin Allah da tilas zai sauko bisan dukan wanda bai riga ya sami ceto ba tukuna.

Sau da dama, waɗannan mutanen masu mutumci ne, waɗanda suke aikata abinda ya kamata kuma membobin Ikklisiya ne masu aminci. Sai dai, ta wajen zuwa wurin Allah da ra'ayinsu da karkatattar koyarwar da Ikkilisiyarsu ke koyarwa, karkatacciyar koyarwar Ikklisiyarsu, a maimakon koyar da Littafi Mai-Tsarki baki ɗaya. Ba tare da gane haka ba, suna karanta Littafi Mai-Tsarki sau da dama, daga nan a cikin zuciyarsu su murɗa gaskiyar Littafi Mai-Tsarki su maishe ta daidai da abinda suke tunani. Ta haka basu sauraron Littafi Mai-Tsarki da marmarin yin biyayya da shi.

Littafi Mai-Tsarki ya ambaci irin wannan halin sau da dama. Ya yi ta gargaɗi cewa wannan halin zai iya janyo cikakken fushin Allah kan waɗanda suka yi watsi da Maganarsa ta wannan hanyar. Ba ya ba irin waɗannan mutanen ƙarfin hali ko begen cewa ya yiwu Allah ya cece su. A gaskiya ma, su da kansu basu ganin bukatar irin wannan begen. Sun hakikanta cewa sun riga sun sami ceto, ko kuma bisa ga tsarin cetonsu na yi-da-kanka, sun hakikanta cewa zasu iya samun ceto duk lokacin da suka ga dama.

Gaskiyar ita ce Allah yana sane da irin wannan tawayen na ruhaniya yakan kuma ƙyale irin waɗannan mutanen a cikin tawayensu. Misali mun karanta cewa, Yesu ya zo Urushalima domin ya yi wa'azi, Littafi Mai-Tsarki kuma a cikin Markus 6:5-6 yace:

> **Bai ko iya yin wata mu'ujiza a can ba, sai dai ya ɗora wa marasa lafiya kaɗan hannu ya warkar da su. Ya yi mamakin rashin bangaskiyarsu. Sai ya zazzaga ƙauyuka yana koyarwa.**

Yayinda Allah yake da ikon sa mutanen Nazarat gaskantawa da shi, babu shakka yana jaddada cewa mutanen da basu da sha'awar yin biyayya ga dukan Maganar Allah suna cikin hatsarin gaske na ruhaniya. An bayyana abinda Allah yake cewa irin waɗannan mutanen, misali a cikin Irimiya 26:4-6, inda muka karanta cewa:
Ubangiji ya faɗa wa Irmiya ya ce wa jama'a ''haka Ubangiji yace, idan ba za ku kasa kunne gare ni ba, ku yi tafiya a dokata wadda na sa a gabanku ba, ku kuma kula zantuttukan bayina, annabawa, waɗanda na yi ta aiko muku, to, amma ba ku kula ba. Saboda haka zan mai da wannan haikali kamar Shilo, in mai da wannan birni ya zama abin la'ana ga dukan al'umman duniya.

## Waɗanda a cikin tawali'u suka amince da cewa suna bukatar yin biyayya da Littafi Mai-Tsarki

Littafi Mai-Tsarki ya yi magana akan mutane iri uku, sune waɗanda suka saurari Littafi Mai-Tsarki suka kuma yi marmarin biyayya da shi. Sun hakikanta cewa Littafi Mai-Tsarki wanda shine Bishara, dokar Allah ce da ke magana da su. Sun fahimci cewa su masu zunubi ne da suka kumyata sun kuma shiga uku da Allah. Sun gane cewa kowacce kalma da ta fito daga Littafi Mai-Tsarki daga bakin Allah take, saboda haka tilas a saurare ta. Sun gane cewa Allah ne kaɗai zai cece su, kuma ko da yake ya kamata a hukumta su da mutuwa ta har abada sabili da zunubansu, suna begen cewa, ya yiwu Allah zai yi masu jinƙai (Luka 18: 13). Suna ƙoƙarin yin biyayya da dukan abinda suka gaskanta daga cikin Littafi Mai-Tsarki da yake sun sani cewa biyayyarsu bata taimaka ba ta kowacce hanya ga ceto ko kuma tabbatar da cewa Allah zai cece su. Ya yiwu su koyi cewa Allah yana ceton ɗumbin mutane a wannan lokacin, da yake shi mai-jinƙai ne ya yiwu suma zasu sami ceto.

Saboda haka suna roƙon Allah domin jinƙansa, tare da sanin cewa jinƙan Allah ne kawai wanda basu cancanci samu ba idan suka sami ceto. A halin da ake ciki kuma, yayinda suke haƙurin sauraron Allah (Makoki 3:26), su kan yi koƙarin koyon iyakar abinda suka iya daga Littafi Mai-Tsarki, domin su iya yin biyayya da dokar Allah iyaka iyawa.

Bamu san abinda ya sa halin wannan ruƙunin mutanen na uku ya banbanta da na ruƙuni na biyu ba. Ya yiwu Allah yana jawo su domin ya cece su. Ya yiwu kuma haka tana faruwa ne domin an rubuta dokokin Allah a cikin zukatansu, kuma lamirinsu yana yi masu gargaɗi game da illar zunubi. Gaskiyar dake da muhimmanci ba cewa mene ne ya sa suke da sha'awar yin biyayya da Littafi Mai-Tsarki a zukatansu ba. Gaskiyar da ke da muhimmanci ita ce suna da wannan halin yin biyayya da Littafi Mai-Tsarki.

Tilas ne mu tuna cewa kowa, a kowanne lokaci, wanda ya yi biyayya da waɗansu dokokin Allah yana ayyukan ruhaniya ne. Sai dai wannan aikin ba zai taimaka ga samun ceton mutum ba (Afisawa 2:8-9). Zaɓaɓɓu ne kaɗai zasu sami ceto, kuma aikin ceto, aikin Allah ne ɗungurumgum. Dalili

ke nan da ya sa Allah zai iya ceton jariri ko mutum da bashi da cikakke hankali wanda yake ƙarƙashin sauraron Littafi Mai-Tsarki.

A cikin shirin Allah mai-ban al'ajibi, Ya ba zaɓaɓɓu kunne na ruhaniya, waɗanda suke cikin masu rai da ke sauraron Maganar Allah. Mun karanta a cikin Matta 11:15:

**Waɗanda suke da kunne bari su ji.**

Saboda haka mun sani Cewa, Allah, a cikin aikinsa mai ban al'ajibi na ceto, yana magana a kan mutane daga fannoni daban daban guda biyu. A ɓangare guda, ya yi magana a kan waɗanda suke ƙarƙashin sauraron Bishara, waɗanda idan suna iya fahimtar Maganar Allah ko kaɗan, zasu yi ƙoƙarin biyayya da Littafi Mai-Tsarki. A cikin biyayyarsu, suna addu'a domin jinƙan Allah, suna haƙurin sauraron Allah, suna begen cewa suma zasu sami ceto. A cikin burinsu na yin biyayya, suna cikin wani wuri (Littafi Mai-Tsarki) inda Allah zai cece su idan suna sha'awa.

A wani ɓangaren kuma, Allah yana bada manyan lambobin gargaɗi ga waɗanda suke ƙarƙashin sauraron Maganar Allah, amma waɗanda ba zasu saurara cikin ƙanƙancin zuciya, da sha'awar yin biyayya da Maganar Allah ba. Ta wurin ayyukansu, suna nuna cewa sun raina Maganar Allah. Yana gargaɗin cewa waɗannan ayyuka, idan suka ci gaba, zasu ƙarasa da hukumcin cikakkar kumya, la'ana, asarar gado, mutuwa, waɗanda duka suke cikin fushin Allah a kan zunubi.

Wannan ba lokacin girman kai ba ne, da nuna isa, ko muƙami, ko neman girma. Ba lokaci ne na nuna fifiko a ruhaniya ko kuma rashin kumya cikin ruhaniya ba. Lokaci ne da ya kamata mu gane da cikakken ikon Littafi Mai-Tsarki a bisa rayuwarmu, saboda haka mu saurari abinda Allah yake faɗa mana yau a hankali.

Lokaci ya yi da kowanne zai gane abin kumyar zunubansa, da kuma tabbacin cewa, ya cancanci fuskantar cikakken fushin Allah, sabili da zunubansa. Lokaci ya yi da zai yi addu'a ga Allah domin neman jinƙansa. Jinƙansa marar iyaka yafi gaban abinda wani daga cikinmu ya cancanci samu ko kuma tunani.

A yau, a cikin jinƙansa mai-ban al'ajibi, Allah yana ceton mutane masu ɗumbin yawa. Saboda haka yana yiwuwa, cewa yayinda wani daga cikinmu ya nemi jinƙai, idan bamu riga mun sami ceto ba, ya yiwu muna ɗaya daga cikin waɗannan mutane masu ɗumbin yawa, da babu mai iya ƙirgawa.

**BABBAR TAMBAYAR ITA CE**: Kana roƙon Allah domin ceto cikin tawali'u, da cikakken sanin cewa, ba ka cancanci samun ceto ba ko kaɗan, yayinda ka dubi irin rashin biyayya da tawaye da ka yi wa dokar Allah? Ka kuma tuna da mutanen Ninivah. (Yunana 3:6-10).

## BARI ALLAH YA YI WA KOWANNE ƊAYAN MU JINKAI!